**COURSE GUIDE**

# HAU 217
# INTRODUCTION TO HAUSA POPULAR MUSIC (SHARHI KAN MAKAƊA DA MAWAƘAN HAUSA)

**Course Team** Dr. Aliyah Adamu Ahmad (Course Writer) - SSU
Professor Ibrahim Malumfashi (Course Editor) - KASU

NOUN

**NATIONAL OPEN UNIVERSITY OF NIGERIA**

© 2023 by NOUN Press
National Open University of Nigeria
Headquarters
University Village
Plot 91, Cadastral Zone
Nnamdi Azikiwe Expressway
Jabi, Abuja

Lagos Office
14/16 Ahmadu Bello Way
Victoria Island, Lagos

e-mail: centralinfo@nou.edu.ng
URL: www.nou.edu.ng

All rights reserved. No part of this book may be reproduced, in any form or by any means, without permission in writing from the publisher.

Printed 2023

**ISBN: 978-978-058-821-2**

**CONTENTS** **PAGE**

Gabatarwa (Introduction)…………………………….............. iv
Manufar Kwas (Course Aim)………………………………… iv
Yadda Za A Nazarci Kwas (Working Through the Course)…. v
Kashe-kashen Kwas (Study Units)…………………………… v
Auna Fahimta (Assignment).………………………………… v
Jinga (Tutor Marked Assignment)……………………................ vi
Jarrabawar Ƙarshen Darasi…………………………………... vi
(Final Examination and Grading)……………………………. vi

## GABATARWA (INTRODUCTION)

Wannan darasi na HAU 217, yana da muhimmanci wajen koyon darashin Hausa, musamman abin da ya shafi nazarin adabi, adabin ma kuma ɓangaren da ake wa laƙabi da Waƙa ta baka da rubutacciya.
Darasin ya kasu zuwa rukunai da kashe-kashe da suka faro daga sanin mene ne waƙa da kuma ire-iren waƙa da raba-rabenta. Haka kuma yaƘunshi tarihin samuwar waƙa ta gargajiya da rabe-rabenta da yadda ta wanzu a zamanin zaman gargajiyar Hausawa zuwa zamanin zuwan Musulunci da zuwan Turawa.

Daga can kuma an kawo sharhikan yadda yanayin waƙoɗin gargajiya suka samu sauyi ta fuskar jigo da manufa da salailai saboda samun baƙin al'adu na Larabawa da Turawan Ingilishi da suka gauraya da na Hausawa saboda cuɗanyar da takasance a tsakani.
A cikin darasin an zo da cikakken bayani kan dukkan zubi da tsarin kwasɗin ta yaddaɗalibai za su naƙalce shi ba da wahala ba. AƘarshen kowane kashi an zo da tambayoyin auna fahimta da kuma yanayin gane ko darasin ya zauna sosai da gindinsa.

DagaƘarshe kuma an zo da fasalin tambayoyi daɗalibai za su gani domin nazari kafin zuwan jarabawa aƘarshen karatu. An kuma zuba waɗansu ayyukan nazari da mai karatu zai iya amfani da su dominƘarin nazari da tushi a gida. Haka kuma an samar da dama daɗalibai za su iya tuntuɓar malami dominƘarin haske a duk lokacin da wani abu ya shige duhu.

## MANUFAR KWAS (COURSE AIM)

Domin kyautata karatu da koyarwa kowane kashi na da tasa manufa bayan babbar manufar kwasɗin ta bakiɗaya da aka zo da ita a farkon darasi. Ke nan abin daɗalibai za su yi domin sauƙaƙa wa karatun nasu shi ne su karanci kowace manufa da ke liƙe da kowane kashi na darasi domin gane ciki da wajen darashin, ba tare da an samu matsala ba.
Idan an kula da kyau, manyan darussan da ke tattare da kwasɗin suna da dama, sai dai za a iya taƙaita su zuwa kamar haka:

- Ma'anar Kiɗa da Kashe-kashensa
- Ma'anar Waƙa da kashe-kashenta
- Asali da samuwar waƙar Hausa ta gargajiya da ta zamani.
- Danganta tsakanin waƙoƙin baka da rubutattu na zamani
- Yadda ake nazarin waƙar Hausa
- Ratayen wasu daga cikin waƙoƙi, tsofaffi da sababbi waɗanda aka yi nazari a cikinsu

## YADDA ZA A NAZARCI KWAS (WORKING THROUGH THE COURSE)

Domin ganin an samu shawo kan wannan darasi an tsara darasin ta yaddaɗalibai za su iya jan ragamar karatun ba tare da tutsu mai yawa ba. An dai rarraba kwasaɗin zuwa rukuni-rukuni da yakeƘunshe da kashe-kashe masu biye da juna, kuma kowane kashi an rarraba shi yaddaɗalibi zai ga dangantakarsa daɗan uwansa da ke biye. Saboda haka fahimtar darasin zai biyo karatun ta-natsu daɗalibai za su yi wa darasin, su kuma auna fahimtarsu ta amfani da tambayoyin da aka zo da su aƘarshenn darasin. Da yake kuma akwai aikin jinga da malami zai dinga bayarwa bayan kowane kashi na kwas, ɗalibi zai samu damar ganin fasalin yadda jarabawa za ta kasance in an gama darasin bakiɗaya ba tare da ya dogara da malami ba a wannan lokaci. Ana fatar a kammala kwasɗin cikin mako ????, wato kowane kashi a cikin mako guda.

DagaƘarsheɗalibai su sani cewa idan suna nazarin kwasɗin, malaman da za su dinga tuntuɓa ba koyaushe za su kasance tare ba, saboda haka sai su yi jadawalin karatunsu ya dace da kowane kashi na karatu, su kuma dinga ziyara da leƙa abubuwan da malami ya tanada dominƘarin nazari domin faɗaɗa sani daƘarin haske.

Me ya kamataɗalibai su mayar da hankali kai a lokacin gabatar da wannan darasi? Su tabbata sun fahimci abubuwa da keƘasa:

1. Kowane darasi ko kwas yana da rukuni ko 3 ko 4.
2. Kowane rukuni yana da kashi 3 ko 4 ko 5 ko 6
3. Kowane kashi yana da yankin auna fahimta.
4. Kowane darasi na da jingar da za a yi a gida.
5. Kowane darasi ko kwas na tafe da manazarta da wasu ayyukanƘara nazari.

## KASHE-KASHEN KWAS (STUDY UNITS)

A cikin wannan kwas akwai rukuni 3 da kuma kasha-kashe 4,5zuwa 6, kowane kashi yana a matsayin mako guda ne na darasi, ke nan za a kammala shi cikin mako 17. Ana kuma fatar a amsa tambayoyi auna fahimta aƘarshen kowane kashi, dagaƘarshe kuma a amsa tambayoyi na jinga don ganin ko darasin ya zaunu da kyau.

Domin kyautata karatun kwasɗin an ratayo manazarta da wasu ayyukan da za a iya cewa suna da muhimmanci ga wannan kwasaɗin, za suƘara haske fiye daƘma, musamman ma dai tsofaffin waƙoƙin Makaɗan Hausa, da kumawaƙoƙin zamanimusamman waɗanda ke tashe a wannanƘarni na 21. Samun waɗannan tare da kwasɗin zai inganta

nazari da karatu sosai. Ke nan a shiga gonarɗakin karatu a gida ko inda ake ajiye littattafai a kusa ko nesa zai inganta nazarin wannan kwas.
A kula da liƙau da ake sa wa a cikin kowane kashin darasi, za su taimaka wajenƘara haske na nazarin kwasɗin bakiɗaya, sai dai a tabbata liƙauɗin suna aiki yadda ya kamata, kada a bari sai lokacin da ake buƙatar su, a laluba a ga ba su aiki, wato dai a gwada komi kafinƘarshen kwasɗin.

**AUNA FAHIMTA (ASSIGNMENT)**

Shi wannan kwas na tsarin da ba ruwanka da malaminka ne, ko na tafi-da-gidanka, shi ya sa ake jaraba fahimtar karatu ta hanyoyi UKU, hanya ta farko ita ce ta auna fahimta aƘarshen kowane kashin darasi, sa'annan kuma a zo da jinga da za a baɗalibiƘarshen kowane kashi, shi ma, sai dagaƘarshe a yi jarabawarƘarshen zangon karatu, wanda zai nuna an zoƘarshen darasin.

Auna fahimtar da ake yi aƘarshen kowane kashi za ta kasanceƘaramar jarabawa ce, za ta zo da maki 30 daga cikin 100. Ke nan, ana buƙatarɗalibi ya amsa tambayoyi uku inda za a zaɓi 2 su kasance su keɗauke da maki 30, maki 15 kowace tambaya. Sauran maki 70 za su zo ne a jarabawarƘarshen kwas.
Jarabawa dai kamar kullum za a gabatar da ita ce daga gida, ita ma ba a cikin cikin aji ba, kuma za ta kasance ta Intanet ne, ke nan sanin na'ura maiƘwaƙwalwa abbu ne mai muhimmanci gaɗalibi.

**JINGA (TUTOR MARKED ASSIGNMENT)**

Jingar aji tamkar gwajin jarabawa ce gaɗalibai, saboda haka amsa jingar da keƘarshen kowane kashin darasi zai baɗalibi damar fahimtar yadda jarabawarƘarshe za ta kasance ne. Yana da kyauɗalibai su mayar da hankali domin amsa irin waɗannan samfur na tambayoyi, domin za su sauƙaƙa amsa tambayoyin jarabawa aƘarshen darasin bakiɗaya.

**JARRABAWAR ƘARSHEN DARASI (FINAL EXAMINATION AND GRADING)**

Ita dai jarabawa ita ce hanyar da ake gane koɗalibi ya gane darasi ko kuma ya samu naƙasu a wani ɓangare, saboda haka tanaɗauke da kaso ma fi tsoka na 70 cikin 100. Ba wani dabo a cikin wannan fasali domin anaɗauko samfurin jarabawar ne daga tambayoyin da aka dinga turawa na auna fahimta da kuma jinga. Ke nan mayar da hankali wajen amsa waɗanan tamayoyi a lokacin darasi zai rage zafin tambayoyinƘarshen darasi.

**MAIN COURSE**

**CONTENT** **PAGE**


| | | |
|---|---|---|
| **Rukuni Na Daya** | **Samuwar Waƙa Da Ma’anarta……………………** | **1** |
| Kashi na 1 | Kiɗa ……………………………………….. | 1 |
| Kashi na 2 | Waƙa……………………………………….. | 9 |
| Kashi na 3 | Rerawa……………………………………... | 14 |
| Kashi na 4 | Dangantakar Kiɗa da Waƙa………………... | 18 |
| **Rukuni Na Biyu…………………………………………** | | **24** |
| Kashi na 1 | Makaɗa da Mawaƙan Hausa………………. | 24 |
| Kashi na 2 | Kashe-kashen Waƙoƙin Baka……………… | 28 |
| Kashe na 3 | Kashe- kashen Waƙoƙin Baka I…………… | 37 |
| Kashe na 4 | Kashe- kashen Waƙoƙin Baka II………….. | 41 |
| Kashi na 5 | Waƙoƙin Wasu Halittu Da Yanayi Waɗanda Ba Mutane Ba………………….. | 47 |
| .. | | |
| Kashi na 6 | Kashe-kashen Waƙoƙin Baka Dangane da Jigoginsu…………………………………… | 53 |
| **Rukuni Na Uku…………………………………………** | | **60** |
| Kashi Na 1 | Kayan Kiɗan Hausawa…………………….. | 60 |
| Kashi Na 2 | Kayan Kiɗan Hausawa I…………………… | 68 |
| Kashi Na 3 | Nazarin Jigogin Waƙoƙin Ƙarni Na Ashirin Da Ɗaya…………………………... | 73 |
| Kashi Na 4 | Zubinwaƙoƙin Hausa A Ƙarni Na 21…….. | 78 |
| Kashi Na 5 | Zubin Waƙoƙin Hausa A Ƙarni Na 21…..... | 83 |
| Kashi Na 6 | Feɗe Waƙar Jarumar Mata Ta Makaɗi Hamisu Yusuf Sa’id (Breaker) Bisa Gadon Nazarin Waƙar Baka Bahaushiya… | 96 |

# RUKUNI NA 1 SAMUWAR WAƘA DA MA'ANARTA

Kashi na 1 Kiɗa
Kashi na 2 Waƙa
Kashi na 3 Rerawa
Kashi na 4 Dangantakar Kiɗa da Waƙa

## KASHI NA 1 KIƊA

**Abubuwan da Suke Ciki**

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufar Darasi
1.3 ƙunshiyar Darasi
    1.3.1 Ma'anar Kiɗa
        1.3.1.1 Ma'anar Kiɗa a Zahirance
        1.3.1.2 Ma'anar Kiɗa a Luggance
        1.3.1.3 Ma'anar Kiɗa Daga Bakin Masana
1.4 Kammalawa
1.5 Taƙaitawa
1.6 Jingar Aiki
1.7 Manazarta da Wasu Ayyukan Nazari



### 1.1 Gabatarwa

Kalmar kiɗa da waƙa ba su buƙatar gabatarwa a cikin al'ummar Hausawa, saboda irin sanayyar da suke da ita dangane da kalmomin, da kuma tasirin kiɗan da waƙar a wajensu. Ta fuskar magana da aiki, waƙa tana a matsayinta, ba ta sauyawa. A kodayaushe aka yi maganar waƙa, ana nuni ga wani aiki da ake aiwatarwa ta fatar baki, ta amfani da zaɓaɓɓun kalmommin harshe domin shiryata a cikinƘwaƙwalwa ta la'akari da jigo da salo da yanayin masu saurare domin isar da sako. Ko da kuwa wannan saƙon na saka nishaɗi ne da raha a cikin al'umma. Shi kuma kiɗa yana yi wa waƙa rakiya ne don tafiyar da ita, ta yi armashi.Wannan ya sanya koƘaramin yaro aka yi wa maganar waƙa, zai karya murya da nufin rerota, domin kasancewar tsarinta na daban, sa'annan zai iyaƘarawa da yin rawa domin ita ce abokiyar tafiyar waƙa, domin kuwa ya buɗe ido, ya tarar ana aiwatar da ita, kuma ya fahimci abin da take nufi a aikace. Idan kuwa mun fahimci abin da ake nufi da kiɗa da waƙa domin mun wayesu, mun taso cikinsu, kalmomin ba baƙi ba ne a wurinmu, abin da ya rage, shi ne mu bi wannan darasi a hankali domin fahimtar ma'anar kiɗa da waƙa a ilmance.

## 1.2 Manufa

Kowane lamari ba a yin shi sai da manufa. Manufar wannan darasi kamar yadda taken ya nuna magana ke za a zurfafa kan kiɗa da waƙa a fage na ilimin matakin karatu na jami'a. sai dai daga cikin muhimman manufofin wannan darasi akwai:

- Gabatar da kiɗa da waƙa gaɗalibai, domin su san alƙiblar darasin
- Bayyana tarihin waƙar a cikin al'umma a taƙaice
- Bayar da ma'anoni na waƙa daban-daban da aka ciranto daga bakunan masana da manazarta harshen Hausa.
- Sai kuma gabatar da ma'ana kiɗa da waƙa a lokaciɗaya da sauransu

## 1.3 ƙunshiyar Darasi

AƘarƙashinƘunshiyar wannan darasi za a fara da gabatar da tarihin waƙa a taƙaice, wanda shi ne kan gaba. Sanin tarihin zai bayar da haske da gabatar da abin da aka yi guzurin gabatarwa a cikin darasin. Sa'annan sanin ma'anar waƙa da kiɗa zai biyo ba. AƘarƙashin ma'anar waƙa akwai kashe-kashe da za su biyo baya, don sauƙaƙa fahimtar darasin.

### 1.3.1 Mene ne Kiɗa?

Daga jin kalmar kiɗa abinda zaiɗarsu a zuciyar mutum shi ne, amo na sauti da ake samarwa ta amfani da kayan kiɗa. Ma'anar kiɗa ta zahiri da ta lugga da kuma yadda aka nazarceta a rayuwa ta yauda kulum shi za a gani a cikin wannan tattaunawar da ke biye. Sanin ma'anar kiɗa zai zamatamkar shimfiɗa ga dukkanin abinda za a faɗi a cikin wannan kwas.

#### 1.3.1.1 Ma'anar Kiɗa ta Zahiri

Kiɗa kamar yadda bayani ya gabata, wani amo ne na sauti. Kiɗa a rayuwa ta zahiri bai tsaya ga rayuwar nishaɗi kaɗai ba, yana iyaɗaukar ma'anoni da dama a muhallai daban-daban. Idan sarki zai yi wata sanarwa ga jama'arsa ko mutanen garinsa, an ana kaɗa kuge (waniƘarfe mai amo) domin jama'a su taru kofar mai gari ko shugabansu domin a yi musu wata sanarwa. A nan an yi amfani da kiɗa a kan Kuge, domin sanarwa. Idan jama'ar da suka tafi yawan fatauci suka yada zango

domin su huta. Idan suka tashi za suɗora da tafiya, sai ka ga an buga waniƘarfe domin duk inda mutum yake ya hanzarta dawowa cikin jama'a kar a tafi ba da shi ba. Idan aka zuyo a zamanin da aka kafa makarantun boko aƘasar Hausa, akowace makaranta akwai waniƘarfe da ake kira Gwarje, wanda ake bugawa domin a sanar daɗalibai da malamai cewa lokacin cin abinci da lokacin canjin aji da lokacin tashi daga karatu ya cika. Wannan fa na nuna ana kaɗa wani abu domin sanarwa ba domin kiɗa na nishaɗi ba. Idan aka samu nasara a wurin yaƙi, ana yin kiɗa idan masu yaƙi sun dawo gidajensu domin shaida wa jama'ar gari cewa an samu nasara. Daga wannan za a ga cewa a zahiri sauti ne koɗaukar wani abu a buga shi kan wani abu, shi ake nufi da kiɗa.

### 1.3.1.2 Ma'anar Kiɗa a Luggance

Ma fi yawa waƙar baka, musamman wacce muka tashi muka ga ana aiwatarwa a cikin al'umma tana tafiya tare da kiɗa. wannan kiɗa shi ne abokin tafiyarta, domin yanaƘara mata armashi da sanya nishaɗi daƘara riƙe mai sauraronta na tsawon lokaci ba tare day a gaji ba. Da za a cire kiɗan da ke tattare da waƙoƙinmu, ba shakka waƙoƙin za su zama lami, su yi saurin gundurarwa a rage saurarensu. To idan haka ne ko kiɗa yana da muhimmanci ga waƙoƙin baka da ya kamata a waiwayi shi a cikin wannan darasi don bayaninsu ya tafi tare.

A cikin ƙamusun Hausa (CNHN, 2006:243) [1]an bayyana cewa:

"Kiɗa na nufin kiɗa a wannan muhalli. Bugun ganga ko kalangu, koƘwarya, ko goge, ko garaya, (ko taushi ko kotso) da hannu ko da makaɗi ko da wata ko da wani abu,"

### 1.3.1.3 Ma'anar Kiɗa Bisa Fahimtar Shaihunan Malaman Hausa

Kiɗa wani amo ne da ake samarwa ta hanyar amfani da abin bugu ko sarrafawa don tafiyar da waƙa. Kiɗa mafi yawa an fi yin sa da waƙa, amma akwai lokuttan da ake yinsa zallarsa a matsayin alama ta wani keɓantaccen al'amari ko take na abu. Akwai kaɗe-kaɗe da ke alamtar da wani tarihi ko wani abu da ake wanzarwa waɗanda keƘunshe da bayanai ko kuma ana fassara su da wata ma'ana tun asali a cikin al'ummar Hausawa, kamar kaɗa tamburra a lokuttan yaƙi da sanarwa da sauransu. Bayan samun ci gaba na zamani, aka samu kiɗi na garuruwa (misali kiɗan Sakkwato) da na gidajen rediyo irin na buɗewa da rufewa misali (kiɗan gidan rediyo na BBC) da kiɗan takenƘasa (National anthem) da sauransu da dama.

[1]Sa'id, B (ed). (2006) {amusun Hausa. Wallafar Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya. Jami'ar Bayero Kano. Ahmadu Bello Uni~ersity Zaria. Shafi na 243.

Kiɗa a duniyarmu ta yau musamman a wasu al’ummomi da suka ci gaba a rayuwa, yana zuwa shi kaɗai a matsayin alamar nuna wani al’amari keɓantacce. Kaɗe-kaɗen sun shafi ɓangarori da yawa na rayuwa kamar na tarihi da farin ciki da soyayya da baƙin ciki da sauran ɓangarori na rayuwa. Ga yadda yadda masana suka bayyana kiɗa da:

A cewar Gusau (2008:54)[2]
“Kiɗa wani amo ne (sauti) da ake samarwa ta amfani da kayan kiɗa, a samar da sauti wanda kan ratsa jikin mai saurare, ya saka masa karsashi har ya dinga rausayawa yana tattakawa ko jujjuyawa.”

### 1.3.1.4 Ma’anar Kiɗa Bisa Ra’ayoyin Masana

Tarihin kiɗa da waƙa yana komawa ga tarihin zaman al'ummar Hausawa na farko. Ana fara kowane al'amari da dalili, kan haka ne aka kintaci kiɗa da waƙa ya samu ne lokacin da mutum yake gabatar da wani aiki mai wahala ko mai sauƙi, sai ya riƙa rera waƙoƙi domin samun sauƙin tafiyar da wannan aiki cikin sauƙi. Wanda ya ke zaune yana huce gajiya, kan rera waƙa domin ya nishaɗantar da rayuwarsa. Haka zalika wanda yake zaman kaɗaici kan rera waƙa don ya cirewa kansa kaɗaici da rage dogon zango na tsawon lokaci. Wannan waƙar tana fara zuwa ma mutum ta fuskar guna-guni, daga baya ne waɗansu kalmomi gajeru ke biyowa baya. Wasu lokuta waɗannan kalmomi suna zama a matsayin yabo da kirari ko gwarzantawa, a yayin da mutum ya yi wani abin azo-a-gani ko ya burge kansa. Zai yi kirari don nuna bajinta da gwaninta tare da gwarzanta kan shi.

Daga haka waƙa ta zama al'adar Bahaushe. Al'adar al'umma kuma ita ce hanyar da suke tafiyar da rayuwarsu a kai. Kamar yadda masana suka bayyana irin su Bunza (2006:ii)[3] da ya ce ‘Al’ada na nufin dukkanin rayuwar ɗan adam na abin da ke wakana ga rayuwar tun daga haihuwa har zuwa kabari. Al’adar mazauna wuri ko yanki tana tasiri ga rayuwar mutum domin nan ya tashi, ya tar da ana aiwatar da ita, ya rayu da ita, kuma a kanta za a yi masa hukunci’. Kenan idan muka yi la’akari da bayanin da ya gabata dangane al’ada, za mu fahimci cewa kowace al’umma tana da keɓantacciyar al’adar da ta ginu a kanta, wadda al’ummar ke rayuwa bisa wannan tafarki. Wannan tsarin rayuwa shi ake kira tsari na gargajiya. Ita kuwa gargajiya tana tafiya ne bisa abin da rayuwarɗan adam ke so, da wanda ya dace da shi, don rayuwar ta yi daɗin gudanarwa.

[2]Gusau, S. M (2008) Wa}o}in Baka a {asar Hausa: Yanaye-yanayensu da Sigoginsu. Benchmark Publishers Limited, Kano. Shafi na 54
[3]Bunza, A. M (2006) Gadon fe]e Al’ada. Tiwal Nigeria Limited, Lagos. Shafi na ii.

Waƙa na daga cikin abubuwan da rayuwa ke so da sha’awa, tare da gasnin tasirinta ga tafiyar da zuciya da saurin isar da saƙo ga masu saurarenta. Wannan ya sanya ta samu karɓuwa a cikin al’ummar Hausawa, kuma suka taso da ita a cikin jini. Wanda har ma ba a iya cewa ga lokacin da suka fara yinta sai dai a yi hasashe ko kuma a iya rarrabe waƙa da sashe na al’adun Hausawa. Wannan ya ba waƙa damar ratsa al’adu daban-daban na rayuwar al’ummar Hausawa cikinƘanƙanen lokaci.

Sannu a hankali har duk wani al'amari in za a gudanar da shi, sai an nemo mawaƙi domin ya waƙe wannan al'amarin. Tarihi ya nuna ko mutuwa ta faru, in za a kai mutum makwancinsa, sai an raka shi da kiɗa da waƙa. Sarkin sudan (2008:335)[4] ya bayyana cewa, wannan kiɗan da waƙa ma fi yawa jikoki suka fi yin shi ga mamacin domin su samu damar cashewa da yi masa shaƙiyanci. Sa’annan wata dama ce na haɗuwar ‘yan uwa na kusa da nesa, waɗanda aka daɗe ba a haɗu da su ba, domin sada zumunci. Jikokin nan ba lallai sai waɗanda mamacin ya haifa kai tsaye ba, har da jikokin ‘yayyensa daƘannensa da ‘yan uwa da abokan arziki, tare da abokansu.

Kiɗa da waƙa wani babban al'amari ne ga Bahaushe domin daga lokacin da aka haifi jinjiri ake fara waƙe zuwansa, har renonsa ta hanyar tawai, har ya fara yin waƙoƙi da kansa a dandali. Idan ya zama ango nan ma sai an waƙe shi, kuma idan ya zama attajiri ko basarake ko sarkin noman garinsu, zai samu mawaƙan da za su waƙe shi. Kenan waƙa kamar yadda Gusau, (2013)[5] ya bayyana, waƙa tana wakana daga haihuwa daƘuruciya da balaga da manyanci da tsufantaka da mutuwa har zuwa rayuwa ta bayan mutuwa.

Ibrahim (1974: ɓii-ɓiii)[6] ya bayyana ra’ayoyin ra’ayoyi uku na samuwar waƙa aƘasar Hausa da ya haɗa da danganta waƙar da Sasana da ake yi[7] na suna da dangantaka das hi. Sai ra’ayin waƙa ta samu daga wajen tsofaffin daulolin Afirka na Mali da Shonghai, waɗanda dauloli ne da suka yi tashe aƘarnukan da suka gabata. Ra’ayi na uku kuwa shi ne na

---

[4]Sarkin Sudan, I. A (2008) Jiya Ba Yau Ba: Waiwayen Rayuwar Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa. Kundin Digiri na Uku, Jami’ar Usmanu [anfodiyo, Sakkwato. Shafi na 335.

[5]. Gusau, S. (2013) Dangantakar Wa}o}in Baka da Al’adun Hausawa,in E[cerpts of International Seminar on ***Deterioration of Hausa Culture***, Organize by Katsina State History and Culture Bureau in Collaboration with Ummaru Musa ‘Yar’aduwa Uni~ersity, Katsina ,Pages 743-58, ISBN-125-633-8

[6]Ibrahim, M.S (1974) *Kowa Ya Sha Ki]a* . Roukhba Publishers, Kano. Shafi na ~ii-~iii.

[7]Mawa}i zamanin Manzon Allah. Ya yi wa}a a zamanin Jahiliyya, daga baya ya musulunta ya ci gaba da kare Manzon Allah a duk lokacin da ake jefe shi ta hanyar wa}a, sai ya mayar da raddi. Sunansa na asali Hassanu Ibn Thabit, saboda bakin Hausawa da yawan fa]a yau da gobe, sai sunan ya koma Sasana.

sun sami waƙa daga kiɗan farauta, sai kuma na yaƙe-yaƙe na tsakaninsu daƘabilun da ke kewaye da su.

Har wayau a wata faɗa ta Gusau (2014:3)[8] inda yake bayanin faruwar waƙa, ya jaddada cewa, al'adu na Hausawa su ne ke yin jagorancin wajen gina waƙoƙin baka na gargajiya, ta yadda masu gina waƙoƙin suke amfani da tunaninsu wajen shirya waƙoƙin ta la'akari da abubuwan ke zagaye da su da yanayin zamantakewar rayuwarsu. Haka zalika ya tabbatar da cewa waƙoƙin baka sun faro ne aƘasar Hausa a lokacin da Bahaushe ya fara kafa iyali, musamman lokacin da suka fara wayewa da farauta ta tudu da ta ruwa har zuwa lokacin da suka fahimci dabarar noma da sauran sana'o'i na tattalin arziki.

Kasancewar waƙa tana da daɗaɗɗen tarihi a cikin al'ummar Hausawa na tsawon zamani da ba a iya iyakancewa ba, wannan ya sa ta samu zama a matsayin babban rukuni daga cikin rukunnan al'adun Hausawa, wadda Hausawa suka gina ta hanyar amfani da tunaninsu da imaninsu da zamantakewarsu da tsarin rayuwarsu da amfani da kayan amfaninsu da la'akari da yanayinƘasarsu da halittun da ke rayuwa a cikin muhallinsu. A taƙaice dai waƙa na dunƙule da rayuwar Bahaushe ciki da bai, daɗaɗɗiya wacce lokacinta ya shuɗe, tarihinta ya ɓace, waƙa ta adana cikin hikima da azanci.

**Auna Fahimta**

| | |
|---|---|
| 1. | Me ka/kika fahimta dangane ga ma'anar kixi ko kixa? |
| 2. | Ma'anar kiɗa ta zahiri ba ta tsaya ga nishaɗantarwa kawai ba, za a yarda da akwai<br>wasu sautuka da suka zama……. |

**Kammalawa**

A wannan darasi an kawo bayani game da ma'anar kiɗa a Hausa dangane da ma'anarsa ta zahiri da ta lugga da kuma ta bakin masana Adabin Hausa. An yi haka ne domin ɗalibai su fahimci gundarin abinda zai ja ragamar tunanin masana game da matsayin kiɗa a cikin al'ummar Hausawa.

[8]Gusau, S. M (2014) Wa}ar Baka Bahaushiya (The Hausa Oral Song). Bayero Uni~ersity Kano, Inaugural Lecture Series no.14.

## 1.4 Taƙaitawa

- A wannan darasin an fahimci ma’anar kiɗa? Haka nan an gano yadda kiɗa yake da matsayi ga al’ummar Hausawa
- Awannan darasi anfahimci ma’anar kiɗa a luggance, da kuma a zhirance, sa’annan an ga ma’anar kiɗa bisa fahimtar masu ilmi kan waƙa

## 1.5 Manazarta

Bunza, A. M (2006) *Gadon Feɗe Al’ada*. Tiwal Nigeria Limited, Lagos. Shafi naii.

Gusau, S. M (2008) Waƙoƙin Baka a ƙasar Hausa: Yanaye-yanayensu da Sigoginsu. Benchmark Publishers Limited, Kano. Shafi na 54

Gusau, S. M (2013) Dangantakar Waƙoƙin Baka da Al’adun Hausawa, in Excerpts of International Seminar on ***Deterioration of Hausa Culture***, Organize by Katsina State History and Culture Bureau in Collaboration with Ummaru Musa ‘Yar’aduwa Uniɓersity, Katsina, Pages 743-58, ISBN-125-633-8

Gusau, S. M (2003) *Jagoran Nazarin Waƙar Baka*, Bench Mark Publishers,Kano

Gusau, S. M (2014) *Waƙar Baka Bahaushiya (The Hausa Oral Song)*. Bayero Uniɓersity Kano, Inaugural Lecture Series no.14.

Ibrahim, M.S (1974) Kowa Ya Sha Kiɗa . Roukhba Publishers, Kano. Shafi na ɓii-ɓiii.

Sa’id, B (ed). (2006) *ƙamusun Hausa*. Wallafar Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya. Jami’ar Bayero Kano. Ahmadu Bello Uniɓersity Zaria. Shafi na 243.

Sarkin Sudan, I. A (2008) Jiya Ba Yau Ba: Waiwayen Rayuwar Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa. Kundin Digiri na Uku, Jami’ar Usmanu ɗanfodiyo, Sakkwato. Shafi na 335.

Yahya, A. B (1997) *Jigon Nazarin Waƙa*. Fisbas Media Serɓice, Kaduna. Shafi na 4.

## 1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1 Kiɗì ko Kiɗa wani sauti ne da ake samarwa ta amfani da kayan kiɗa, ko wani abu wanda za a haɗa shi daɗan'uwansa don ya bayar da wani amo na sauti. Ana amfani da ganga da makaxi don a samar kixa, haka kuma ana amfani da tafin hanuwa biyu ko ƙwarya da hannu ko ƙwarya da makaxi ko dutse da dutse ko sakaina da sakaina da sauransu duka don a samar da sautin kixa.

2 na sanarwa da ilmantarwa da kuma faɗakarwa.

# KASHI NA BIYU WAƘA

## Abubuwan da Suke Ciki

2.1 Gabatrwa
2.2 Manufar Darasi
2.3 ƙumshiyar Darasi
  2.3.1 Ma’anar Waƙa
    2.3.1.1Ma’anar Waƙa a Zahirance
    2.3.1.2Ma’anar Waƙa a Luggance
    2.3.1.3Ma’anar Kiɗa da Waƙa Daga Bakin Masana
  2.3.2 Dangantakar Kiɗa da Waƙa
2.4 Taƙaitawa
2.5 Jingar Aiki
2.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Nazari
2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

## 2.1 Gabatarwa

An ga ma’anar kiɗa a kashin da ya gabata. A nan kuma za a ga ma’anar waƙa. Wasu mutane ba su bambancewa tsakanin kiɗa da waƙa, ko tsakanin makaɗi da mawaƙi. A irin wannan bincike naƘwaƙwaf, ake tantance ma’anar kowane daga cikinsu ta kowace fuska. Bayanan da za a gani nan gaba kaɗan sun haɗa da ma’anar waƙa ta fuskoki daban-daban kamar yadda aka gani ga kiɗa.

## 2.2 Manufar wannan darasi

Manufar wannan darasi shi neɗalibai su iya tantance ma’anar waƙa, tare da sanin cewa waƙa wani abu ce muhimmi a rayuwar Hausawa ta kowace fuska.

## 2.3 Ƙumshiyar Darasi

A wannan darasi za a ga ma’anoni da manufofin waƙa. Akwai tambayoyin auna fahinta, bayan an taƙaita darasin za aɗauki aikin jinga, sa’annan a ga jerin manazarta waɗanda litattafai ne da maƙalu da makamantansu daɗalibi zai nemiƘarin bayani a cikinsu.

### 2.3.1 Ma’anar Waƙa

Wanda duk ya ji kalmar waƙa, sai ya fara tunanin kalmomi kamar su rerewa, ko wasu kalamai masu zuwa tare da kiɗa domin nishaɗantarwa. A rayuwa ta zahiri da fahimtar malamai za a nazarta kan waƙa. Sauran bayanai sun haɗa har da duba ma’anar waƙa a cikinƘamusoshi kafin a karanta tambayoyin auna fahimta.

#### 2.3.1.1 Ma'anar Waƙa a Zahirance

Waƙa fitacciyar kalma ce da ta shahara tsakanin al’umma na kowane yanki, haka ma a bakuna masana da manazarta da masu aiwatar da ita (mawaƙa) da ‘yan kallo (waɗanda ake yiwa suna saurarawa, amma ba su da wannan hikimar). Hikimar waƙa tana zama wata baiwa ga wanda Allah ya bai wa ita, na sassaƙa kalmomi masu sautiɗaya ko tsariɗaya ko sarrafa rumbun kalmomin harshe a faɗe su cikin wata siga mai tsari da armashi da gwanewa, ta yadda ba kowa ke iya wannan tsari ba. Amma a wajen mawaƙi abu ne mai sauƙi, domin an halicce shi da wannan baiwar. Ana samunɗaiɗaikun jama’a su koyi waƙa, sai dai bisa ga rinjaye, baiwa ce da mutum ke tashi da ita na halitta.

Kenan dai wannan waƙar tana a matsayin jerin kalmomi ne masu bayyana hikima da fasihancin mutum. Waƙa a tsarin adabin Hausawa ta bambanta da zube irin na tatsuniya ko labarai, haka ta sha bamban ta fuskar siga da yanayi da wasan kwaikwayo. Ita waƙa tsarinta yana tafiya da karin murya mai daɗi, yadda zai burge mai saurare ko nazari. Za mu waiwayi ra’ayoyin masana dangane da ma’anar waƙa domin jin ta bakinsu.

#### 2.3.1.2 Ma'anar Kiɗa da Waƙa Bisa Ra'ayoyin Malaman Hausa

Masana da manazarta sun bayyana ra’ayoyinsu mabambanta dangane da ma’anar waƙa. kamar yadda muka san ana rarrabe muna akwai waƙar baka da kuma rubutacciya. Daga cikin masanan akwai waɗanda suka bayyana ma’anar waƙar baka kaɗai, aka waɗanda suka bayyana ma’anar rubutacciyar waƙa. akwai waɗanda suka gwama ma’anonin wuriɗaya. Tun da cewa muna magana ne kan waƙar baka, za mu taƙaita kan kawo ra’ayoyin da suka keɓanta kan waɗar baka kaɗai kamar haka:

Yahya, (1997)[9] ya bayyana waƙa da:

“Waƙa tsararriyar maganar hikima ce da taƘunshi saƙo cikin zaɓaɓɓun kalmomi da aka auna domin maganar ta reru ba faɗa kurum ba.”

Shi ma Gusau (2003: iii)[10] ya bayyana cewa:

[9]Yahya, A. B (1997) Jigon Nazarin Wa}a. Fisbas Media Ser~ice, Kaduna. Shafi na 4.

"Waƙa zance ne shiryayye cikin hikima da azanci da yake zuwa gaba-gaba bisaƘa'idojin tsari da daidaitawa, a rere cikin sautin murya da amsa-amo na kari da kiɗa, sau da yawa kuma a tare da amshi."

Ta la'akari da ra'ayoyin da aka gabatar, mun fahimci akwai wasu keɓaɓɓun kalmomi da suka danganci waƙa da suka haɗa da shiryawa/tsarawa da hikima da zaɓen kalmomi da aunawa da kiɗa da sautin murya da amshi da sauransu da dama. Waɗannan siffofin su ne suka haɗu, suka bayar da waƙar baka ta Hausa.

### 2.3.1.3 Dangantakar Kiɗa da Waƙa Bisa Ra'ayoyin Malaman Hausa

A magana ta yau da kullum, kiɗa kan zauni ma'anar waƙa, haka waƙa kanɗauki matsayin kiɗa. Sau tari sai mawaƙi ya ce " sai na kai mai kiɗa", wannan ba ya nufin sautin kiɗa kaɗai ba, wato a yi ta buga gangumma; ana kai gayyar kiɗan gangumma lokacin da ake rera waƙa. Idan kuma aka ce 'an waƙe shi' to waƙar an yi mata rakkiya da waƙa. Idan har akwai wannan fahimtar, to ana iya bayyana ma'anar kiɗa da waƙa da cewa " tsararren zance ne na hikima wanda aka shirya cikin gunduwowi, wasu lokutta ana gabatar da shi ga masu tsaurare tare da sautin da zai ba shi armashi domin jin daɗin masu sauraro.

**Auna Fahimta**

1. Duba ra'ayoyin masana mene ne tushen ginuwar waƙoƙin baka na Hausa?
2. Waƙoƙin baka sun zama tamkar wata makaranta a wajen Hausawa. Yi ɗan tsokaci dangane da haka.

**Kammalawa**

Wannan darasi ya yi shimfiɗa kana bin da za a tattauna a wannan kwas wanda shi ne waƙa. Ya yi tsokaci kan waƙar baka da samuwarta, sa'annan aka biyo da ra'ayoyin masana dangane da waƙa da suka haɗa da Yahya (1997) da Gusau (2003) da Gusau (2008) da sauransu. Sa'annan mun ga kiɗa da waƙa a tare da ma'anarsu. DagaƘarshe an tsara tambayoyin auna fahimta gaɗalibai.

[10] Gusau, S. M (2003)

## 2.4 Taƙaitawa

- Bayyana samuwar waƙar baka a cikin al'ummar Hausawa kaƘarfafata da hujjoji
- Kawo ra'ayoyin masana biyu (2), da aka gabatar dangane da ma'anar waƙa tare da sharhi akai
- Yi bayani mai gamsarwa kan kiɗa da waƙa a waƙoƙin baka na Hausa.

## 2.5 Jingar Aiki

- Ta yaya za a rarrabe tsakanin Tunanin Gusau, S. M (2003) *Jagoran Nazarin Waƙar Baka*, Bench Mark Publishers, Kano da Yahya, A. B (1997) *Jigon Nazarin Waƙa*. Fisbas Media Serɓice, Kaduna. ta fuskar waƙa?
- Me ya bambanta ma'anar kiɗa zahirance da ta fuskar lugga?

## 2.6 Manazarta

Bunza, A. M (2006) *Gadon Feɗe Al'ada*. Tiwal Nigeria Limited, Lagos. Shafi naii.

Gusau, S. M (2008) Waƙoƙin Baka a ƙasar Hausa: Yanaye-yanayensu da Sigoginsu. Benchmark Publishers Limited, Kano. Shafi na 54

Gusau, S. M (2013) Dangantakar Waƙoƙin Baka da Al'adun Hausawa, in Excerpts of International Seminar on ***Deterioration of Hausa Culture***, Organize by Katsina State History and Culture

Bureau in Collaboration with Ummaru Musa 'Yar'aduwa Uniɓersity, Katsina, Pages 743-58, ISBN-125-633-8

Gusau, S. M (2003) *Jagoran Nazarin Waƙar Baka*, Bench Mark Publishers,Kano

Gusau, S. M (2014) *Waƙar Baka Bahaushiya (The Hausa Oral Song)*. Bayero Uniɓersity Kano, Inaugural Lecture Series no.14.

Ibrahim, M.S (1974) Kowa Ya Sha Kiɗa . Roukhba Publishers, Kano. Shafi na ɓii-ɓiii.

Sa'id, B (ed). (2006) *ƙamusun Hausa*. Wallafar Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya. Jami'ar Bayero Kano. Ahmadu Bello Uniɓersity Zaria. Shafi na 243.

Sarkin Sudan, I. A (2008) Jiya Ba Yau Ba: Waiwayen Rayuwar Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa. Kundin Digiri na Uku, Jami'ar Usmanu ɗanfodiyo, Sakkwato. Shafi na 335.

Yahya, A. B (1997) *Jigon Nazarin Waƙa*. Fisbas Media Serɓice, Kaduna. Shafi na 4.

## 2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1 Masana waƙa sun yarda da cewa al'adun Hausawa su ne tushen ginuwar waƙoƙinsu, musammanwaƙoƙin baka. Saboda haka waƙoƙin baka na Hausa ana gina su ne ta hanyar hasko al'adun Hausawa kamar sana'o'i da gine-gine da tsarin shugabanci da abinci da sauransu.

2 Haƙiƙa waƙoƙin baka sun zama tamkar wata makaranta a wajen Hausawa, kasancewar suna fahimtar da jama'a abubuwan da za su yi musu jagora a rayuwarsu ta yau da kullum a cikin nishaɗi.

## KASHI NA UKU RERAWA

### Abubuwan da Suke Ciki

3.1 Gabatrawa
3.2 Manufar Darasi
3.3 ƙunshiyar
  3.3.1 Ma’anar Rerawa
  3.3.2 Rauji
  3.3.3 Gaɓa
3.4 Taƙaitawa
3.5 Jingar Aiki
3.6 Manazarta
3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

### 3.1 Gabatarwa

A wannan darasi za a tattauna wani al’amari da ya shafi sautin da ke tafiyar da waƙa wanda ake kira rerewa da raujin waƙa. kamar yadda bayanai suka bayyana a kashi na farko da na biyu a cikin wannan kwas, rerewa ita ta bambanta waƙa da magana ta yau da kullum, saboda haka ma ake ganin in ba rerewa to babu waƙa.

### 3.2 Manufar Darasi

AƘarshen darasi ana sonɗalibai su san ma’anar rerawa, da rauji da gaɓa. Sanin waɗannan shi ne shimfiɗar ga neman yadda ake nazarin waƙa, musamman waƙar baka ga mai sha’awar yi wa waƙar tarke.

### 3.3 ƙunshiyar Darasi

#### 3.3.1 Ma’anar Rerawa

Rerawa wata dabara ce ta daidaita murya a cikin halin waƙa. Mawaƙi kan daidaita rauji da kiɗa a yayin furta gabar kalma a lokacin rerawar waƙa.

Wata babbar sifa ce daga cikin siffofin waƙoƙin baka na gargajiya. Bayan mawaƙi ya Ƙulla zaren tunanin shirya baitocin waƙa daƘudirin

da yake da shi kan fannin da zai waƙe da bayanan da zai jeranta na tunani a cikin waƙa, sai kuma ya yi tunani sigar da zai rera waƙar ta yadda za ta fito da saƙon da yake da shi, ya sadar da shi ga al'umma. Kowane mawaƙi yana da nasa azanci da kuma murya da za ta fito da baitukansa ga fili. Murya wani wani ta sha bamban da ta wani wajen rera waƙa. Sau da yawa ko waƙa tana da ma'ana, idan ba ta samu rerawa mai kyau ba, saƙon waƙar ba zai samu isa ga al'umma yadda ya kamata ba, kuma ba za ta yi armashi ba.

### 3.3.2. Rauji

Rauji na nufin masaukar murya a gaba. A cewar Gusau, (2014:23) inda ya kawo ma'anonin rauji a luggance da kuma a ilmance. Murya kan tashi sama, ko ta faɗiƘasa, ko kuma ta sunkuya. Waƙoƙin da ake rerawa tare da kiɗa su suka fi yawa a rukunin waƙoƙin baka na Hausa. Littafin Makaɗa da Mawaƙan Hausa na I & II na Gusau, (2000) yanaɗauke da bayani dalla kan rerawa da rauji a cikin waƙoƙin makaɗan Hausa.

Kenan hauhawa da sakewa da muke ji a cikin waƙoƙinmu nab aka na gargajiya, shi ma wani hikima ce da mawaƙa ke amfani da ita wajen rera waƙoƙinsu. Da za a ce waƙoƙin su tafi baiɗaya ba tare da lanƙwasa ba, ko hayi da gangare, abin ba zai bayar da ma'ana ba. Amma sai a samu wata gaɓa a cikin baiti da idan an kawo kanta, an san za aɗaga murya ne ta tashi sama, wata gaɓa kuwa idan aka zo gar eta ba makawa ko mai biyar waƙa ya san da cewa sauke murya za a yi. Wannan hawan da sauka baƘaraminƘayatar ba ne da ke tattare a cikin waƙoƙin baka na gargajiya.

### 3.3.3 Gaba

Dukkanin maganganun da muke furtawa nay au da kullum suna tafiya ne bisa tsarin gaɓa. Gaɓoɓi ne ake haɗawa daban-daban su bayar da kalmomi masu ma'ana waɗanda ake zaɓowa daga cikin rumbun kalmomin da muke da su don gabatar da zance. Waƙa ma zance ne, sai dai tana da wasu sigogi da suka bambantata da maganarmu ta yau da kullum, sa'anna aƘoƙarin samar da biyan buƙata a fagen waɗa, ana karya dokar maganarmu da muka saba yi, don a samu biyan buƙata.
A fannin waƙa, gaba na nufin sashen kalma. Kalmomin da ake jerawa a cikin waƙa domin su ba da ma'ana suna cikin siffar gabobi ne. Misali kalmar waƙa tana da gaba biyu. *wa*daƘ*a* idan ana rera waƙa, to wajen furta kowace gaba ne ake samun rauji. Mun ga ma'anar rauji bayanin da ya gabata mailamba 1.3.2

**Auna Fahimta**

| | |
|---|---|
| 1. | Me ake nufi da Rerawa? |
| 2. | Kawo ma'anar Rauji da gaɓa a taƙaice? |

**Kammalawa**

Muna sauraren waƙoƙin baka da dama har akwai waɗanda muke riya muna son su, don suna yi muna daɗi. Amma da yawa ba za mu iya cewa ga dalilin da ya sa waƙoƙin suke bisa tsarin da muke ganinsu ko mu saurare su ba. hasali ma ko mawaƙan da ke da fasaharƘulla zaren waƙa ba za su iya sanin irin hikimomin da ke Ƙunshe a cikin waƙoƙin da suke shiryawa su rera. Sirrin wannan lamarin shi ne kiɗa da rerawa da rauji da gaɓa da baituka da ake tsattsarawa cikin waƙa don su bayar da ma'anar da ake buƙata, kamar yadda aka yi bayaninsu a cikin wannan darasi.

## 3.4 Taƙaitawa

- An fahimci rerawa tana taimakawa wajen fitar da ma'anar waƙa.
- Rerawa kanta wani salo ne da mawaƙa ke amfani da shi domin su jawo hankalin masu saurarensu su fahimci saƙon waƙar ko saƙon mawaƙi.

## 3.5 Jingar Aiki

- A naka/naki ra'ayi me ye dangantakar kida da waƙa?
- Daga cikin Waƙoƙin baka akwai masu zuwa da kiɗa da waɗanda ba su zuwa da shi tattauna tare da misalai daga waƙoƙin masana.
- Yi bayanin kiɗa mai amfani wanda ba ya zuwa da waƙa tare da misalansa da ka/ki sani.
- Yi taƙaitaccen bayanin waɗannan: kiɗa, rerawa, rauji da gaɓa.

## 3.6 Manazarta

Gusau, S. M. 2011. Tarihi Da Hanyar Nazarin Waƙar Baka Bahausiya. A Cikin *Waƙoƙin Baka Na Hausa*. Century Research and Publishing Limited, Kano.

Gusau, S. M (2014) Waƙar Baka Bahaushiya (The Hausa Oral Song). Bayero Uniɓersity Kano, Inaugural Lecture Series no.14.

Ibrahim, M.S (1974) Kowa Ya Sha Kiɗa. Roukhba Publishers, Kano. Shafi na ɓii

**3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta**

1. Rerawa dabara ce da ake daidaita murya a cikin halin waƙa.
2. Rauji na nufin hauhawa da sakewa da saukewar murya a waƙa. A fannin waƙa gava na nufin sashen kalmomi na waƙa.

# KASHI NA HUƊU DANGANTAKAR KIƊA DA WAƘA

## Abubuwan da Suke Ciki

4.1 Gabatarwa
4.2 Manufar Darasi
4.3 ƙunshiyar Darasi
 4.3.1 Dangantakar Kiɗa da Waƙa
 4.3.2 Kiɗa Mai Ma'ana Wanda ba ya Zuwa Tare da Waƙa
 4.3.3 Waƙoƙin da Ake Rerawa ba Tare da Kiɗa ba
 4.3.4 Waƙoƙin da ke Tafiya Tare da Kiɗa
4.4 Taƙaitawa
4.5 Jingar Aiki
4.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Nazari
4.7 Amsoshin Amsoshin Auna Fahimta

## 4.1 Gabatarwa

Wannan darasi ci gaban wanda aka faro ne daga farkon wannan kwas. Wanda yana magana ne kan kiɗa da waƙa a cikin asl'ummar Hausawa, kuma kiɗan ma na gargajiya wanda aka taso da shi tun tali-tali. Bayan an gabatar kiɗa da waƙa a can baya, muradin wannan darasi shi ne yaƘara zurfafa wajen bayyanan kayan cikin kiɗa da waƙa. TaƘoƙarin samar da abin da ake son gabatarwa, an kalli dangantakar kiɗa da waƙa kasancewarsu suna tafiya kafaɗa da kafaɗa, sa'annan aka yi nutsu wajen bayanan abubuwan da ke wakana a cikin kiɗan da waƙa kamar rerawa da rauji da gaɓa da sauransu kamar yadda za mu gani cikin darasin.

## 4.2 Manufa

Kamar yadda sauran darussa sukeɗauke da manufa ko maƙasudin aiwatar da su, shi ma wannan maƙasudinsa ba zai wuce abubuwa kamar haka:

- Danganta kiɗa da waƙa a faifan nazari
- Bayanin kan nau'o'in kiɗa da muke da su ga dalibai
- Zurfafawa kan abubuwan da keƘarƙashin waƙar baka da su ke tallafa mata wajen tsayawa daƘafafunta

## 4.3 Ƙunshiya

### 4.3.1 Dangantakar kiɗa da waƙa

Kamar yadda aka bayyana tun a gabatarwar wannan darasi, wannan darasi da wanda ya gabata ruhinsuɗaya, kuma dukkaninsu shimfiɗa ga kwasɗin ba kiɗaya. A nan za a ci gaba da inda aka tsaya na zurfafawa kan bayanin kiɗa da waƙa.

Dangantakar kiɗa da waƙa ta samo asali tun wurin haihuwarsu, domin kuwa masana ba su rarrabe wajen samuwarsu ba. Duk inda ake maganar samuwarsu, to ana danganta su da tusheɗaya. Ibrahim (1974)[11] ya bayyana hakan inda yake cewa, ana hasashen ɗan adam ya samu kiɗa ne a lokacin day a fara neman abinci ta hanyar farauta. Daga baya ne mutane suka fara yaƙe-yaƙe tsakaninsu, inda sana'ar ta kiɗa taɗaraƘasaita. Wannan hasashen ana ganin ya shafi samuwar kiɗa ne a al'ummomi na duniya gabaɗaya, ba al'ummar Hausawa kaɗai ba.

Wannan ya nuna muna cewa kiɗa da waƙa tagwayen juna ne tun asali, wanda har ta sanya ake yi musu kallon abuɗaya. Wannan ya sa idan har za a aiwatar da su ana tafiya da su lokaciɗaya, domin dacewarsu. Saboda irin dangantakar da ke tsakanin kiɗa da waƙa ana iya shigar daɗayan cikinɗayan a kirasu da sunaɗaya ba tare da wata damuwa ba. Misali waƙa, idan aka ambace ta a cikin maganar yau da kullum, babu buƙatar ace kiɗa, domin ana ganin ai ta haɗe kiɗan domin suna tafiya tare da juna, musamman ga 'yan gargajiya. Haka sau da yawa ga 'yan zamani idan suka ce kiɗa, to ba makawa suna nufin abu biyu, wanda ya haɗa kidan da waƙa. Don haka dangantakar biyun ta sa ake yi musu kallon abuɗaya.

Duk da cewa suna iya zama daban-daban ba tare da an gwama su wuriɗaya ba. Amma lamarinsu zancen Bahaushe ne da yake cewa 'in ka ga raƙumi ka ga buzu'. Anan za mu so mu ga dangantakar kiɗa da waƙa, kasancewar an ga ma'anar kowanensu a kashin da ya gabata, sa'annan a dubaɗananan rukunnan da biyowaƘarƙashinsu. Wannan kashin tamkarƘarin bayani ne ga kashin da ya gabata.

### 4.3.2 Sauti a Matsayin Kiɗa

Sauti na nufinƘara wacce za a ji da kunnuwa. Ana samun sautuka a cikin abubuwa mababanta masu rai da marasa rai. Kamar sautin iska, sautin saukar ruwa, sautin tafiya, sautin magana da sauransu. Sai dai

[11]Ibrahim, M.S (1974) *Kowa Ya Sha Ki]a* . Roukhba Publishers, Kano. Shafi na ~ii.

dukkanin sautukan da aka ambata ba su ake son yin magana ba a nan. Wannan nau’in sauti ana samar das hi da niyya ko da gangan don biyan buƙatar rayuwa. Sa’annan ana amfani da wasu abubuwa da za su taimakawa wajenɗaukaka sautin daƘara masa armashi da amsa-amo ga masu saurare. Waɗannan ababen su ake kira kayan kiɗa. su kuwa kayan kiɗan sun bambanta dangane da nau’in kiɗan da ake so a aiwatar. Sautin da za a samar ya ratsa jiki ya sanya mutum ya tashi ya tattaka ko ya rausaya ko ya jujjuya jikinsa, to akwai saƙon da wannan sautin ya sadar ga mai rausayawar. Idan har aka samar da amo na kiɗa, jama'a duk inda suke suka taru domin a sadar musu da wani saƙo; da wannan za a fahimci kiɗa wani sauti ne mai bayyana saƙo daga mai samar da shi zuwa ga al'umma. Kiɗa kuma kamar ma'anarsa ta sama, saƙo ne ake sadarwa ga jama'a cikin hikima.

### 4.3.3 Kiɗa mai Ma'ana Wanda ba ya Zuwa Tare da Waƙa

Kamar yadda aka bayyana a baya, akwai kiɗa mabambanta da ake aiwatarwa don manufofi da dama. Kowanne yana dacewa da manufar da aka aiwatar das hi dominta. Ire-iren waɗannan sautukan kiɗa sun haɗa da kiɗa wanda ake yi domin nishaɗantarwa amma ba ya zuwa tare da waƙa. Kamar irin kiɗe-kiɗen da ake yi domin gabatar da shirye-shirye na gidajen Rediyo, duk sautuka ne na kiɗa waɗanda aka shirya ba tare da waƙoƙi ba. Wannan nau'in kiɗa ana ba shi fassara daidai da fahimtar mai sauraro. Misali "tititi-tititi, tititit-tititi" *ga mu ga sakkwato, babu halin shiga,* wannan sautin za a ga kowane gidan rediyo yana da nasa. Kamar gidane rediyon jihar jigawa na da nasu kiɗan kamar haka "dididi-dididi" *Jigawa na kira*. Da yawan irin waɗannan kiɗe-kiɗe musamman na garuruwa sunaƘunshe da tarihi na wani abu da ya taɓa faruwa, sai a riƙa ambatonsa a cikin kiɗa.

### 4.3.4 Waƙoƙin da ake Rerawa ba Tare da Kiɗa ba

Duk da cewa mafi yawan waƙoƙin baka suna tafiya ne tare da kiɗa, wanda kiɗan na daga cikin siffofin da suka rarrabe tsakanin waƙar baka da rubutacciya. Akwai wasuɗaiɗaikun waƙoƙin Hausa waɗanda ake rerawa ba tare da kiɗa ba. Sai dai tsurar kalamai da sauka da direwar murya ba tare da kiɗa ba. irin waƙar da Mawaƙi Lauwali Kandab'ula Gusau ya rera wa Sani Yariman Bakura. Turken waƙar "Sani Yarima Maso Gaskiya". Mawaƙi ɗan Shata ya rera waƙarsa kan "Yaƙin Neman Jahar Zamfara", ita ma wannan waƙar ba ta da kiɗa. Akwai kuma makaɗa Shamsu Fuwa a waƙarsa ta Umaru Musa ‘Yar’aduwa (tsohon ShugabanƘasar tarrayyar Nijeriya), wadda ya rera babu kiɗa, sai dai tafi da hannu da yaransa ke yi domin amon waƙar ya tafi da tafin.

### 4.3.5 Waƙoƙin da ake Rerawa Tare da Kiɗa

Waƙoƙin da ke tafiya tare da kiɗa su ne suka fi yawa a cikin waƙoƙin baka, kuma su al'umma suka fi sani. Waɗannan waƙoƙin idan za a yi duba kan su suna dam akaɗa da yawa daga ɓangarori daban-daban naƘasar Hausa, waɗanda sun rayu ne zamani daban-daban. Akwai sunayen waɗannan makaɗan da misalan waƙoƙinsu har ma da hotunansu. Waƙoƙin da ke tafiya tare da kiɗa sun fi daɗi da armashi, domin akwai sauti mai tashi daga kayan kiɗan Hausa na gargajiya da na zamani waɗanda ake amfani da su wajen samar da sautin da zai tafi daidai da muryar waƙa. Idan sautin kiɗa ya fara tashi, ga kuma muryar waƙa, to dole hankali da tunani su karkata ga mawaƙi domin a fahimci saƙonsa. Misalan waƙoƙin baka na Hausa waɗanda ke tafiya tare da kiɗa akwai:

Waƙar Alƙali Abu ta Makaɗa Ibrahim Narambaɗa Tubali. Da Waƙar Sarkin Sudan na Kwantagora Mu'azu wadda Salihu Jankiɗi ya yi masa. Da Waƙar Alhassan Sarkin Dogarai wadda Mamman Shata Katsina ya rera masa.

**Auna Fahimta**

**1.** Me za ka/ki ce dangane da samuwar kixa?
**2.** Da gaske an fi yin waƙoƙin Hausa na baka tare da kixa?

**Kammalawa**

Wannan darasi an tattauna kan dangantakar kiɗa da waƙa, inda aka fahimci cewa suna da bambanci ta kowace fuska wato a zahirance da a luggance, amma kuma dangantakarsu taƘ*uƙut* ce inda har masu sauraron waƙo ke ganin ana kiran kiɗa da sunan waƙa, haka nan ana kiran waƙa da sunan kiɗa. Kuma ana kiran kiɗa da waƙa da sunan kiɗa kawai, haka nan ana kiran waƙa kawai da sunan waƙa kawai idan ba kiɗa



### 4.4 Taƙaitawa

- An fahimci dangantakar kiɗa da waƙa wadda kiɗa shi ne ginshiƙin sanya waƙa ta yi armashi
- An ga rukunin mawaƙa masu amfani da kiɗa, da waɗanda ba su amfani da kiɗa sai dai zubin waƙa kawai ta hanyar rerawa, da kuma tafi
- An kuma tantance rabe-raben makaɗa da mawaƙa

## 4.5 Jingar Aiki

- Bayyana dangantakar kiɗa da waƙa a taka fahimta?
- Mene ne bambancin waƙa da maganar fatar baki ta yau da kullum?
- Akwai rukunin waƙoƙin da ba su da kalmomi, yi bayyani a kansu

## 4.6 Manazarta

Bunza, A. M (2006) *Gadon Feɗe Al'ada*. Tiwal Nigeria Limited, Lagos. Shafi naii.

Gusau, S. M (2008) Waƙoƙin Baka a ƙasar Hausa: Yanaye-yanayensu da Sigoginsu. Benchmark Publishers Limited, Kano. Shafi na 54

Gusau, S. M (2013) Dangantakar Waƙoƙin Baka da Al'adun Hausawa, in Excerpts of International Seminar on ***Deterioration of Hausa Culture***, Organize by Katsina State History and Culture Bureau in Collaboration with Ummaru Musa 'Yar'aduwa Uniɓersity, Katsina, Pages 743-58, ISBN-125-633-8

Gusau, S. M (2003) *Jagoran Nazarin Waƙar Baka*, Bench Mark Publishers,Kano

Gusau, S. M (2014) *Waƙar Baka Bahaushiya (The Hausa Oral Song)*. Bayero Uniɓersity Kano, Inaugural Lecture Series no.14.

Ibrahim, M.S (1974) Kowa Ya Sha Kiɗa . Roukhba Publishers, Kano. Shafi na ɓii-ɓiii.

Sa'id, B (ed). (2006) *ƙamusun Hausa*. Wallafar Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya. Jami'ar Bayero Kano. Ahmadu Bello Uniɓersity Zaria. Shafi na 243.

Sarkin Sudan, I. A (2008) "Jiya Ba Yau Ba: Waiwayen Rayuwar Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa". Kundin Digiri na Uku, Jami'ar Usmanu ɗanfodiyo, Sakkwato. Shafi na 335.

Yahya, A. B (1997) *Jigon Nazarin Waƙa*. Fisbas Media Serɓice, Kaduna. Shafi na 4.

## 5.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Kamar yadda Ibrahim (1974) ya bayyana akwai hasashe dangane da samuwar kixa, inda ake ganin ɗan adam ya samu kiɗa ne a lokacin da ya fara neman abinci ta hanyar farauta. Daga baya ne mutane suka fara yaƙe-yaƙe tsakaninsu, inda sana'ar ta kiɗa taɗaraƘasaita.
2. Eh gaskiya ne waƙoƙin baka na Hausa sun fi tafiya tare da kixa kasancewar kixan shi ke ƙarawa waƙar armashi.

## RUKUNI NA BIYU

| | |
|---|---|
| Kashi na Ɗaya | Makaɗa da Mawaƙan Hausa |
| Kashi na Biyu | Kashe-kashen Waƙoƙin Baka |
| Kashe na Uku | Kashe- kashen Waƙoƙin Baka I |
| Kashe na Huɗu | Kashe- kashen Waƙoƙin Baka II |
| Kashi na Biyar | Waƙoƙin sanyi da damana,da kakar abinci |
| Kashi na Shida | Kashe-kashen Waƙoƙin Baka Dangane da Jigoginsu |

## KASHI NA ƊAYA MAKAƊA DA MAWAƘAN HAUSA

### Abubuwan da Suke Ciki

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufar Darasi
1.3 ƙunshiyar
 1.3.1 Makaɗan Baka Maza
 1.3.2 Makaɗan Baka Mata
 1.3.3 Haɗakar Mawaƙa
1.4 Taƙaitawa
1.5 Jingar Aiki
1.6 Manazarta
1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



### 1.1 Gabatarwa

A kashin farko an yi tsokaci kan kiɗa ma’anarsa da irie-irensa. Aɗaya daga cikin kason an ga ma’anar waƙa bisa ra’ayoyin masana. A wannan kashin za a tattauna game da masanan su kansu sha’awarsu a fagen waƙa. Za a gaƘumshiyar mawaƙan.



### 1.2 Manufar Darasi

Bayyana mawaƙa ta fuskar abubuwan da suke waƙewa. Idan aka ga kason mawaƙa ta wannan fuskar, to za a samu sabon fasalin daban da wanda aka daɗe ana gani na bayyana kason mawaƙan ta fuskar jigo ko kayan kiɗansu. Wannan kamar wata hanya ce ta kallon mawaƙan.

## 1.3 ƙunshiyar

### 1.3.1 Makaɗan Baka Maza

Idan za a yi magana kan waƙar baka, kuma wadda ake amfani da Kalangu ko Taushi, sai ka ji an ambato jerin maza kafin a ammbato mata. Wannan ba zai rasa nasaba da al'adun Hausawa ba, wanda ya shafi wasu sana'o'i sun fi raja'a ga maza, wasu kuma ga mata. Nazarin al'adun Hausawa zai bayyana dalilan dakan sa hakan. Amma a waƙar baka za a ga maza ne suka mamaye wannan ɓangaren duk da cewa har mata akwai. Daga cikin misalan sunayen makaɗa akwai:

Alhaji Musa ɗanƙwairo Maradun, Alhaji Inka Bakura, Alhaji Ibrahim Narambaɗa, Alhaji Shehu Ajilo, Mamman Shata Katsina, ɗan'inna Sabon Birni, Alhaji Maidaji Sabon Birni, Garba Maitandu Shinkafi, Abubakar Kassu Zurmi, Alhaji ɗanba'u Gidan Buwai, Alhaji Babangida Kakadawa, Alhaji ɗanmaraya Jos, Alhaji Sani Sabulu Na Kanoma, Alhaji Sani ɗan'Indo, Alhaji Shehu Ajilo. Sa'adu Bori, Mamman gawo Filinge, Sule Maikwamsa.
Waɗannan misalai ne daga cikin tsofaffin makaɗan baka na Hausa.

### 1.3.2 Makaɗan Baka Mata

Mata suna riƙe kalangu su yi waƙa kamar maza. Kuma ana yi musu kiɗa su yi jagorancin kiɗa da waƙa kamar yaddaƘungiyar maza ke yi. Kason mata a farfajiyar waƙar baka bai kai na maza ba, amma dai akwai mata waɗanda ke da sha'awar waƙar baka kamar yadda za mu ga misalansu a wannan taken:

Kulu Mukkunu, Binta Zabaya Katsina, Hajiya Uwani Zakirai, Malama Nana Maitafasa, Hajiya Amina Rikici Kwatarkwashi, Hajiya Binta Zabaya ɗanbatta, 'yammatan Nijar, ƙungiyar Mata 'yan Kulub (Club), Hajiya Fati ɗiyar Isah, Hajiya Aishatu 'Yarkana, Hajiya Sa'adatu Barmani Coge.
Fitattun mata mawaƙan baka waɗanda ake samu a ɓangare daban-daban naƘasar Hausa.

### 1.3.3 Haɗakar Mawaƙa

An sunaye na maza da na mata mawaƙa. An kuma fahimci duk waɗannan sunayen na manyan mawaƙa ne. To akwai lokacin da jagora yake neman yara maza ko mata ko kuma 'yammata da ''yan samari domin su yi masa karɓin waƙa. Haka nan a dandali za a samu waƙoƙi waɗanda 'yammata ne masuƘananan shekaru, ko samari ke rerawa.

Awannan zangon ana iya cewa akwai waƙoƙin da ake yin haɗaka, manya daƘanana kan gwamatsu su tafiyar da waƙa.

**Auna Fahimta**

| | |
|---|---|
| 1. | Jero makaxan baka na Hausa maza guda biyar |
| 2. | A zayyano maxan baka na Hausa mata guda biyar |

**Kammalawa**

Bayanai ne suka zo domin bayyana waɗanda ake samu a farfajiyar waƙar baka. Kowane rukuni daga cikin al'ummar Hausawa ana samun mawaƙan baka kamar yadda muka gani a sama.

## 1.4 Taƙaitawa

- Daga cikin makaɗa da mawaƙan Hausa akwai mata, (manya da matasa, da yara), akwai kuma maza (manya da matasa da yara)
- Ana kallon rabe-raben mawaƙanbaka dangane da sha'awarsu a fagen waƙa wato abinda suke waƙewa.

## 1.5 Jingar Aiki

- Kawo rukunin mutanen da ke yin waƙar baka ta Hausa
- Ya mawaƙan baka ke haɗaƘungiya wajen sarrafa waƙoƙinsu?

## 1.6 Manazarta

Gusau, S.M. () Makaɗa da Mawaƙan Hausa

Gusau, S. M. 2011. Tarihi Da Hanyar Nazarin Waƙar Baka Bahausiya. A Cikin *Waƙoƙin Baka Na Hausa*. Century Research and Publishing Limited, Kano.

Gusau, S. M (2014) Waƙar Baka Bahaushiya (The Hausa Oral Song). Bayero Uniɓersity Kano, Inaugural Lecture Series no.14.

Ibrahim, M.S (1974) Kowa Ya Sha Kiɗa. Roukhba Publishers, Kano. Shafi na ɓii

## 1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

**1)**

a) Alhaji Ibrahim Narambaɗa
b) Alhaji Shehu Ajilo
c) Mamman Shata Katsina
d) ɗan'inna Sabon Birni
e) Alhaji Musa Xanƙwairo Maradun

**2)**

**a)** Hajiya Uwani Zakirai
**b)** Malama Nana Maitafasa
**c)** Hajiya Amina Rikici Kwatarkwashi
**d)** Hajiya Uwaliya Mai Amada
e) Hajiya Magajiya Xanbatta

## KASHI NA BIYU KASHE-KASHEN WAƘOƘIN BAKA

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufar Darasi
2.3 ƙunshiyar
 2.3.1 Waƙoƙin Baka na Gargajiya
  2.3.1.1 Waƙoƙin Baka Waɗanda ake yi a Dandali
  2.3.1.2 Waƙoƙin Baka Waɗanda ake yi a Cikin Gida
  2.3.1.3 Waƙoƙin da ake yi a filin Yaƙi
2.4 Taƙaitawa
2.5 Manazarta
2.6 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

### 2.1 Gabatarwa

Wannan darasi zai yi magana ne dangane da waƙoƙin da suka shafi muhallan cikin gida da na wajen a cikin waƙoƙin baka na Bahaushe. Mun sani cewa waƙa ta rigaya ta ratsa kowane ɓangare na rayuwar Bahaushe, har ta kai ga ba wani lungu ko saƙo da ba a samunta. Akwai ayyukan cikin gida da ba su tafiya sai da waƙa da suka haɗa dad aka da reno da niƙa da daɓe da sauransu. Akwai kuma waɗanda ake aiwatarwa a wajen gidan Bahaushe kamar a dandali da fagen fama da sauran, wanda duk za a gabatar a cikin wannan darasi.

### 2.2 Manufa

ƙudirin wannan darasi, shi ne a fito da abubuwan da suka shafi hakan:

- Sanin waƙoƙin da ake gabatarwa a cikin muhallin gidan Bahaushe
- Sanin waɗanda ake aiwatarwa a cikin muhallan dab a cikin gida ba
- Da sanin irin jigogin da ke yi wa waƙoƙin jagoranci da sauransu

## 2.3 ƙunshiya

### 2.3.1 Waƙoƙin Baka na Gargajiya

Waƙoƙin baka na garagajiya sun haɗa da waƙoƙin gaɗa waɗanda 'yammata Budare ke yi lokacin da ba su yi aure ba, da waƙoƙin Samari na dandali. Waɗannan waƙoƙin suna rera su a kowane lokaci, ko lokacin bukukuwa ko lokacin nishaɗi. ƙumshiyar waɗannan waƙoƙi faɗakarwa ne kan rayuwar Budurci da samartaka da taka-tsantsan kan haɗɗurran da ke cikin wannan mataki na rayuwa. Waƙar Yara Alo Nanaye ta "yammatan yankin Sakkwato da Waƙar Gwauro ya katse na daga cikin misalan waɗannan waƙoƙin.

#### 2.3.1.1 Waƙoƙin da ake yi a Dandali

Waƙoƙin Dandali su ne 'yammata ke rerawa a dandali da yamma ko da dare bayan an gama cin abinci, kafin a kwanta. Waɗannan waƙoƙin suna tafiya da rawar fyaɗe da tafi. Fyaɗe wani salon rawar 'yammata ne inda suke hajijiya suna juya jiki kamar yanayin guguwa ta iska in ya taso. Inda ake samun yarinyaɗaya ta shiga cikin fage tana waƙa, ta yi juyi ta faɗi abin da ke ranta ta juyo, su kuma sauran matan suna tafa (taɓi) mata. Haka za su ci gaba da yiɗaya bayanɗaya kowace da nata baiti da za ta karanto, idan shiga ta kai kanta za ta fito cikin fage a gane ta, ta faɗi nata baiti ta koma wata ta fito, har aƘare.

ƙumshiyar waƙoƙin dandali na 'yammata sun haɗa da, faɗakarwa kan haɗarin rashin kai bante (budurci), da soyayya da begen masoya da kuma zaman gidan miji. Ana samun jagora a cikin 'yammatan, sai sauran su amsa. Misalin waƙar 'yammata shi ne na *Ruwa Yamma*, wadda 'yan mata ke yin da'ira su riƙe hannuwansu, suna rawa suna rera waƙa, kowace ta shiga ta yi tata rawa harƘarshe kamar haka:

**Bayarwa:** Ye ruwaye
**Amshi:** Ruwa yamma
**Bayarwa**: Albasa ta yi kara
**Amshi**: Ruwa yamma
**Bayarwa**: Yaushe za mu muɗebo
**Amshi**: Ruwa yamma
**Bayarwa:** Gobe za mu muɗebo
**Amshi**: Ruwa yamma
**Bayarwa**: In garin ba nisa
**Amshi**: Ruwa yamma
**Bayarwa**: Can garin Atakulle
**Amshi**: Ruwa yamma

**Bayarwa**: Ye ruwaye
**Amshi**: Ruwa yamma (Gusau 2013:60)[1]

Su ma samari suna da nasu nau'in waƙoƙi da suke gudanarwa a dandali. Mafi yawan waƙoƙin yara maza suna tafiya tare da wasannin motsa jiki. Jigon waƙoƙin shi ne jarumtaka da koyon kariya a fagen yaƙi da koyar da bajinta na zamansu 'ya'ya maza. Misalin waɗannan waƙoƙin su ne a cikin wasan *ɗan na kangal-kangal*, wannan wasar maza sukan yi da'ira, wani na waƙa sauran suna karɓawa. Wannan wasan kowa zai kama abokin wasanshi, ɗayan zai dafe wuyanɗaya, ya sagaleƘafafuwanshi a sama, ya sako hannayenshi da kanshiƘasa kamar jemage suna reto, yadda ba zai faɗi ba. Idan ya sauka shi maɗayan zai yi kwatankwacin yaddaɗayan ya yi, suna rera waƙa kamar haka:

| | |
|---|---|
| • Waƙa | Amshi |
| • ɗan na kangal-kangal | Jemage |
| • Wane dubi sa'anka | " |
| • Kar ka hau kakanka | " |
| • Ko ka hauɗan yaro | " |
| • Ko ka hau tsohonka | " |
| • Na yi nitso na kamo kifi ko ruwa ban sha ba | " |
| • Dan na kangal-kangal | "(Dembo 1972: i)[2] |

### 2.3.1.2 Waƙoƙin da ake yi a Cikin Gida

Kasancewar dukkanin rayuwar matar Bahaushe tana yin ta a cikin gida, idan ba wata lalura ta fita cikin gidan nan ta gitta ba, kamar fitaɗibar ruwa ko yin itace ko yin ziyara da sauran harkokin sada zumunci irin buki da sauransu. Wannan ya sanya tana da waƙoƙin da take aiwatarwa da sukaƘunshi hoton rayuwarta kacokan. Waƙoƙin da ake rerawa a cikin gida sunƘunshi dukkanin ayyukanta na cikin gida da take cikin farin ciki ko baƙin ciki ko gyaran hali ko koke da sauransu. Waɗannan ayyukan sunƘunshi daka da na niƙa da dabe da tawai da sauran ayyukan da mata ke aiwatarwa masuɗaukar lokaci da suke buƙatar waƙa domin saka nishaɗi a lokacin aiwatar da su. Waɗannan waƙoƙin mata ke shirya su suna rerawa a lokuttan da suke gabatar da ayyukan gida domin samun sauƙin yin aikin ba tare jin wata wahala ba. ƙumshiyar waƙoƙin kan nishaɗantar da zuciya, kuma suna faɗakarwa kan halin rauywar yau da kullum. Ma fi akasari waɗannan waƙoƙin manyan mata ke shirya su. Misali waƙoƙin akwai:

[1] Gusau, S. M (2013) Wasanni Don Yara. Century Research and Publishing Company, Kano. Shafi na 60.
[2] Dembo, U (1972) Wasannin Yara. Northern Nigerian Publishing Company, Zaria. Shafi na i.

(a) Waƙoƙin Tawai: waƙoƙi da mata kan amfani da azanci wajen shirya su don aiwatar das u a lokuttan da suke yi wa yaransu tawai. Al'adar kunya gaɗiya musamman 'ya'yan farko ta sanya katanga ga nuna soyayya tsakanin iyaye mata da 'ya'yansu. Amma wannan bai hana cikin tawai mace ta fakaici idanun manya taɗan tawata yaronta don ta nunaƘaunarta da ke tsakaninta das hi, misali:

ɗan farin gilashi ne,
Gilashi ba na mota ba,
ɗan farin agogo ne mai haɗa lokaci daidai,
A ba shi madara a goya shi,
A kai shi wajen farar kaka,
Farar kaka ta goya shi.

Haka ma a cikin wata waƙa, an fitoƘarara an nuna al'adar sakaya tawanɗan fari ga idanun mutane kar a ga wautar uwarsa inda ake cewa:

Tawanɗan fari sai da dare,
Ban yi da rana ba, kar su gani,
Kar maƙiyan Allah su gani,

Bayanɗan farko da ake ɓoyon yin tawansa, dukkanin sauran yara ana yi musu tawai ba tare da an sakaya ba. Wani abin sha'awa ga yin tawai yanaɗauke da wasu kalamai na tarihi masuƘunshe da bayanin rayuwar yaro, kamar gatansa ko wadatar gidansu ko fito da nasabarsa ko bayyana shin a nawa ga jerin haihuwa a wajen iyayensa da sauran bayanan da dama. Haka zalika tawan yana iya zama keɓantacce ga sunan yaro, ta hanyar amfani da sunansa wajen yi masatawai. Wannan ya sanya ake samunɗaiɗaikun sunayen da suke da tawansu na musamman wanda da an ambato sunayensu an san tawansu misali:

Maryam: Meri maryam 'yar lele
Kyawo ya hana taɓawa

Hauwa'u: Hauwa'u mai miya da gudan sa
In ka ji sallaɓa rago ne
Salab-salabɗan akuya
Miyar kaɗi koɗan kaza
Gidan da babu Hauwa ya zama kango

Nana: Nanuwa 'yar Shehu uwar gari
Ba ta aureɗauye ta sha wuya
Daga sarki sai attajiri
Sai ko wani babban malami

Aliyu: Ali zakin fama

Yusuf: Yusufuɗa, Yusufu bawa, Yusufu Sarki

Wani babban muhimmancin da tawai yake da shi a cikin a'ummar Hausawa, shi ne yana bai wa uwa damar ta nuna soyayyarta gaɗanta, sa'annan ta samar da nishaɗi a lokacin take zaman kaɗaici ita da yaro. Tawan na zama hanyar motsa jiki da sanya kuzari ga yaran. Wanda idan har ana yi musu shi, har zallo suke suna nuna jin daɗinsu da fara'arsu da uwayensu mata. Ta hanyar tawai mace na iya bayyana halayyar da take ciki na rayuwar aurenta na jin daɗi ko akasin haka. Wanda cikin azanci za ta bayyana irin rayuwar da take a gidan miji.

(b) Waƙoƙin Dabe: daɓe wani aiki ne na matan Hausawa wanda yake tafiya daƘarfi wajen aiwatar da shi. Al'adar daɓe ta daɗe a cikin al'adun matan Hausawa da ake yi wa waƙa, amma saboda wasu dalilai ya sanya waƙoƙin sun ɓace sai dai masana suna ambato cewa akwai waƙoƙin a cikin ayyukansu amma ba su gabatar da waƙoƙin. dalili kuwa shi ne, wannan al'adar ta faro tun kafin zuwan musulunci, kasancewar mata zalla ke haɗuwa wajen yin wannan aikin, dama idan mata suka haɗu tsakaninsu suna cire kunya su riƙa tattauna halayyar rayuwarsu musamman zamantakewarsu ta aure da mazajensu. Wannan ya sanya mafi yawan waƙoƙin sukeƘunshe da batsa na abubuwan da suka shafi zaman aure da sauransu.

(c) Bayan zuwan musulunci, duk irin waɗannan waƙoƙin da suka saɓawa koyarwar addinin musulunci aka yi watsi da su face kaɗan daga cikinsu da ba suɗauke da kalaman ɓatanci. Sannu a hankali, waƙoƙin suka fara ɓacewa a cikin al'umma, domin an daina aiwatar da su, kuma malaman da suka yi rubuce-rubuce a cikin waɗannan ɓangarorin sunƘyamaci ambatonsu. Misalin waɗannan waƙoƙin su ne:

**Bayarwa:** Kaico duniya gidan aro
**Amshi:** Kaico duniya gidan aro
**Bayarwa**: Kaico lahira matabbata
**Amshi:** Kaico lahira matabbata
**Bayarwa**: Ana kwanan dole wata rana,
**Amshi:** Ana kwanan dole birirƘasa, Tabarma babu balle gado

Su waƙoƙin daɓe, manyan mata da suka yi aure suka kai wasu shekaru ke yin su. Al'adar daɓe ta samu asali idan aka yi aure, kafin mace ta tare gidan miji, ɓangaren mata suna neman izinin a ba suɗakin daɗiyarsu za ta zauna don su je su gyaraɗakin su yi jere. Duk matar da ba ta isa wankeɗiya ba, ba ta kai munzalin da za ta yi daɓe ba. Amma idan ta kai ga aurar daɗiya, za ta gayyato abokanta, ta hanyar raba musu goro, don

su zo su yi mata kara, na gyara mataɗakinɗiyarta. A lokacin iyayen ango za su ba suɗakin da za su gyara wanda nan ne amaryarsu za ta zauna. Ranar da za a yi daɓen dukkanin gidajen sun san da zaman ranar. Matan za su yi sammako su je gidan su fara yin aikin, suna waƙe-waƙensu har su gama. Su kuma ɓangaren ango, za su yi musu abinci da za sub a su don karramawa. A baitukan da za su biyo baya, za mu ga cewa mata ne ke yi wa uwar miji habnaici na taƘi ta karrama sun a basu abin tarbo da aka al'adanta kamar haka:

Kai ku daɓa mata,
Ba don halinta ba,
Tuwo ba ta ba mu ba,
Ba don halinta ba,
Hura ba ta ba mu ba,
Ba don halinta ba,
Kai ku daɓa mata,
Ba don halinta ba.

Daɓe yana a matsayin filastarɗaki ta gargajiya. Damaɗakunanmu na gargajiya idan akaƘare, suna tattare da ɓurji da tudu da gangare. Shi kuwaɗakin amarya ana so a yi masa lebur, ya tafi daidai a shafe, ya yi sha'awa. A yayin yin wannan aikin abokan ango za su kaiƘasa ta ɓurji su zuba cikinɗaki, su kuma matan za su samu wani abin bubbugaƘasa tare da yayyafa ruwa, sa'annan a samu ɓawanɗiyanɗorawa a dafa su, a riƙa watsawa cikinɗakin don ya yi sulɓI ya yi launin baƙi, wanda shi ne a matsayin fenti. A jiƙa sai ya jiƙu, a riƙa yayyafawaɗakin a yi layi-layi kamar yadda akeɗauko sharanɗaki, a biyo wata na gaba, wata na binta, suna yayyafa ruwan kalar, yana jiƙa lakar da ke cikinɗakin, suna sa mabugi suna daɓewa ko daddale wurin tamkar an simince wajen. Irin sun gamaɗaki zai fito zar kyau saboda an daidaita shi da mabugi, sa'annan sai a sami wani abin yin zane ko kara, a ja layi-layi ga jikin bangonɗakin tun bai bushe ba, sai ya bayar da wani zane mai ban sha'awa. Haka ake yi waɗakin amarya, abin gwanin ban sha'awa (Hira da Hajiya Nasara Bello Dodondaji).

(c) Waƙoƙin Daka: daka yana daga cikin ayyukan mata na cikin gida mai wahala da gundurarwa, domin yana tafiya daƘarfin jiki. Don haka matan Hausawa ba su bar daka haka nan ba sai da suka samar masa da hanyar sauƙaƙa shi, don su rage wahalar da ke cikinta da saka nishaɗi a lokacin aiwatar da shi. A cikin dakan nan suke faɗan rayuwarsu da kokensu da zamantakewarsu da farin cikinsu. Wannan ya sanya tsakan kishiyoyi suke amfani da daka wajen nuna kishinsu ga juna, indaɗaya za ta sa daka ta soki abokiyar zamanta, ita ma ko ba ta yi niyyar yin dakan ba, za taɗebo tata tsaba ta saka a turmi don ta mayar da nata martani.

Kusuɗebo muna wutaɗakin Mage,
ɗakin Mage ba wuta saiƘwanƙwammai,
Haba kusu, saiƘwanƙwammai,

Da jin wannan waƙar an san da wadda ake, wadda ita ce abokiyar zama. ɗayar tanaƘoƙarin ta nuna cewa mata ba da kome cikinɗakinta sai iskoki, inda ta yi mata kinaya da suna mage. Wani abin ban sha'awa da dakan nan shi ne, matan suna amfani da turmi da taɓarya ta hanyarƘwanƙwasa, don samar da sautin kiɗan da suke so. Aɗayan baitin da za a gabatar za a ga sa-in-sa tsakanin abokan zama, duk a a cikin daka kamar haka:

Amarya: Yaya kurciya, yaya cilikko yaya suda
Yaya in kina wa Allah ki bar gidan nan

Uwargida: Wallahi ban barinsa, wallahi ban barinsa
Amarya: koɗiya maza ki haifa kina barinsa
Bale waɗannan 'yan mata 'yan daɗin takaici
Yaya ba ta wa Allah, ba ta wa ma'aiki.

(d) Waƙoƙin Niƙa: kamar waƙoƙin daka, su ma ana yin su saboda sauƙaƙa wahalar aikin. A da can lokacin da babu ci gaban injin, mata suna daka abinci su nike da hannuwansu, kafin su sarrafa zuwa da abin da suke son sarrafawa. Su ma waƙoƙin na nika sun fara ɓacewa kamar yadda waƙoƙin daɓe suka ɓace, amma su ba suɗauke da batsa, sai dai an yi saurin watsi da su ne don samun ci gaba na zamani na yin niƙa da injin. Misalin wannan waƙa shi ne:

Hure yar yar yar,
Hure baƙin Carki,
Hure bana goron benaye,
Ko da maso wasa,
ɗiya ta so aure,
Uwa ba ta shirya ba,
Uba bai shirya ba,
Ku ba ta aron taskira,
Ku ba ta aron lehe,
ku ba ta aron Saurayin da bai taba lalle ba.
(*Taskar Adabin Mata*, 2018)[3]

### 2.**3.1.3 Waƙoƙin da ake yi a Filin Yaƙi**

Waƙoƙin da makaɗa ke rerawa a filin daaga su ake kira waƙoƙin yaƙi. Mawaƙan kan bi jaruman yaƙi suna yi musu kirari irin na bajinta, suna kuma rera musu waƙa koda a taskiyar daji ne. Bayan an dawo gida daga

[3] Hadiza, S. da wasu (2018) *Taskar Adabin Mata*, Annour Multi-Media Limited

wajen yaƙin, mawaƙan kan shirya waƙa suna sassaƙa abinda idonsu ya gani a wajen yaƙin domin sun zama ganau ba jiyau ba. Irin waɗannan mawaƙan ana ba su wata alama su rataya ga wuyansu ko su saka ga jikinsu domin tantancewa da su, gudun kar a kai musu farmaki da tunanin cewa su abokan gaba  ne, wato ‘yantattu ne,ba a kama su[4]. Da waɗannan Makaɗan ake yawon kai farmaki tsakanin mayaƙa. Daga cikin misalan makaɗan yaƙi akwai:
Akwai Makaɗa Ango Mai Zari na Gobir. Makaɗin Sarkin Gobir Ummaru Shawai ne (1916-1945) ga misalin waƙar da Makaɗa Ango ya yi wa ubangidansa:

> Mijin Maduga,
> Koda ganin mijimmu an san shi,
> Kokawa da kai,
> Ba riba takai ba,
> Kwaj ja mai gidanga ya faɗi[5].

**Auna Fahimta**

| | |
|---|---|
| 1. | Su waye suke waƙoƙin dandali |
| 2. | Jero sunayen waƙoƙin da mata suke a cikin gida guda uku |

**Kammalawa**

Waƙar baka ita ce farko da Hausawa suka fara sabawa da ita kafin kowane rukunin Adabin baka na Hausa. Kusan a kowane al’amari na Bahaushe sai ya sa waƙa a cikinsa. Akwai waƙar da Bahaushe kan yi lokacin farauta. Da lokacin noma, da lokacin hutawa da lokuttan reno da a cikin kowane irin al’amari har ma lokuttan zaman makoki idan an yi masa mutuwa. A Wannan kaso an ga misalan hakan.

## 2.4 Taƙaitawa

- An ga waƙoƙin gaɗa, waɗanda ‘yammata da manyan mata ke shiryawa a dandali da wurin taruruka na taya murna
- Ana iya bambanta waƙoƙin da ake aiwatarwa na dandali da na filin yaƙi?
- A kowane al’amari na rayuwar Bahaushe, zaka tarar an yi masa waƙa

[4] Gusau, S. (2005) *Maka]a da Mawa}an Hausa*, Bench Mark Publishers, Shafi na 2
[5] Gusau, S. (2005) kamar ]uren da ke sama shafi na 2

## 2.5 Manazarta

Dembo, U (1972) *Wasannin Yara*. Northern Nigerian Publishing Company, Zaria. Shafi na i.

Gusau, S. M. (2005) *Makaɗa da Mawaƙan Hausa*, Bench Mark Publishers, Shafi na 2

Gusau, S. M (2013) Wasanni Don Yara. Century Research and Publishing Company, Kano. Shafi na 60.

Hadiza, S. da wasu (2018) *Taskar Adabin Mata*, Annour Multi-Media Limited

Hira da Hajiya Nasara Bello Dodondaji, a gidanta da ke Bado Ƙuarters, ranar 16/2/2020,Ƙarfe 3:15 na rana.

## 2.6 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Yammata ne suke waƙoƙin dandali ma fi akasari da daddare.

a) Waƙoƙin daka
b) Waƙoƙin niƙa
c) Waƙoƙin tawai

## KASHI NA UKU KASHE- KASHEN WAƘOƘIN BAKA I

3.1 Gabatarwa
3.2 Manufar Darasi
3.3 ƙunshiyar
 3.3.1 Waƙoƙin Da ake yi a wasu keɓaɓɓunLokuta
 3.3.2 Waƙoƙin da ake rerawa lokacin bukuwan Al'ada
 3.3.3 Waƙoƙin da ake rerawa lokacin bauta
 3.3.4 Waƙoƙin da ake rerawa lokuttan NishaɗI ko Baƙin Ciki
3.4 Taƙaitawa
3.5 Jingar Aiki
3.6 Manazarta
3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



### 3.1 Gabatarwa

AƘarƙashin wannan kason za a ga gabatar da kashe-kashen waƙoƙin baka da suka danganci mutanen da ke gabatar da su, da kuma lokuttan da ake yinsu, tare da misalai. Kasancewar waƙoƙin baka rukuni ne mai faɗin gaske, ba zai yiwu a tattauna rabe-rabensu a cikin darasiɗaya ba, wannan darasin ci gaban wanda ya gabata ne. Amma an zaɓi a kalli wani ɓangare na daban da wanda ya gabata, inda a can gaba za a sake gabatar da ci gabansu a wani darasi na daban.



### 3.2 Manufa

Daga cikin manufar wannan bincike shi ne a gabatar da:

- Ci gaba da nazarin kashe-kashen waƙoƙin baka
- Sanin irin lokutta daban-daban da ake aiwatar da waƙoƙin baka da sauransu.



### 3.3 ƙunshiya

#### 3.3.1 Waƙoƙin da ake yi a wasu keɓɓun lokuta

Bayan waƙoƙin da ake yi na baka da suka danganci al'umma, akwai waɗanda ake gabatarwa da suka danganci lokutta daban-daban na farin

ciki da na baƙin ciki. Waƙoƙin da ake samarwaƘarƙashin wannan rukuni sun daɗe da samuwa. Kuma sun fara shuɗewa saboda zamanin nan da ya zo da wasu baƙin al'adu, Hausawa suka rungumi al'adun suka fara sauya nasu da na wasu baƙin saboda dalilai daban-daban. Bayanan da ke biye za su yiƘarin haske kan hakan.

### 3.3.2 Waƙoƙin da ake Rerewa Lokacin Bukukuwan Al'ada

Bukin buɗin daji, yana daga cikin bukukuwan al'ada inda mafarauta da matsafa da 'yan bori naƘasar Hausa kan nemi dabba mai suna *Sayaki* su yanka ta su fassara kayan cikinta da yanayin shekara mai zuwa. Waɗannan rukunin jama'a masu jagorantar wannan bikin suna samun rakiyar mawaƙa da makaɗa a cikin jeji. Misalin waƙoƙin waƙoƙin da ake gudanarwa a wannan bukin su ne:

> "Gwauro mai hankalin Sayakin daji,
> Sai na taho in ga mai hikimar banza,
> Ga Mu'azu gwauron zaki"[6]

### 3.3.3 Waƙoƙin da ake Rerawa Lokuttan Bauta

Kundaye da dama sun ruwaito irin kalamai cikin sigar waƙa da mutanen kano ke yi a kowace shekara idansun taru a bakin dutsin Dala domin gudanar da nau'in bautarsu. Ga misali:

Ga tsunburburar Kanawa,
Ga magajin Dala,
Mai gida saman dutsi,
Da kunƘi da kun so,
Ku bi ni ba ra'i ba[7].

### 3.3.4 Waƙoƙin da ake Rerawa a Lokuttan Nishaɗi / Baƙin Ciki

Waɗannan waƙoƙin sunƘunshi na bukukuwa (bukin suna, ko aure, ko mutuwa, ko shayi/kaciya). Waɗannan suna daga cikin waƙoƙin da ake rerawa a wajen wanzar da al'amurran da sukwa shafi matakan rayuwar Bahaushe.

Lokacin mutuwa ana jin masu zaman makoki suna faɗin*ashe wane bai jimre ba, ashe wane ya tafi kenan, lallai wane ya tafi kenan*.

Lokacin tarewar Amarya masu yi mata rakkiya suna faɗin:

---

6. Umar, G. (2012) *Bukukuwan Hausawa* Ol-Faiyh Print Gusau, shafi na 29
7 Ibrahim, M.S. (1982) "Dangantakar Al'ada da Addinin: Tasirin Addinin Musulunci Kan Al'adun Hausawa na Gargajiya", Kundin Digiri na Biyu, Kano: Jami'ar Bayero

Jagora: Ayye mama, ayye mama,
‘Yan Amshi: Mama ye wa iye,
Jagora: Ayye mama labo-labo,
‘Yan Amshi: mama ye wa iye,
Jagora: Da aure yana raka aure,
‘Yan Amshi: Mama ye wa iye,
Jagora: Da na biki mun tafi tare,
‘Yan Amshi: mama ye wa iye

Lokacin bukin suna waɗanda suka je taya mai jego murna suna rera waƙoƙi kamar haka:

> Mata ciki da Goyo Ikon Allah,
> Wance da ta yaye sai kumaɗauka,
> In an gama kuma sai labari[8]

**Auna Fahimta**

| | |
|---|---|
| **1.** | Daga cikin waƙoƙin da ake gudanarwa don nishaxi akwai…... da …… |
| **2.** | Kawo bukuwan al’ada guda biyu da ake gudanar da waƙoƙin baka |

## 3.4 Taƙaitawa

- Ko bayan rukunnan jama’a, akwai wasu waƙoƙI da sukakeɓanta ga wasu lokuta na musamman ko faruwar wasu al’amura kamar mutuwa, ko bauta ta gargajiya ko rashin ruwan sama da rashin abinci, duk sai lokacinsu ya kama akejinsu a bakin al’ummun ko mawaƙa

**Kammalawa**

Bayanan da suka gabata sun bayyana irin waƙoƙin da maza ke aiwatarwa tare da bayyana sunayen wasu daga cikin makaɗa maza. Haka ma an bayyana su ma mata da irin nasu waƙoƙin. mun ga cewa waƙoƙi aƘasar Hausa suna da lokuttan da ake aiwatar da su bisa ga tsarin da al’ada ta tanada.

---

[8]. Irin wannan ]an wa}a ana tsintarsa a cikin wa}o}i da Hajiya Barmani Choge ke rerawa a lokacin da da ke nisha]antar da jama’a.

## 3.6 Manazarta

Bunza, A. (2009) *Narambaɗa*, Ibrash Islamic Publication Centre.

Gusau, S. M(2002) *Sarkin Taushi Salihu Jankiɗi*, Baraka Publishers

Gusau, S. M(2005) kamarɗure na sama. Gusau, S. (2016), *Makaɗa da Mawaƙan Hausa*, Century Research and Publishing, Limited Kano

Gusau, S. M (2009)*Diwanin Waƙoƙin Baka* Zaɓaɓɓun Matanoni na Waƙoƙin Baka na Hausa, Century Publishers, Limited.

Gusau, S. (2018) *Diwanin Waƙoƙin Baka* **Juzu'i na Uku**, Matanonin Wasu Waƙoƙin Alh. Dr. Mamman Shata Katsina, Century Publishers, Kano.

Ibrahim, M.S. (1982) "Dangantakar Al'ada da Addinin: Tasirin Addinin Musulunci Kan Al'adun Hausawa na Gargajiya", Kundin Digiri na Biyu, Kano: Jami'ar Bayero.

Umar, G. (2012) *Bukukuwan Hausawa* Ol-Faiyh Print Gusau, shafi na 29

## 3.1 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Waƙoƙin bikin aure da na suna
a) Bikin Buxar Dawa Waƙoƙin Bauta

## KASHI NA HUƊU KASHE-KASHEN WAƘOƘIN BAKA II

**Abubuwan da Suke Ciki**

4.1 Gabatrawa
4.2 Manufar Darasi
4.3 ƙunshiyar
 4.3.1 Waƙoƙin Wasu Rukunin Jama’a
 4.3.1.1 WaƙoƙnWasu masu Sana’o’i
 4.3.1.2 Waƙoƙin Wasu Mata
 4.3.1.3 Waƙoƙin ‘yammata
 4.3.1.4 Waƙoƙin Wasu Mata (Karuwai)
 4.3.1.5 Waƙoƙin ‘Yammata
 4.3.1.6 Waƙoƙin Yara (Mata da Maza
 4.3.2 Waƙoƙin Garuruwa
 4.3.3 Waƙoƙin Wasu Gidajen Watsa Labarai
4.4 Taƙaitawa
4.5 Jingar Aiki
4.6 Manazarta
4.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



### 4.1 Gabatarwa

Al’ummar Hausawa suna da rukunna mutane mabambanta da suka haɗa da Sarakai masu mulki, akwai attajirai, akwai kuma talakawa. Cikin waɗannan rukunnan da aka ambata a sama, akwai maza akwai mata, akwai yara, akwai matasa, kuma dukkanin rukunnan ana yi musu waƙa, wasu Waƙoƙin ma kan wasu halittu ne aka tsara su, halittun nan sunƘunshi abubuwan da ba mutane ba. Akwai dabbobi da tsuntsaye daƘwari akwai aljannu. Za a tattauna kan waƙoƙin da ake samu kan waɗannan rukunna mabambanta.



### 4.2 Manufa

AƘarƙashin wannan darasi za gabatarwaɗalibai muhimman abubuwan da sukaƘunshi:

- Sanin cewa makaɗan Hausa suna da rukunna daban-daban
- Akwai makaɗan da suka keɓanta ga wasu rukunin jama’a, irin makaɗan sarauta.
- Akwai waɗanda suke yi wa kowa waƙa, mai kudΙ da talaka

- Akwai waɗanda wasu abubuwa suka sa gaba don waƙewa, ba don neman la'ada ba, waɗanda su ne makaɗan sha'awa

## 4.3 Ƙunshiyar Darasi

**Waƙoƙin Wasu Rukunin Jama'a**

A wannan darasi za a ci gaba a inda aka tsaya a darasin da ya gabata mai bayani kan nau'o'in waƙoƙin baka kashi na biyu, inda aka gabatar wasu waƙoƙin baka. Wannan darasi zaiɗora tare da bayanin nau'o'in waƙoƙin da ake yiwa mutane daban-daban da wasu halittu da ke rayuwa a cikin muhallin Bahaushe.

### 4.3.1 Waƙoƙin Rukunin Jama'a

Waƙoƙin da ke cikin wannan rukuni sun shafi mutune ne kurum. Mutanen nan sun haɗa da shugabanni da sarakuna da attajirai da talakawansu da masu sana'o'i daban-daban. Za a ga misalan waƙoƙin wasu daga cikin waɗannan jama'akamar haka:

#### 4.3.1.1 Sarakuna da Manyan Mutane (maza)

Manyan sarakunanƘasar Hausa suna da nau'in mawaƙa iri biyu: Mawaƙan da suke yi wa gidajen sarautu waƙoƙi. Waƙoƙinsu kan gidan sarautar ne, ba sarki mai ci ba. Sai mawaƙan da ke yi wa Basarake mai ci. Misali Makaɗa **Salihu Jankiɗi Rawayya**, ya samu sarautarsa ta Sarkin Taushin Sarkin Musulmi a dalilin kiɗan da yake yi wa masarautar gidan Sarkin musulmi da ke Sakkwato. Kafin Salihu Jankiɗi, Makaɗa **Muhammadu Dodo Maitaushi** mutuminƘasar Bakura, shi ne riƙe da Sarautar Sarkin Taushin Sarkin Musulmin Sakkwato. Makaɗa **Audu Inka Bakura**, sananne a fagen waƙa amma makaɗin gidan sarautar Sarkin ɓurmin Bakura ne. Sarkin Kotson Kano, Sarauta ce da aka bai wa Makaɗa **AbdurRahman**
**Uban Inuwa ɗan-korau** saboda yana yi wa marautar Kano waƙa.

Makaɗan manyan mutane sun haɗa da **Shata** uban mawaƙa, akwai waƙar Sarkin Kano Ado Bayero (*Sarkin Ado ɗan Bayero*); da waƙar Sarkin Musawa Usman Liman (*Sadauki Shehu Magajin Mamman*). Makaɗa **Aliyu ɗandawo** shi ma fitaccen mawaƙi ne, daga cikin Sarakunan da ya yi wa waƙa akwai Sarkin Yawuri (*Mai Yawuri Bangon Duniya*), akwai waƙar Sarkin kabin Argungu Muhammadu Sama (*Babban Bajini Muhammadu Sama, Sarkin Kabi ba a gardama da kai, akwai waƙar Sarkin Das Bilyaminu*). Tarihin makaɗan baka aƘasar Hausa ba zai cika ba, sai an haɗa da ambaton Makaɗa **Ibrahim**

**Narambaɗa**. Daga cikin waƙoƙinsa na Sarakuna akwai wadda ya yi wa Sarkin Gobir na Isa Amadu (*Gwarzon Shamaki na Malam Toron Giwa*).

Waƙoƙin sarauta na musamman ne, domin kuwa ana samun kowane gidan sarauta yana da makaɗan da ke yi masa waƙa. Haka zalika ana samun makaɗan da suka shafi keɓantattun sarakuna, ma'ana tun da sarauta lokaci gareta, kowane sarki yana da nashi makaɗi. Makaɗan sarauta ba su yi wa kowa waƙa sai ubannin gidajensu. Dukkanin lalurorinsu ta fuskar abinci da sutura da kuɗaɗen kashewa sun rataya ga waɗanda suke yi wa waƙa, shi ya sanya ba su da damar yi wa wani waƙa sai da izinin uban gidansu.

Bayan manyan Sarakuna akwai manyan mutanen da ke shan kiɗa a hannun mawaƙa daban-daban a matsayin yabo don mai kuɗin ya kyautata musu. Waɗannan waƙoƙin su suka fi yawa a cikin al'umma, domin kuwa kasancewar mawaƙi tamkar maroƙi, yakan yi amfani da hikimarsa wajen gwarzanta wanda yake so don ya karɓi abin hannunsa. Daga cikin waɗannan mawaƙan akwai waɗanda suka manyan mawaƙa ne, suna zaune gidajensu za su yi wa wanda suka yi muradi waƙa, ya aika musu da abin sallama, kamar Alhaji Garba A.D na Kano (*Alhaji Garba A.D na Kano mai kayan leshi*) wannan waƙar Makaɗa Alhaji Musa ɗanƙwairo Maradun ya yi masa ita. akwai waƙar Haji Garban Bichi ɗan Shehu, wadda Makaɗa Alhaji Mamman Shata Katsina yaw aƙe attajirin da sauransu. Akwai kuma waɗanda sukeƘanana da sukeɗaukar abin kiɗa suna zagayawa gidajen masu wadata suna buga ganga don a sallame su. Waɗannan makaɗan sune suka fi yawa a cikin al'umma.

### 4.3.1.2 Waƙoƙin Wasu Masu Sana'o'i

Bayan waƙoƙin da aka gabatar a baya, mun sani cewa sana'o'in gargajiya suna matuƙar muhimmanci aƘasar Hausa. Wannan ya sanya har sarautu ake naɗawa a cikin kowace sana'a. waɗannan sana'o'in irin farauta suna da mawaƙa waɗanda idan har za a je farauta tare da su ake zuwa, suna waƙe gwarzayensu. Sana'o'i irin noma daƘira da su da sauran fitattun sana'o'inƘasar Hausa duk suna da makaɗa.

Daga cikin misalan waɗannan mawaƙan akwai Alhaji **ɗanmaraya Jos** (*Teacher Uban Karatu, Waƙar ɗan'amalanke da waƙar Lebura*), **Barmani Choge** (*mu kama sana'a mata*), **Mamman Amale** (*mu yi noma, ku yi noma bana gero za mu ci, dawa za muci, masara za mu ci,* akwai waƙar*Gora uwar tuwo ta Sa'idu buƙatarki ta biya*), **Audu Inka Bakura** (*Makaranta uwarƘwarai ta kuma mai riƙonƘwarai* Akwai waƙar **Shata** ta Ibrahim Custom (*mai daga magajin mamman, Sani Audi mai ban tsoro*).

### 4.3.1.3 Mata (Sarakai, Attajirai)

Mata ma kamar maza ana samun mawaƙan da ke waƙe su don su bayar da abin hannunsu. Akwai mawaƙan da suke mawaƙan mata kaɗai ne, ba su yi wa kowa waƙa in ba mata ba. Akwai kuma waɗanda mawaƙan jama'a ne suna dubin cancantar wanda za su yi wa waƙa. daga cikin waɗannan sun haɗa da Hajiya **Barmani** Choge ta waƙe Hajiya Maryam Abacha (*Matar ShugabanƘasa mai daraja Hajiya Maryam Abacha*) Alhaji Haruna **Uje** ya waƙe Jimmai (*Jimmai 'yar makaranta, da Balarabata Balarabe*, *Sannu Balaraba sai ke dawo*) Makaɗa **Sa'idu Faru** ya waƙe mahaifiyar Sarkin Kano Maibabban ɗaki. **Shata** ya waƙe (*Maiɗakin Gabas 'yar Iro*) Makaɗa Isah **ɗanmakaho** ya waƙe Hajiya Amina (*mai maganin gargajiya ta Nijar*)Makaɗa Musa **ɗanƙwairo** ya waƙe *Umma magajiyar Murya dagaƘauyen kance.***Maidaji** Sabon Birni ya waƙe Saratun mata na Inna[9] a yankin Gobir da Argungu (*waƙar Inna 'Yar Buƙuma*).

### 4.3.1.4 Mata Karuwai

Mata masu zaman kansu aƘasar Hausa, suna mu'amala da maza masu kuɗi suna yi musu lalurori, inda suke tsoma goma su wanke biyar ba tare da wata takura ba. Dama maroƙi ya fi son duk inda masƙi yake, ya yi waƙa a salla me shi, shi yasa ake samun mawaƙan da ke yi wa karuwai waƙa, su kuma suna kyautata musu. Bayan waɗannan mawaƙan akwai wasu da suke faɗakarwa a cikin al'umma da suka yi wa karuwanci waƙa tare da fito da illarsa kamar Waƙar Alhaji **Sani ɗanbalɗo** (*Zaura'yan inna da baba*, *Gobarar Nera 'yar cin amana*), Waƙar **Shehu Ajilo** (*mun jiyo labarin ta zubas*). **Ali Makaho** ya soki wata karuwa da ta zage shi, inda yake cewa:

Gyara Allah buwayi,
Chali wata Karuwa ta taɓa ni,
Sunanta ba zan faɗi ba,
Ita ma ta gane kanta,
Ta ce ita ba ta son maroƙi,
Ni dai na san gatanɗan bariki sai maroƙi,
Gatan Karuwa ma maroƙi.

### 4.3.1.5 Yammata

Waƙoƙin soyayya da makaɗa ke yin a soyayya suna da yawa, domin nuna irinƘaunarsu ga waɗanda suke waƙewa. A cikin waƙoƙin nasu suna yawan gwarzanta masoyan nasu, tare da surantasu da kyakkyawar sura ta fuskar kyawun halitta da halayya da sauransu. Daga cikin

[9]. Sa'idu, A. (2012) "Nazarin Ayyukan Maka]a Maidaji Sabon Birni 1938-2000" Kundin Digiri na Biyu, Zaria: Jami'ar Ahmadu Bello, shafi na 306

waɗanda suka yi waɗannan waƙoƙin akwai Makaɗa Muhammadu **ɗankurji** ya waƙe wata budurwa Lantana (*Lantana jikanyar Buhari aljannar makaɗa*)

#### 4.3.1.6 Yara (maza da mata)

Ilimi shi ne gishirin rayuwa, babu al'ummar da ba ta darajanta ilimi da kwaɗaitar da nemansa, kowanne na addini da na boko. ɗaliban ilimi ma akwai mawaƙan da suka waƙe su, da nuna irin muhimmancin ilimi a cikin al'umma kamar Alhaji **ɗanmaraya** Jos ya waƙe yara 'yan makaranta (*yara manyan gobe, Yara Allah na nan*), Makaɗa **Audu Inka** Bakura ya yi yara 'yammakaranta waƙa (*makaranta uwarƘwarai ta kuma mai riƙonƘwarai ta riƙeɗ***anta** *ta yi mai sutura ya hito*….) Makaɗa **Uwani** Zakirai ta waƙeɗalibi Azizu (*Azizuɗan makaranta, na tuna da ran ban kwananmu…)*

### 4.3.2 Waƙoƙin Garuruwa

An samu mawaƙan da suka waƙe garuruwa daban-daban, tare da fito daɗaɗɗen tarihin garuruwan ko albarkatunƘasarsu ko yanayin zamantakewarsu ko shaharasu ko wane keɓantaccen al'amari day a shafi garin. Makaɗa **Shata** ya waƙe Birnin Kano (*Kano ta Dabo Madinar Shata, da waƙar Shata ta Shata baƙon Amerika*), Alhaji Garba **Supa** ya waƙe Kano (*Jihar Kano Birnin Dabo*), Makaɗa Amadu **Inka** Bakura ya waƙe garin Sakkwato (*Sakkwato Birnin Shehu da Bello, ya tsare Gaskiya bajinin gidan Hassan, jikan Shehu Sarkin Musulmi*) Makaɗa **ɗanlami** Nasarawa ya waƙe garin Abuja (*Birnin tarayya, birnin tarayya, Abuja, malam maitafiya, tsaya ka ji labarin Abuja*) Alhaji **Sani Sabulu** Na Kanoma, ya waƙe garinsu na Kanoma (*da Kano da Kaduna da kewaye duka Kanoma ag gabansu, amma wurina*) Makaɗa **Miko Shatan Nasarawa** (*Ga ni jihar Jigawa ina kiɗi*).

#### 4.3.2.1 Waƙoƙin Gidajen Watsa Labarai

Manyan gidajen rediyo daƘanana, na jaha da na tarayya da naƘasashen waje suna da mawaƙan da suka waƙe su, su gwarzanta su, tare da nuna fifikonsu akan sauran. Waɗannan waƙoƙin sanannu ne ga masu sauraren gidajen rediyon, domin kuwa za su riƙa saka waƙoƙin akai-akai a lokuttan da suke gabatar da shiraruwansu. Daga cikin waɗannan gidajen rediyon akwai:

VOA, BBC, Dutceɓelle, FRCN, Gidajen Rediyona jihohi, FM Stations:

i. VOA
ii. BBC
iii. Dutceɓelle

iv. FRCN (Rediyo Tarayya na Kaduna), Makaɗa Alhaji Shehu Ajilo ya waƙe wannan gidan Rediyo kamar haka:

**Jagora:** A gaisheku Rediyo tarayya farin gida kafin Sardauna.
**'Yan Amshi:** A gaisheku Rediyo tarayya farin gida kafin Sardauna.
**Jagora:** in ana filin wasaƘwaƙwalwa, da filin kacici-kacici, muma sai mu wasaƘwaƙwalwa
**'Yan Amshi:** A gaisheku Rediyo tarayya farin gida kafin Sardauna
**(**Waƙar Alhaji Shehu Ajilo)
v. FRCN (Talabijin) Alhaji Tunau daga tawagar Sarkin Taushin Katsina ya rera wa gidan Talabijin na tarayya Kaduna waƙa kamar haka:

**Jagora:** Za mu bikin Talabijin, nuna hwarin cikimmu ne gabaɗaya,

**'Yan Amshi:** Za mu bikin Talabijin, nuna hwarin cikimmu ne gabaɗaya,

**Jagora:** Yau shekararta goma, gwamnatimmu tay abubuwa da dama,

'Yan Amshi: Za mu bikin Talabijin, nuna hwarin cikimmu ne gabaɗaya,

**Jagora:** kai jama'a zamanin siyasa, kun ga irin abubuwan da tay yi,
Ta yi duk abinda duk akaiƘasannan, zaƙulo mana hakkimmu tayyi
'Yan Amshi: Za mu bikin Talabijin, nuna hwarin cikimmu ne gabaɗaya,

**Jagora:** Da sojoji sunka karɓi mulki, sun kama aiki gadan-gadan don su yi hani ga yaɗa Ƙarya. (Tunau na Sarkin Taushin Katsina)[10]

Alhaji Aminu Alan Waƙa ya waƙe gidan rediyo na BBC kamar Haka:
BBC Hausa Hantsi leƙa gidan Al'umma kun jiya,

[10]. Maka]a Gilashi Azare ya yi wa Rediyo Talabijin na tarayya kaduna wa}a lokacin da suka cika shekara goma da kafuwa, Malam A}ilu Aliyu ya shirya rubutacciyar wa}a a lokacin cikar bukin Talabijin da ta cika shekara goma kyawawa.

# KASHI NA BIYAR WAƘOƘIN WASU HALITTU DA YANAYI WAƊANDA BA MUTANE BA

**Abubuwan da Suke Ciki**

5.1 Gabatarwa
5.2 Manufar Darasi
5.3 ƙunshiyar
 5.3.1 Waƙoƙin sanyi da damana, da kakar abinci
 5.3.2 Waƙoƙin wasu Halittu da ba mutane ba
  5.3.1.1Waƙoƙin Aljannu
  5.3.1.2Waƙoƙin Mala'iku
5.4 Taƙaitawa
5.5 Jingar Aiki
5.6 Manazarta
5.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

## 5.1 Gabatarwa

A wannan kason za a ga samfurin waƙoƙin da makaɗa ke yi wa wasu halittu da ba mutane ba. Daliin nazarin irin waɗannan waƙoƙin shi ne, domin mu tabbatar da maganar da ta gabata na sha'war mawaƙan baka na Hausa taɗaukar abinda suke so su yi waƙe shi. Wasu daga cikin mawaƙan kan tsaya ga fada, ko manyan mutane kamar yadda bayannan da suka gabata suka bayyana. Wasu kuma na kowa ne wajen bayyana azancinsu. Bayannan da ke biye waƙoƙi ne waɗand aba na mutane ba kamar yadda aka saba gani, ba kuma na gargaɗi da faɗakarwa ba ne, na wasu halitu ne waɗanda ke zagaye da mutane, kuma mutanen suna tarayya da su.

## 5.2 Manufar Darasi

Manufar wannan darasi shi neɗalibai su san kasha-kashen waƙoƙin baka da mawaƙan baka da abubuwan da suke yi ma waƙa waɗanda ba mutane kaɗai ba.

## 5.3 ƙunshiya

### 5.3.1 Waƙoƙin Sanyi da Damana da Kakar Abinci, Fari (rashin abinci)

AƘasar Hausa akwai yanayi biyu, watau lokacin damana da lokacin rani. Damana takanɗauki tsawon lokaci na wata huɗu zuwa biyar, ya danganci ɓangaorinƘasar.a lokacin na damana ake samun ruwa a shuka abinci a yalwata. Idan damanar nan ba ta yi kyau ba, ba za a samu abincin da ake buƙata ba, ko kuma idan aka samu fari, wanda wasu dalilai ke haddasa wannan farin. Makaɗa Bage **ɗansala** ya yi waƙa kan farin da aka shiga da mawuyacin halin da al'umma suka shiga a cikin waƙarsa ta *garin kwaki* inda yake cewa, (*A ci dai ba don aƘoshi ba, garin kwaki ya yi taimaka*). Amma idan damana ta sauka da kyau sai a samu kaka mai kyau. Makaɗa Idi **ɗangiwa** Zuru ya waƙe damanar da ta yi ruwa inda yake cewa (*Abokan aiki ruwa a gaisheku da taimako*). Bayan su akwai wasu mawaƙa da suka waƙe abinci da noma kamar, Maidaji Sabon Birni ya waƙe gonar Maman Nata'Ala (*Gonar Alhaji AliƘare kallonka ta 'yan kuzo, wagga gona Allah yay yi miki gayyar Albarka ta 'yan kuzo*). **ɗanƙwairo** a waƙar Dam na Bakalori (*ya hi gaban a yi mai wargi, a yi hanzari nai*)

Lokacin rani ya fi na damana yawa aƘasar Hausa, domin ya Ƙunshi yanayi uk da suka haɗa da yanayin kaka da yanayin hunturu da yanayin bazara. Lokacin kaka lokaci ne da manoma suka girbe amfanin gona, bayanɗaukewar ruwan sama. Idan tafiya taɗan miƙa sai hunturu ya fara shigowa a hankali har ya yi tsanani, daga nan sai kuma sanyin ya yi bankwana, zafi ya fara kunno kai. Idan zafi ya shigo, shi ma zai fara a hankali har sai ya yi tsanani, sa'annan damana za ta kunno kai. Shi ma wannan yanayi an samu mawaƙan da suka waƙe shi kamar **ɗanmaraya** a waƙar ɗan'adam (*in an yi zafi, ya ce an yi zahi, in an yi sanyi ya ce an yi sanyi, in an yi ruwa ya ce an yi ruwa, in anƘi ruwa ya ce anƘi ruwa*……).

### 5.3.2 Waƙoƙin Sauran Halittu (Masu rai da Marasa rai) Waɗanda ba Mutane

Sauran halittun da ake mu'amala da su masu rai da marasa rai, suna da yawa a da ake ambatowa a cikin waƙoƙinsu, wasu lokuta ma sunaɗaukar abu sukutum su waƙe shi, don fito da surarshi da amfaninshi da bayyana rayuwarsa da dangantakarsa da al'umma. Misalin waɗannan su ne a cikin Waƙar **Shata** ta Apollo (*Kumbo Apollo 11, Shata waƙar ya maida Kada, ya dawo*) inda yake cewa:

**Jagora**: ƙumbo apolo ilabin
Y/Amshi: ƙumbo apolo ilabin

**Jagora**: Amurka sun wani Kumbo
Sunanshi Apolo ilabin
**Y/Amshi**: ƙumbo apolo ilabin

**Jagora**: Sun haɗa shi sun shirya shi
Amurka sun harba shi
Ya tafi har gurin wata
**Y/Amshi**: ƙumbo apolo ilabin

**Jagora**: Kuma ya je da lafiya
Ya komo da lafiya
**Y/Amshi**: ƙumbo apolo ilabin

**Jagora**: Cikon biyun suka shirya

Sai suka sa kare a ciki
Ya tafi har garin wata
Ya je ya sauka lafiya
Ya komo da lafiya

**Y/Amshi:** ƙumbo apolo ilabin[11]

Hakama a cikin abubuwa masu rai, irin nau'o'in dabbobi da tsuntsayeƘwari da tsirrai an yi waƙe-waƙe da dama da suka haɗa da Waƙar Makaɗa Babangida **Kakadawa** (*ina bakin kogi kada na dubina, yana ta hararena*), Waƙoƙin Alhaji **Garba Maitandu** Shinkafi (*Sarkin Tuttular Kaya, Kunama nika wa kiɗa)*, misalign wannan waƙar shi ne:

**Amshi**: Kunama zan wa kiɗi
Zama ciwo ag gareta
Ta halban na jiya (maimatawa x2)

**Jagora**: Ikon Allah mutane (maimaitawa x 2)
'Yar abu 'yar tsito
Gara halbin jaki bakwai
Da takinta cikin kure

**Amshi**: Kunama zan wa kiɗi
Zama ciwo ag gareta
Ta halban na jiya (maimatawa x2)

---

[11] Gusau, S. M (2018) Diwanin Wa}o}in Baka Juz'i na Uku. Century Research and Publishing Limited. Kano . Shafi na 453.

**Jagora**: Na ga gidan ta kulɓa

Amma jiya na ji Sakkwatawa sun ce,
Gaton ruhewa nan take
Kanawa sun ce haba!
A gindin dutse take
Su ko ‘yan Hausa sun ka ce
Ga ciyawa take
Buzu ya ce gali
Ga gindin rogo take
ɗiyan yarbawa suna faɗin mololi
Haba ga gindin kwakwa take
Hillani na faɗin cikinɗan rame take
Maraɗawa na faɗin haba bas u gane ba
Duk ga tankanɗaki take
Buzu ya ce bari-tani-baka tamba
Ko’ina daiɗakinta ne
Turawa na faɗin sukopiyo ‘yar baya ce
Su ko ‘yan Borno sun ka ce
Ijiwa ye……………….[12]

### 5.3.2.1 Waƙoƙin Aljannu

Irin imanin da Bahaushe yake da shi dangane da iskoki da mu’amalarsa das u maiƘarfi, ya sanya iskoki suka taka muhimmiyar rayuwa a cikin ɓangare na rayuwarsa. A cikin adabin Bahaushe babu inda babu nason iskoki, musamman ma waƙoƙinsa na baka waɗanda keɗauke dad aɗaɗɗiyar fasaharsa da rayuwarsa da zamantakewarsa da duk wani abu da ya shafi al’amarin rayuwarsa. Ana iya cin karo da tasirin iskoki a cikin waƙoƙin baka daban-daban a matsayin ambato a cikin waƙa ko kuma aɗauko aljaniɗungurungum a waƙe kamar yadda ake samu a cikin waƙoƙin bori da sauransu.

Kiɗan gurmin Bori, Waƙar **Uwani** Zakirai (Waƙar Aljani Badakwa, da waƙar Aljani Barhaza, da Waƙar Aljana Inna)[13], Mamman **Amale Sububu** ya waƙe wasu Aljannu a cikin waƙoƙinsa na noma (*ya riƙa noma da Gaskiya na bakwai bai saba ba da zama, tabi’ar Aikau baƙa guda, ya kiraka ya nuna ga Aljana, in kaƘi ta shanye maka jini*) Sa’adu Bori (*Dango maye, babbaɗan babba, maye, mai gida yamma gajere, maye, kakka taɓa Dango shi kasheka*).

[12] Bunza, A. M (1999) Ra]a]i da Zogin Cuta a Ma’aunin Bahaushe (Tsokaci kan Wa}ar Kunama ta Garba mai Tandu). Ma}alar da aka gabatar a Jami’ar Usumanu [anfodiyo, Sakkwato. Shafi na 5.
[13]. Faya-fayan Garmahon wa}o}inta da aka samo gidan rediyo na FRCN

Idan muka waiwayi waƙar amale sububu wacce yake yi wa Aikau za mu ga yana cewa:
Na sa anɗauki doguwa ta zamna,
Domin a tara gero
Na sa anɗauki aljana anƘara
Domin a hau da suna
Na sa anɗauki aljana ta kauce
Na bar mutum da kaya
Wani yaɗauko zaƙuma ya tushe
Ta danne zuciyatai
Ni banɗauka ba
Wanda yaɗauka ya kwan ciki

**5.3.2.2 Waƙoƙin Mala'iku**

A cikin waƙoƙin baka na Hausa, can ba a rasa ba sukan ambato mala’iku a cikin waƙoƙinsu. Ambaton ya danganci bagiren waƙa da manufar da ake so a isar. Misali a wajen siifantawa ta yabo ana kwatanta mutum da mala’ika don a nuna kyawun mutum ya wuceƘima, haka ma akan ambato mala’ikun rahama a inda ake maganar rahama da sassabci, a kuma ambato mala’ikun azaba a saɓanin haka kamar a cikin waƙar Shago ta Makaɗa Shago inda yake cewa:

**Auna Fahimta**

| | |
|---|---|
| **1.** | Kawo sunan mawaƙan baka biyu da suka yi wa Aljanu waƙa. |
| **2.** | Wane suna ake kiran makaxan da suke yi wa tsirrai da tsitsaye da saurahalittu da ba mutum ba waƙa? |

**Kammalawa**

Wannan kason ya tattauna a kan waƙoƙin da ake yi wa gidan watsa labarai inda aka kawo misalan mawaƙan da suka yi gidajen rediyo da talabijin daban-daban waƙoƙi. An ga waɗanda suka waƙe yanayi naƘasa da shekara kamar damana da rani da wata da dabbobi kamar Kada da wasu garuruwa. An fahimci kowane mawaƙi da sha’awarsa ko a cikin farfajiyar waƙar.



**5.4 Taƙaitawa**

- An ga wasu waƙoƙI na yanayi kamar sanyi da damana da kakar abinci

- An kuma kawo misalai daga waƙoƙin wasu halittu kamar Taurari irin su Kumbo Apolo, akwai waƙoƙinƘwari kamar su Kunama da Tsuntsaye irinsu Kanari

## 5.5 Jingar Darsi

- Kawo sunayen mawaƙan baka uku, da misalan waƙoƙinsu waɗanda suka yi manyan mutane aƘasar Hausa waƙa.
- Duniya zaman 'yan marina ne, kowa da inda ya mayar da gabansa in ji makaɗa ɗanlami Nasarawa, tattauna wannan hange nasa bisa bayan da suka gabata kan Kason mawaƙa dangane da waƙoƙinsu
- Waƙoƙin baka kundin adana Tarihi ne, kawo manyan abubuwa biyu da aka fahimci waƙoƙin baka



## 5.6 Manazarta


Bunza, A. M (1999) Raɗaɗi da Zogin Cuta a Ma'aunin Bahaushe (Tsokaci kan Waƙar Kunama ta Garba mai Tandu). Maƙalar da aka gabatar a Jami'ar Usumanu ɗanfodiyo, Sakkwato. Shafi na 5.

Gusau, S. M (2018) Diwanin Waƙoƙin Baka Juz'i na Uku. Century Research and Publishing Limited. Kano. Shafi na 453.

Sa'idu, A. (2012) "Nazarin Ayyukan Makaɗa Maidaji Sabon Birni 1938-2000" Kundin Digiri na Biyu, Zaria: Jami'ar Ahmadu Bello, shafi na 306




## 5.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

**1.** Daga cikin mawaƙan baka da suka yi wa aljanu waƙa akwai:
   a) Mamman Amale Dansububu
   b) Sa'adu Bori.

2. Makaxan sha'awa

# KASHI NA SHIDA KASHE-KASHEN WAƘOƘIN BAKA DANGANE DA JIGOGINSU

## Abubuwan da Suke Ciki

6.1 Gabatarwa
6.2 Manufar Darasi
6.3 ƙunshiyar
6.3.1 Kashe-kashen Waƙoƙin Baka Dangane da Jigoginsu
6.3.1.1 Yabo
6.3.1.2 Zambo
6.3.1.3 Zuga
6.3.2 Gargaɗi, Faɗakarwa, Ilmantarwa
6.3.2.1 Gargaɗi
3.2.2.2 Faɗakarwa
6.3.2.3 Ilmantarwa
6.3.2.4 Nishaɗantarwa
6.4 Taƙaitawa
6.5 Jingar Aiki
6.6 Manazarta
6.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



## 6.1 Gabatarwa

A wannan kashi, kamar yadda sauran darussan da suka gabata, za a yi bayanin kashe-kashen waƙoƙin baka ta fuskar misalansu da suka gina jigoginsu (saƙon su kan yaba gwarazansu, ko kushe masu jayayya da masoyansu, ko zuga iyayen gidansu). Kacokam wannan kashi zai yi bayani ne kan jigogon wasu waƙoƙin makaɗa.



## 6.2 Manufa

Manufar wannan darasi kamar sauran darussa, ba zai wuce:

- Gabatar da jigogin waƙoƙin baka
- Sanin jigogin da suka gina wasu wasu waƙoƙin baka
- Bayar da misalan waɗannan jigogin daga cikin waƙoƙin baka

## 6.3 Ƙunshiya

### 6.3.1 Kashe-kashen Waƙoƙin Hausa na Baka Dangane da Jigoginsu

A wannan ɓangaren za mu tattauna kan nau'o'in jigogin da muke da su a cikin waƙoƙin baka, tare da gabatar da misalai da cikin waƙoƙin makaɗan baka da muke da su kamar haka:

#### 6.3.1.1 Yabo

Yabo shi ne kishiyar zambo ne, inda ake amfani da kalmomi a bayyana wani abu game da mutum domin ya ji daɗi, kuma jama'a su ji daɗi game da abinda aka faɗa kansa shi ne manufar yabo. Idan aka faɗi wani abu wanda ya munana sunan mutum, ko aka yi amfani da kalamai marasa daɗi game da shi, to ya zama Zambo. Waƙar Yabo da Kuma Zuga ta Sarkin Kano Aliyu ta makaɗa **Isa Kwargam** misali ce:

**Jagora**: *Ga dodon makangara,*
*Wa bai san na Audu ba,*
*Gwanki ka da mai nawa,*

**'Yan 'amshi**: *Wandara makaye,*
*'Yan maza na tsoron karo da kai*[14]

Waƙar Yabo da Kuma Zuga Sarkin Yawuri Abdullahi ta makaɗa **Aliyu ɗandawo** wani misali ne:

**Jagora**: *Ba a hayemaka sai in ka yarda,*
*Audu ka hi madwacci, dwaci,*
*Ka hi guba in anka zure ma,*
*Ka hi wuta zafiɗan mamman,*

**'Yan 'amshi**: *Wanda Allah,*
*Ya hi bin shanu ayi ikko,*
*Ka hi Gwanja, ka hi Kano Audu,*
*Ko Masar sai dai a yi tono,*
*Ruwan zuma, ba lasar dauɗa, bi da mazaɗan maman,*
*Koma shirin daagaɗan Isah, na yanzu kay yi musu ko ta kwana,*
*Sai dai su bi ba don sun so ba*[15]*,*

---

[14]. Gusau, S. (2016) *Maka]a da Mawa}an Hausa II*, Century Research and Publishing Limited, Kano shafi na 53
[15]. Daga Cikin faifan Wa}ar Sarkin Yawuri Abdullahi wadda maka]a Aliyu [andawo ya yi masa.

### 6.3.1.2 Zambo

Shi ma zambo wani jigo ne daga cikin jigogin waƙoƙin baka da ake sukar wani a fakaice, wanda duk wanda ya ji wannan suka yana iya gane wanda aka yi wa zambon idan har ya san shi, domin kuwa za a siffanta wau halaye ko sura ta wannan da aka yi zambon dominsa, ta yadda za a iya tabbatar da cewa das hi ake. Misalin wannan shi ne:

**Jagora**: *In ka ji ana batutuwan da ba kyawo,*
**'Yan amshi:** ɗan Sarkinga ne ***Zamarƙe***[16]
**Jagora:** Bamin kokawa bai iya ba,
Koda yaushe shi aka Shammata,
**'Yan amshi**: Ga wata kokawa ta wuce da shi,
Karsa nai kakkaɓe mashiƘasa[17].

### 6.3.1.3 Zuga

Shi kuwa zuga ana iza mutum ko cicciɓa shi ko kambama shi, a kai shi ga wani babban matsayi wandaƘila ma bai kai shi ba, don a sanya shi ya aikata wani abu da bai yi niyyar yi ba. Dama halayyarɗan Adam ce na son a kuranta shi, sai ya ji kansa ya yi girma, ya ga cewa ya kai wani babba da zai iya yin abu ko ya hana yin wani abu. Wannan na daga cikin jigogin da mawaƙan baka ke amfani da shi wajen samun biyan buƙatunsu ta fannin lamarin waƙa. Muna iya tsintar misalin zuga a cikin baitin da ke tafe.

**Jagora**: Batunga da za ni hwaɗa maka,
Kai mini gahwara,
**'Yan amshi**: Wada duk aka gadon arziki,
Wada duk aka gadonɗaukaka,
Mamman ka gadi Abubakar
Koda sayen hali nan akai, bbaba halin da kakai kuɗɗi shi kai[18],

### 6.3.2 Gargagaɗi, Faɗakarwa, Ilmantarwa

Sanar da jama'a wani abu muhimmi wanda zai amfani rayuwarsu, shi ne ilmantarwa. Idan aka ilmantar da jama'a, sai a faɗakar da su amfanin ci gaba da ilmin da suka samu. Idan aka tunantar da jama'a kan su ci gaba

---

[16]. An ]auko wannan ]an wa}a daga cikin faifan wa}o}in Alhaji Musa [an}wairo Maradun. Wannan wa}a ya yi wa Sarkin }ayan Maradun, mai taken "[an Ahmadu tsayaye, ko dauri ba ya wargi"

[17]. "Wa}ar Ibrahimu na Guraguri, mai Shinkahi bajinin maza……" waddamaka]a Ibrahim Naramba]a ya rera wa Magajin garin Shinkafi

[18]. Maka]a Sa'idu Faru, wa}ar Sarkin Musulmi Muhammadu Macci]o mai taken "ya yi sarki daidai wada mai yanzu yarri}a, Alhaji Macci]o jikan mamman mai dubun bara"

da hanuwa kan wani al'amari in mai cutarwa ne, ko na amfanuwa ne, sai a ce hakan ya zama gargaɗi.

### 6.3.2.1 Gargaɗi

ɗiyan waƙar da za a gabatar aƘarƙashin wannan sashen, sunaɗauke da kyakkyawan misali dangane da misalin gargaɗi da aka samun cin karo da shi a cikin waƙoƙin baka kamar haka:

**Jagora**: Makaranta uwarƘwaraita, kuma mai riƙonƘwari,
Ta riƙeɗanta tayimailadabi, ya yi hankali,
Ta hore shi, ba shi rena iyayensa,
Ba shi rena, iyayen wasu,
'**Yan 'amshi**: Gwamnati horo takai muɗau ilmi gaskiya[19]
**Jagora:** Mu gargaɗi mai gina ramin mugunta,
Shi dai mai gina ramin mugunta,
To ka gina shi gajere, in baka sani ba kai ka faɗa,
**'Yan'amshi**: Mu gargaɗi mai ginaramin mugunta[20]
**Jagora**: Yaƙi mukai da rashinɗa'a
Kowa ya lura da zamani[21]

### 6.3.2.2 Faɗakarwa

Haka ma misalai da ake da su na faɗakarwa a cikin waƙoƙin makaɗan baka ba suƘirguwa, wannan baiti da aka bayar zai zama misali da aka tsakuro daga cikin waƙoƙin:

**Jagora:** Ba a hawan Sallah, sai da lahiya uwar jiki,
sai da ke aka cin duniya, ana ta malkashi, har ana
rawar jiki
**'Yan'amshi**: Na taho in gaisheki, lafiya uwar jiki,
Babu mai hushi da ke[22]

### 6.3.2.3 Ilmantarwa

Ilmantarwa ba ta taɓaƘarewa a cikin al'umma, domin kuwa dukkanin rayuwar duniya koyo ake, shi yasa Hausawa ke yi wa duniya kirari da makaranta. Su kuwa mawaƙa suna da cikin mutanen ke amfani da

---

19. "Wa}ar mu dau ilmi Gaskiya" ta Audu Inka Bakura

20. Wa}ar Garga]i kan mutane su guji yin yaudara da mugunta ta Alhaji Mamman Shata Katsina

21. Maka]a Musa [an}wairo Maradun a wa}arsa ta garga]i kan halayen banza, na rashin ]a'a

22. A cikin wa}ar [angiwa Zuru wadda ya fa]akar kan kula dalafiyar jikimai suna, "Lafiya uwar jiki……"

misalai na rayuwa don su buga misali a cikin waƙoƙinsu. Wannan koyarwa ce a cikin al'umma. Ga misali nan daga cikin waƙa:

**Jagora:** Sababbin kuɗin Nijeriya anka samat,
**'Yan'amshi**: An canza mana kuɗi, biyan buƙatummu don yaƘaru[23]
**Jagora:** Kun san Polio ab bai da kyau, bari yaraƘanana yake kashi[24]
**Jagora:** Sida mugun ciwo ce, in ya kamaka, boka bai fidda ka, likitta bai fidda ka[25]

### 6.3.3 Nishaɗantarwa

Wani babban jigo ne daga cikin jigogin waƙoƙin baka mai armashi da yakeƘayatar da masu sauraro. Waƙa tana da tasiri ga zuciya da za ta saka mai sauraro annashuwa a duk lokacin da ya saurareta. Wannan nishaɗin da yake samu ga waƙa shi ya sa yake buƙatuwa da ya riƙa maimaita saurarenta ba tare da ya gundura ba. Ba don nishaɗin da waƙa ke da shi ba, da mutum idan ya saurareta sauɗaya ba zaiƘara marmarin sake saurarenta ba. Waƙoƙin 'Yan kama da waƙoƙin zari kusan na nishaɗantarwa ne. Misali:

Sani Kurhi daAmadu Ashana mawaƙaban dariya ne. Aikinsu su samu waƙoƙin wasu makaɗa, sai su yi musuɗani na sauti ko amon waƙoƙin ta hanyar canza kalmomin ainihin waƙar da na ban dariya. Misali*Tuwo yasha lalabar makahi* in ji Sani Kurhi wadda ya canza daga waƙar larabci ta Ishiriniya......

Waƙar Bawa ɗan'anace 'Yartsakkuwa wadda ya yi wa mutanen Raha yana cewa:

**Jagora:** Arna da kaka kuna shan giya
Sai da rani ku ce bakuƘaunar giya,
matsa ga aiki gamawa akai,
Danjimma gojen mutanen Raha

Amadu Ashana ya ari amon wannan waƙar ya mayar da shi kamar haka:

**Jagora:** Yara da rani ku ce bakuƘaunar awo,
Amma matsama masa haɗewa kukai,
Ta'ala muna roƙonka masaɗari,
Zama tunda masat haɗewa Mukai.

---

[23]. Wa}ar ilmantarwa kan sababbin ku]in Nijeriya wandda Maka]a Sa'idu Faru ya yi
[24]. Wa}ar Sule mai kwamsa kan illar Cutar Shan-inn mai suna Polio
[25]. Wa}ar ilmantarwa kan cutar Sida / kabari kusa/ "Aids"

**Auna Fahimta**

1. Jero jigogin waƙoƙin baka na Hausa guda uku
2. Jigon bandariya da na nishaɗantarwa duk abuɗaya ne, ko mun aminta da hakan?

**Kammalawa**

A wannan kashi samfuri ne waƙoƙin masu jigo iriɗaya. Waɗannan waƙoƙi sunaƘarƙashin jigon ilmantarwa, da faɗakarwa da nishaɗantarwa kamar yadda aka tattauna a sama. Wani abin burgewa shi ne, idan za a yi nazarin waƙoƙin nishaɗantarwa, sai an yi nazarin asalin waƙoƙin da rukunin 'yankaman kan yi waɗani su sauya kalmominsu da na nishaɗi. Wannan ana iya kiransa da aron fasaha.



## 6.2.1 Taƙaitawa

- Waƙoƙin da aka gani a sama sunƘunshi na zambo da yabo waɗanda duk wasu halaye ne da ake furtawa cikin maganganun azanci
- An ga rukunin wasu waƙoƙi na ilmantarwa da faɗakarwa domin al'umma su farga da abinda ke faruwa a cikin al'ummarsu

## 6.5 Jingar Aiki

- Su wa ake kira 'yan kama? Me ya bambanta 'yan kama da 'yan gambara?
- Me ake kiraɗani a waƙoƙin baka?
- Kawo jigogin waƙoƙin baka uku tare da misalanɗan waƙaɗaya aƘarƙashin kowane misali



## 6.6 Manazarta

Gusau, S. (2016) *Makaɗa da Mawaƙan Hausa II*, Century Research and Publishing Limited, Kano shafi na 53

Waƙar Sarkin Yawuri Abdullahi wadda makaɗa Aliyu ɗandawo ya yi masa.

Waƙar Alhaji Musa ɗanƙwairo Maradun. Wadda ya yi wa SarkinƘayan Maradun, mai taken "ɗan Ahmadu tsayaye, ko dauri ba ya wargi"

Waƙar Ibrahimu na Guraguri, mai Shinkahi bajinin maza……" waddamakaɗa Ibrahim Narambaɗa ya rera wa Magajin garin Shinkafi

Waƙar Sarkin Musulmi Muhammadu macciɗo mai taken "ya yi sarki daidai wada mai yanzu yarriƙa, Alhaji Macciɗo jikan mamman mai dubun bara" ta Makaɗa Sa'idu Faru.

Waƙar mu dau ilmi Gaskiya" ta Audu Inka Bakura.

Waƙar Gargaɗi kan mutane su guji yin yaudara da mugunta ta Alhaji Mamman Shata Katsina

Waƙar gargaɗi kan halayen banza, na rashinɗa'a, ta Makaɗa Musa ɗanƙwairo Maradun

Waƙar ɗangiwa Zuru wadda ya faɗakar kan kula da lafiyar jikimai suna, "Lafiya uwar jiki……"

Waƙar ilmantarwa kan sababbin kuɗin Nijeriya ta Makaɗa Sa'idu Faru.

Waƙar Sule mai kwamsa kan illar Cutar Shan-inn mai suna Polio

Waƙar ilmantarwa kan cutar Sida / kabari kusa/ "Aids" ta Sa'adu Bori, Nijar

## 6.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. daga cikin jigogin waƙoƙin baka akwai:

a) Yabo
b) Zuga
c) Zambo

3. Nishaɗi da bandariya duka abu xaya ne domin haka ne ma aka sami erukunin mawaƙan baka na Hausa da ake kira makaxan bandariya, kuma an yarda waɗannan makaɗa na sanya nishaɗi ƙwarai a zukatan masu sauraro tare da sanya su dariya.

# RUKUNI NA UKU

Kashi Na 1 Kayan Kiɗan Hausawa
Kashi Na 2 Kayan Kiɗan Hausawa I

## KASHI NA 1 KAYAN KIƊAN HAUSAWA

**Abubuwan da Suke Ciki**

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufar Darasi
1.3 ƙunshiyar Darasi
    1.3.1 Kayan Kiɗan Hausawa
        1.3.1.1 Kayan Kiɗan Hausawa na Gargajiya
        1.3.1.2 Kayan Busawa
        1.3.1.3 Kayan Bugawa
        1.3.1.4 Kayan Kiɗa na Girgizawa
    1.3.2 Kayan Kiɗan Hausa na Zamani
        1.3.2.1 Ganga
        1.3.2.2Kayan Busawa
        1.3.2.3 Kayan Daddanawa na Zamani
        1.3.2.4 Sutudiyo
        1.3.2.5 Komfuta
1.4 Taƙaitawa
1.5 Jingar Aiki
1.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Nazari
1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



### 1.1 Gabatarwa

ƙarƙashin wannan kashi za a tattauna kan ababen da ake amfani da su wajen samar da sauti. Wannan sauti da shi waƙa ke tafiya. A Rukuni na farko, kashi na biyu, an yi shimfiɗa kan ma’ana ta kiɗa da waƙa. A wannan ɓangaren tattaunawar za ta kasance kan kayan da makaɗa ke amfani da su wajen tafiyar da sauti.



### 1.2 Manufa

ƙudirin wannan darasi shi ne domin a gabatar daɗalibai abubuwa masu muhimmanci da dangane da kiɗa da waƙa kamar:

- Gabatar musu da kayan kiɗan gargajiya mabambanta
- Bayyana wasuɗaiɗaikun mawaƙa nab aka da abin kiɗansu
- Gabatar da Kayan kiyan kiɗan zamani tare da misalansu

## 1.3 Kayan Kiɗan Gargajiya da na Zamani

Manyan rukunnan kayan kiɗan biyu ne: waɗanda suka daɗe ana amfani da su wajen samar da sauti, da kuma waɗanda suka samu ga Hausawa saboda haɗuwar Hausawan da wasu falsafofi na waƙa ta zamani.

### 1.3.1 Kayan kiɗan Hausawa na Gargajiya

Waɗannan kayan kiɗa su ne Bahaushe ya faro da su tun lokacin da ya fara yin kiɗa. waɗannan kayan sun samu ta hanyar amfani da wani abin da za a buga ko aƘwanƙwasa ko a girgiza ko a busa don su samar da sauti ko amo daban-daban maiƘayatarwa. Da tafiya ta yi nisa ne aka yi ta samun ci gaba naƘayatar da su da yi musu dabaru daban-daban da samar da kayan kiɗa na kaɗe-kaɗe daban-daban.

#### 1.3.1.1 Kayan Bugawa

Akwai kayan kiɗa na bugawa da dama da suka haɗa da Kalangu / ganga, kotso, tambari, da taushi, kuntigi da kukuma da tandu, da kuge duk kayan kaɗawa ne na samar da sauti. Makaɗan Hausa na gargajiya da dama suna amfani da irin waɗannan kayan kiɗa na waƙoƙinsa. Daga cikin makaɗan waɗannan kayan kiɗa akwai:

- Kalangu: Alhaji Dr. Mamman Shata da Alhaji Muhammadu Gambu
- Kotso: Ibrahim Narambaɗa da Maidaji Sabon-birni
- Ganga: Alhaji Mamman Kwantagora da Baballe Maiganga
- Kuntigi: Alhaji Adamu ɗanmaraya Jos da Alhaji Sani ɗan'indo
- Kukuma: Garba Sufa da Amina Maikukuma

Misalan hotunan wasu daga cikin kayan kiɗan:



Kalangu



Bandiri



Ganga



Ƙuge

### 1.3.1.2 Kayan Kiɗa na Busawa

Ta kayan kiɗa na busawa kuwa akwai Farai da kakaki da algaita da sarewa, da shantu daƘaho duk kayan busawa da baki ne domin samar da sauti. Misalin waɗannan kayan daga hotuna su ne:



Sarewa

### 1.3.1.3 Kayan Kiɗa na Gogawa

Su ma akwai makaɗan da suka keɓanta ga waɗannan kayan kiɗa da suka haɗa da goge, gurmi, garaya. Kowane abin kiɗa da nau'in sautin da yake bayarwa, wanda da zarar an ji wannan kiɗan an san da abin kiɗan da aka yi amfani da shi. Daga cikin masu amfani da waɗannan kayan kiɗan su ne masu kiɗan bori, sai dai ko bayan su akwai makaɗan suke amfani da su a matsayin abin kiɗa. Misalin masu amfani da waɗannan kayan kiɗan su ne:

- Garaya: Alhaji dawai Maigaraya da Ado Joji
- Gurmi: Ali Makaho da Haruna Oji
- 



Garaya

### 1.3.1.4 Kayan Kiɗa na Bugawa na Mata

Waɗannan kayan kiɗan mata ne da aka fi yi a cikin gidan Bahaushe. Waɗannan kayan kiɗan sun haɗa da tasoshi, Ƙwarya, gora, turmi da taɓarya. Matan da ke zaune a cikin gida ba a bar su baya wajen sarrafa nasu azanci ba, ta hanyar amfani da kayan kiɗa don samar da sautuka mabambanta masu armashi daga cikin waɗannan mata mawaƙa akwai:

- ƙwarya: Barmani Choge da Fati ɗiyar Isah da sauransu.

### 1.3.1.5 Kayan Kiɗa na Girgizawa

Waɗannan nau'in kayan kiɗa ne da ake samun abubuwa da za a riƙa girgizawa don su bayar da sauti maiƘara. Wannan sautin wani lokaci ana yinsa yare da waƙa shi kaɗai, wani lokaci kuma za a haɗa su tare da wani abin kiɗa na bugawa, ta yadda sautukan biyu za su haɗu wuriɗaya su samar da sauti maiƘayatarwa. Daga cikin nau'in kayan wannan kiɗan akwai, kara-kara, da kacakaura, da kacau-kacau, akayau, akwai kuma zari da zobba da mundaye.

### 1.3.2 Kayan Kiɗan Hausawa na Zamani

Kamar yadda sunan ya nuna, kayan kiɗa ne da suka samu zamanin da Hausawa suka haɗu da wasu baƙi masu nau'in kayan kiɗa daban da nasu. Sai suka ari baƙin kayan kiɗan suka gauraya da nasu wajen kiɗan. Daga cikin waɗannan kayan kiɗan akwai:

### 1.3.2.1 Ganga

Babba wannan wata nau'in ganga ce da ake kiɗan mandiri da ita. Siffarta ta bambanta da gangumman Hausawa na gargajiya. Irin waɗannan ana amfani da su a studiyo, watoɗakin samar da sauti na zamani



Gangunna da Farantai

### 1.3.2.2 Kayan Busawa

Su ma waɗannan kayan kiɗa na busawa ne amma na baƙi wanda zamani ya zo muna da su sakamakon cuɗanya da wasu al'ummu, masu siffa da kakaki kamar jita da dangogin kayan busawa na zamani

### 1.3.2.3 Kayan Daddanawa na Zamani (Piyano)

Waɗannan kayan kiɗa na zamani suna da ababe da yawa da ake dannawa, don samar da samfurin kiɗan da ake buƙata. Idan aka taɓa wannan ɓangare zai ba da sautin kiɗa daban, idan aka taɓa wani, shi ma da nasa sabon samfurin. Irin waɗannan kayan kiɗa su suke tashe a duniyar mawaƙa da wajen ibadodi na kiristanci da wuraren sheƙe aya da sauransu. Misalin wannan shi ne aƘasa.




### 1.3.2.4 Studiyo

Waniɗaki ne da aka tanada musamman domin aiwatar da kiɗa. A cikin wannanɗaki akwai kayan kiɗa mabambanta da masu amsa amo ko kuwwa, sa'annanɗakin bai da wurin iska mai yawa ke shiga da za ta hana sauti ya fito yadda ake buƙata da sauransu. A takaice an shirya shi ne a matsayinɗakin sarrafa sauti na zamani.

### 1.3.2.5 Komfuta

Kasancewar duniya ta koma bisa tsari na na'ura maiƘwaƙwalwa (digital), duk wani abu da za a gabatar na ci gaban zamani, kama daga makarantu ne ko asibitoci ko wajen noma ko wajen tsaro ko wajen tafiyar da mulki, hakan bai yiwa face sai an yi amfani na'ura maiƘwaƙwalwa wajen tafiyar da aikin. A fagen kiɗa ma ba a bar su a baya ba, akwai na'uramaiƘwaƙwalwa wadda ake sarrafawa domin samar da abubuwa da yawa ciki har da sauti. Gusau, S. M. (2016)[1]

---

[1]. Gusau, S. (2016) *{amusun Kayan Ki]an Hausa*, Century Research Publishing Limited.A cikin wannan littafi za a samu nau'o'in kayan ki]an Hausawa tsofaffi da sababbi, da hotunansu. Haka nan ana samun sunayen maka]a na Hausa, kuma kowane maka]i da kayan ki]ansa.

**Auna Fahimta**

| | |
|---|---|
| 1. | Kawo kayan kixan Hausawa nau'in ganguna da ake bugawa guda uku. |
| 2. | Waxanne ne kayan kixa na gogawa? |
| 3. | Me ake da shi a zamanance a matsayin kayan kixan Hausa ? |

**Kammalawa**

Kayan kiɗan Hausawana gargajiya da na zamani aka tattauna a kai. Na zamani sun gauraya da na gargajiya a sakamakon haɗuwar Hausawa da baƙin al'ummu. Hausawa sun karɓi sabuwar fasaha ta tsara kiɗa da waƙa har da sababbin kayan kiɗan domin tafiya daidai da zamani.



## 1.2.1 Taƙaitawa

- Mun ga kayan bugawa kamar su ganga, mun kuma ga kayan busawa kamar su Algaita, akwai kuma na girgizawa kamar kacau-kacau, da na gogawa kamar tasoshi
- Akwai computer da studiyo da piyano waɗanda su ne ake ya yi yanzu domin inganta sauti

## 1.5 Jingar Darasi

- Lissafa kayan kiɗan Hausawa goma (10) waɗanda suke na gargajiya ne
- Sarewa kiɗa ce ko sauti, ko waƙa?
- Kawo misalan kayan bushe-bushe



## 1.6 Manazarta

Ahmed, S. (2019) "Sabon Zubin Waƙoƙin Hausa a ƙarni na 20" Kundin Digiri na Biyu, Jami'ar Usumanu ɗanfodiyo, Sokoto

Gusau, S. (2016) *ƙamusun Kayan Kiɗan Hausa*, Century Research Publishing Limited.

## 1.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Akwai ganga da kalangu da tambari.
2. Akwai garaya da gurmi da molo.
3. Fiyano

# KASHI NA BIYU KAYAN KIƊAN HAUSAWA

**Abubuwan da Suke Ciki**


2.1 Gabatarwa
2.2 Manufar Darasi
2.3 ƙunshiyar Darasi
    2.3.1 Kayan Kiɗan Hausawa
        2.3.1.1 Kayan Kiɗan Hausawa na Gargajiya
        2.3.1.2 Kayan Busawa
        2.3.1.3 Kayan Bugawa
        2.3.1.4 Kayan Kiɗa na Girgizawa
    2.3.2 Kayan Kiɗan Hausa na Zamani
        2.3.2.1 Ganga
        2.3.2.2 Kayan Busawa
        2.3.2.3 Kayan Daddanawa na Zamani
        2.3.2.4 Sutudiyo
        2.3.2.5 Komfuta
2.4 Taƙaitawa
2.5 Jingar Aiki
2.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Nazari
2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta




## 2.1 Gabatarwa

Saninmu ne waƙoƙinƘarni na 17, 18 da 19 jigoginsu sun keɓanci addinin musulunci, faɗakarwa koyar da ilimi da duk wani abu da ya shafi kwaɗaitar da al'ummu na su zama abinƘwarai, babu hululu. Wannan ya sanya a waɗancan lokuttan duk darussa na addini da koyon ibada da gargaɗi ana tsara su cikin waƙa, a watsa su cikin al'umma, su kuma su lazimci karantasu da maimata su don darussan da ke cikin waƙoƙin. dukkan waƙoƙin da suka shafi neman duniya, ɓatanci da batsa, aka yi watsi da su, masu ruhin addini suka maye gurbinsu. Mata a cikin gida idan suna aikace-aikacensu waɗannan waƙoƙin suke rerowa. Sai dai waƙoƙin da suka maye gurbinsu waɗanda su ne naƘarni na 20 da 21 salonsu ya sauya daga waɗanda muka ambata a baya kwata-kwata, inda aka samu cuɗanya da baƙi, waɗanda su ne turawa, aka samu ilimin boko, aka fara siyasa aka samu kayan jin daɗi na more rayuwa. Nan take aka samu wasu mawaƙa suna yin waƙoƙin sha'awa irin na soyayya da waƙe ababe masu kyau, da waƙoƙin siyasa musamman na jam'iyyu sauransu. Wannan darasi zai yi duba zuwa ga zubi da tsarin waƙoƙinƘarni na 21.

## 1.2 Manufa

Kamar kowane darasi daga cikin darussan Da suka gabata, a wannan darasi za a gabatar da abubuwan da sukaƘunshi:

- Gabatar da waƙoƙinƘarni na 21 ga al'umma.
- Gabatar nau'o'in kayan kiɗan Hausawa na gargajiya
- Gabatar da nau'o'in kayan kiɗa na zamani da Hausawa suka ara daga baƙi.

## 2.3 ƙunshiya

### 2.3.1 Sabon Zubin Waƙoƙin Hausa Hausa a ƙarni na 21

Mawaƙan zamani sun fara samuwaƘarshenƘarni na Ashirin daɗaya (21)[2] saboda sauyin da al'ummar Hausawa suka samu ta fuskoki daban-daban na rayuwarsu. A wannan kashi za a leƙa yadda waƙoƙin suke a da da kuma sauyin da aka samu a waƙe a wannanƘarni na 21.

#### 2.3.1.1 Yanayin Kiɗan Waƙoƙin Zamani na Hausa (Muhallin Kiɗa daɗakin samar da sauti)

KafinƘarni na 21 mawaƙa kan rera waƙoƙinsu tare da kiɗa, da sauti irin wanda ake samarwa da kayan kiɗan Hausawa na gargajiya. Ko kuma mawaƙi ya shirya waƙarsa ba tare da kiɗan ba, ya gabatar da ita ga wanda ya yi waƙar dominsa. Amma a wannanƘarni na 21 an samu sababbin kayan kiɗa daga makwabtan Hausawa waɗanda suka shigoƘasar Hausa ko kuma Hausawan suka kai musu ziyara, sai aka samu tasirin dangantaka ta fuskar karɓar sababbin kayan kiɗa aka haɗa su da tsofaffin kayan kiɗa na gargajiya ana samar da sautin waƙa da su. Irin waɗannan kayan kiɗa, an amabace su a kashin da ya gabata misali Gita, Fiyano, Gangumma irin na zamani[3].

#### 1.3.1.2 Yanayin Jagoranci a Amshin / karɓin Waƙoƙin (amshin shata / karɓa-karɓa)

---

2. Wannan magana an tsince t  ne a cikin littafin Gusau, (2008) *Wa}o}in Baka a {asar Hausa: yanye-yanayensu da Sigoginsu*.Kano Bench Mark Publisher Limited

3. Gusau, S. (2016) *{amusun Kayan Ki]an Hausawa*, kamar ]ure na 26 da 27

Jagora da ‘yan amshinsa aka sabu da su waƙoƙin baka. Ko kuma makaɗi shi daɗan ma’abbansa, ko kuma shi kaɗai. AƘarni na 21 ana samun duk irin wannan yanayi na amshi. Inda bambancin ya bayyana shi ne, a waƙoƙin baka irin na da, ba a cika haɗa maza da mata a matsayin ‘yan amshi ba. Duk da yake ana samunɗaiɗaikun waƙoƙin baka waɗanda akwai haɗaka[4]. Waƙoƙin wannan zamani cike suke da salon haɗa ‘yammata da samari a matsayin masu yi wa jagora amshi, kuma yanayin amshin yana zama kodai amshin shata, ko kuma na karɓa-karɓa[5]. Ana iya samun jagora da mutum biyu mata, ko jagora da mace da namiji, ko jagora da mata da yawa.

Mace: Taho muzauna mu yi alƙawali ni taka ce Ladidin Baba,
Kar ka bar ni, yaka dawo wurina ban saba ba.
Namiji: Taho zo wurina, in ka bar ni ana ban sab aba.
Ladidin Baba, ki dena Kuka, tafiya ba mutuwa ba.
(Nazifi Asananik: Waƙar Ladidin Baba)

### 1.3.1.3 Yanayin ‘Yan amshin Waƙoƙin (Murya /Muryoyi)

Cajin sautin murya a cikin waƙoƙin Hausa kamar a waƙar ɗanmaraya Jos misali ne na yadda ake aron murya a waƙoƙin baka. MawaƙanƘarni na Ashirin suna aron muryar wasu mawaƙa, ko karin wasu waƙoƙi suɗora tasu fasahar a kai. Wasu mawaƙan kan ari karin waƙoƙin baka wajen tsara rubutacciyar waƙa. Wasu kan ari karin takwarorinsu mawaƙa suɗora baitukan waƙarsu. Salon aron kari ko murya bai tsaya a nan ba, ana aron karin wasu waƙoƙin Indiyawa da Turawa da Larabawa wajen tsara falsafarsu.[6] A bayanan da suka gabata an ga yadda makaɗan ban-dariya ke aron karin wasu waƙoƙi su sauya kalmomi a matsayin tasu waƙa don su nishaɗantar. Haka nan ake aron arin waƙoƙin Indiyawa da Larabawa a tsara waƙe cikin Hausa. Misali

> Abinda duk nai miki nayi dama,
> Laifin da nai miki ki yafe mini,
> Na roƙi Alfarma, na roƙi Alfarma,
> (Waƙar Ibro a cikin Fimɗinsa na Ibroɗan Indiya)

---

[4]. Wa}o}in Noma na Kulu Mukkunu Wasagu, da Wa}o}in Mamman Gawo Filinge duk suna daga cikin misalan inda ake samun ha]akar jinsi tsakanin Jagora da’Yan amshin wa}a.

[5]. Suleman, B. (2019) “Sabon Zubi a Wa}o}in {arni na 21 cu” Kundin Digiri na Biyu Jami’ar Usumanu [anfodiyo, Sokoto. Ko a tsofaffain wa}o}i irn na su Maidaji Sabon Birni da Naramba]a wa]anda yanayin amshinsu na kar~a-kar~a ne, watojagora zai fa]i wani sashe na ]an wa}a, sai ‘yan amshi su ci gaba da }ari ga abinda jagoran ya ce wato su iyar masa har a samu cikon ]angon wa}a.

[6]. Bunza, D. (2015) “Aron Murya a Cikin Rubutattun Wa}o}in Hausa”, Yobe Journalof Language, Literature and Culture, Department of Languages and Linguistics

ƙarin bayani kan yadda yanayin amshi a waƙoƙin baka kan samu shi ne sauraron waƙoƙin domin tantancewa.

**Auna Fahimta**

| |
|---|
| 1.Daga cikin kayan kixan Hausawa na zamani akwai ganguna da….. da …… |
| 2.kawo sunayen maƙawan baka na zamani guda uku |
| |

- Anga rukunin waƙoƙi kasha biyu: Tsofaffi da Sababbi
- Tsofaffin irin su waƙoƙin Makaɗa ɗanƙwairo, Audu Waziri ɗanduna, Sani ɗan'indo
- Sababbin Mawaƙa kamar na Naziri Sarkin Waƙa, Nazifi Asnani, Aminu Alan Waƙa, FatiNijar

**Kammalawa**

A wannan kashin an fahimci akwai bambanci tsakanin amshin tsofaffin mawaƙan baka irinsu ɗanƙwairo da Narambaɗa da Maidaji Sabon birni, da mawaƙan wannanƘarni na Ashirin daɗaya musamman waƙoƙin da ake rerawa a sutudiyo (studio) waɗanda ake gani a Fim (Film) da Yutub (You tube) ta fuskar 'yan amshi, da kuma muryar da ake rera waƙoƙin da su. Akwai kamanci na yawan 'yan amshi ko adadinsu, bambanci wajen haɗakar jinsi ne. Haka nan yanayin muryar waƙa kuma akwai tsari irin naɗani tsakanin mawaƙa.



## 1.4 Taƙaitawa

- Wannan tattaunawa tana nunairin yadda aka samu sauyi ga waƙoƙin Hausa ta fuskar sababbin jigogi da yanayin amshi da zubi da tsari
- Waƙoƙin Zamani rubutattu ne, sai dai suna da bambanci da rubutaccin waƙoƙi waɗanda marubuta suka samar aƘarni na 19 da Ashirin
- Bambancin waƙoƙin zamani da tsofaffin rubutattu akwai naƘafiya, wato amsa amo, da yawanɗiyan baiti

## 1.5 Jingar Darasi

- Me kuka fahimta da fasaharɗani a waƙoƙin baka?
- Kwatanta yanayin amshin waƙoƙin Nazifi Asnanik da Maidaji Sabon-birni.

## 2.6 Manazarta

Suleman, B. (2019) "Sabon Zubi a Waƙoƙin ƙarni na 21 cu" Kundin Digiri na Biyu Jami'ar Usumanu ɗanfodiyo, Sokoto.

Bunza, D. (2015) "Aron Murya a Cikin Rubutattun Waƙoƙin Hausa", Yobe Journal of Language, Literature and Culture, Department of Languages and Linguistics

## 1.6 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

**1.** Daga cikin kayan kixan Hausa na zamani akwai ganguna da jita da fiyano.

2. daga cikin mawaƙan baka na zamani akwai:

   a) Aminu Ladan Abubakar (ALA)
   b) Nazifi Asnanic
   c) Fati Nijar

# KASHI NA UKU NAZARIN JIGOGIN WAƘOƘIN ƘARNI NA ASHIRIN DA ƊAYA

**Abubuwan da Suke Ciki**


3.1 Gabatarwa
3.2 Manufar Darasi
3.3 ƙunshiyar Darasi
 3.1.1 Jigogin Waƙoƙin ƙarni na 21
  3.3.1.1 Soyayya
  3.3.1.2 Siyasa
  3.3.1.4 Faɗakarwa
  3.3.1.5 Ilmantarwa
  3.3.1.6 Yabo
3.4 Taƙaitawa
3.5 Jingar Darasi
3.6 Manazarta
3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta




## 3.1 Gabatarwa

Bayan sharar fage da aka yi kan lamarin waƙoƙinƘarni na 21, yanzu kuma za mu zurfafa don sanin me jigoginsu. Kamar yadda muka bayyana a baya na cewa waƙoƙinƘarni na 20 da 21, sun sauya fasali dangane da waƙoƙin sauranƘarnukan da suka gabata. Bahaushe ya ce in kiɗa ya canza, rawa ma sauyawa take. Wannan ya sanya jigogin waƙoƙin ya sauya daga zuhudu, Ƙana'a, bege da sauransu. Yanzu za mu waiwayi waɗannan jigogin don sanin me suke ciki.



## 3.2 Manufa

Manufar wannan darasi wanda ita ce maƙasudin darasin shi ne:

- Sanin jigogin waƙoƙinƘarni na 21
- Nazari da sharhi kan jigogin na Ƙarni na 21
- Kwatanta jigogin waƙoƙinƘarni na 21 da sauranƘarnukan da suka gabace shi.

## 3.3 ƙunshiya

### 3.3.1 Jigogin Waƙoƙin ƙarni na Ashirin da ɗaya (21)

A wannan kashi za a yi bayanin irin saƙonnin da keƘunshe cikin waƙoƙin da ka ga sunanyensu da samfurinsu a cikin bayanan da suka gabata. Wannan saƙo shi ake nufi da jigo. Jigo kuma shi ne manufar waƙa ko saƙon mawaƙi zuwa ga jama'arsa[7]. Daga cikin manufofin yin waƙa akwai gwarzantawa da kushewa da nishaɗantarwa. Ga misali kamar haka:

#### 3.3.1.1 Soyayya

Soyayya na nufin buƙatuwar kusanta da wani ko wata. Akasin so shi neƘi. Soɗabi'a ce da aka halicciɗan adam da ita. Yana jin so koƘi a tunaninsa amma ba a iya ganinsa da ido sai dai a bayyana shi ta hanyar kalmomi da aiki. So na tsakanin mutum da maliccinsa, da son sahabai da alayen Annabi da son dake tsakanin iyaye da'ya'yansu, da son da ke tsakaninƘawaye da abokai da ma'aurata. Ga misalin waƙar soyayya:

So baiƘarewa, so bai canzawa,
Wanda nakeƘauna ko da'iman fa ba zai canza ba,
Ga ni ga ka
Nai nazarin so, ga ni ga ka,
Babu kamar so, ga ni ga ka
(Waƙar ga ni ga ka ta Ali Nuhu)[8]

#### 1.3.1.2 Siyasa

Siyasa tsari ne na tafiyar da jama'a domin a shugabance su wajen tafiyar da wasu lamurransu na rayuwa. Makaɗa kan shirya waƙoƙinsu kan wannan jigo, kasancewar siyasaɗaya daga cikin hanyoyin tafiyar da rayuwa. Mawaƙan siyasa na lokuttan baya, sunaɗauke daɗiyan waƙa da baituka masu nunaki shinƘasa da kishin kai da manufofin jam'iyya da nuna tsintsar aƙidar siyasa[9]. Mawaƙan siyasa na yanzu sun bambanta da na baya saboda wasu dalilai da suka haɗa da neman kuɗi domin biyan buƙatun rayuwa, misali

---

[7]. [angambo, A. (2007) *[aurayar gadon Fe]e Wa}a*, Amana Publishers Kano, shafi na 14

[8]. Suleman, B. (2019) "Sabon Zubi a Wa}o}in {arni na 21 cu" kamar ]ure na 32, shafi na196

[9]. Aikin da Adamu, A. (2004) "Nazarin Zambo da Zagi a cikin siyasar arewacin Nijeriya 1950-1966" Jami'ar Usmanu [anfodiyo, Sokoto, yana ]auke da bayanai kan yadda aka gudanar da siyasa a jamhuriya ta farko. Akwai misalan wa}o}i da wasi}u da dama acikin wannan kundin

**Jagora:** Baban Usamatu ka ba ni mota, zan hau naɗan yi
yawon duniya,
Mu fara sauka Kano mu sauka Abuja, Kaduna, mu dawo Zariya,
Ka ba ni kuɗɗi ka ba ni mota, Tafida saura ka biya mini Saudiyya,
Kai ko Kabiru kaɗan roƙammin, ni ma ko zan yo mamaya,
Zuwaira sauka daga cikin motan nan, don na san kin iya na iya,
Saboda nace ka saka ni alayi, Kabiru jeka kadawo lafiya.
(Muh'd Birnin Magaji: Waƙar Salihu Tafida)

Wannan baiti waƙa ce zuwa ga waniɗan siyasa, amma mawaƙan ba su waƙe wata Aƙida ta siyasa ba, ko tarihin wani al'amari da ya faru ba wanda ya shafi siyasar wanda suke waƙewa, sai dai suna neman biyan buƙatun rayuwarsu ne zuwa ga wanda suke yi wa waƙar kamar mota da kuɗi da kujerar Makka.

### 1.3.1.3 Faɗakarwa

Tunatarwa ga al'ummadomin su yi gyara ga al'amurransu musamman waɗanda ba su tafiyar dasu akan daidai, su daidaita su domin rayuwarsu ta yi kyau shi ake nufi da faɗakarwa[10]. Ana samun jigon faɗakarwa a cikin waƙoƙin kowaneƘarni saboda muhimmin jigo ne wanda ke gyaran halayen al'umma. Misalin faɗakarwa a cikin wannanƘarni shi ne:

**Jagora**: Haƙuri yana da misali ba z akaɗauki reni ba, Alan waƙa
Haƙuri yana da sururi ba z akaɗauki zambo ba, Alan waƙa
Baka zo da Zambo ba, Alan waƙa,
Ba halina zambo ba, Alan waƙa,
Ba da tsegunagun ba, Alan waƙa,
Rama cuta ga macuci bailla ba ne, Allan waƙa,
(AminuAla: Waƙar An Fa Gane Wanzami)

A baitin da ke sama, ana nuni kan amfanin yin haƙuri ga kowane al'amari musamman idan ya shafi mu'amala da mutane a cikin hada-hada ta yau da kullum.

### 3.3.1.4 Ilmantarwa

Ilmantarwa na nufin sanar da jama'a wani sabon abu wanda ba su sani ba. Waƙoƙi na baka ko rubutattu na daga cikin hanyoyin bayar da ilmi a makarantu ko ga taron jama'a ko ga al'umma.

[10]. CNHN,(2006) *{amusun Hausa*, CSNL, Jami'ar Bayero, Kano, shafi na 129

### 1.3.1.4 Yabo

Ana gina waƙa kan jigon Yabo. Yabokuma amfani da kalmomi ne masu nuna amincewa da hali daɗabi'un mutum ko dabba ko wani abu. A waƙoƙin baka idan ana son a yaba mutum ana nuna halayensa kyawawa ne, kuma ana siffantasada wasu halaye daɗabi'u ko ayyuka waɗanda za suƘara masa kwarjini da martaba a idon mutane[11]. Misali a cikinbaitukan waƙa:

**Jagora:** Ku yi waƙar sojoji don na san a gidan nan ba wasa,
Zaki babban jigo hafsoshin gwabzawa,
Yusuf saka mazajeƘi jurewa,
Sojoji in sun jero kai za su yi gaidawa,
Taku sai Giwaɗan Akuya tsalle ya yi saɓawa,
Hadari sai kallo,
YauƘasa na kyawu tun da maza ke riƙo na ta ba wasa,
(Fati Nijar: Waƙar Tukur Buratai)

**Auna Fahimta**

1. Kawo manufofin waƙoƙin baka na zamani guda biyu
2. ….. babban jigo ce waƙoƙin baka na zamani

**Kammalawa**

Jigo shi neƘashin bayan kowace waƙa ta baka ko rubutacciya. In har za a yi nazarin fasihanci a cikin kowace wallafa, to da jigo ake farawa. Dalilin yin haka shi ne jigo yana tare da manufar yin aiki, domin jigo shi ne saƙon kowane aiki. Jigogi irinsu Yabo, da Faɗakarwada Ilmantarwa da siyasa da kuma soyayya aka ga misalansu a bayanan da ke sama.



### 3.4 Taƙaitawa

- Yadda waƙoƙinƘarni na Ashirin daɗaya suke da siffofinsu daban da sauranƘarnonin da suka gabace su, hakanan jigoginsu da salailansu

[11]. Gusau, S. (2002) "Salo a Wa}o}in Baka: Tsokaci Kan Turke da Rabe-Rabensa" A Cikin Nazari a kan harshe da Adabi da Al'adun Hausa, Kano:Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya

## 3.5 Jingar Darasi

- Bayyana ma’anar Jigo a taku fahimta
- Kawo misalan waƙoƙi uku masu jigon soyayya
- Jigon Faɗakarwa muhimmine a cikin waƙoƙi na kowane zamani, kun amince da hakan?

## 3.6 Manazarta

Adamu, A. (2004) “Nazarin Zambo da Zagi a cikin siyasar arewacin Nijeriya 1950-1966” Jami’ar Usmanu ɗanfodiyo, Sokoto.

CNHN,(2006) *ƙamusun Hausa*, CSNL, Jami’ar Bayero, Kano, shafi na 129

ɗangambo, A. (2007) *ɗaurayar gadon Feɗe Waƙa*, Amana Publishers Kano, shafi na 14

Gusau, S. (2002) “Salo a Waƙoƙin Baka: Tsokaci Kan Turke da Rabe-Rabensa” A Cikin Nazari a kan harshe da Adabi da Al’adun Hausa, Kano:Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya

Suleman, B. (2019) “Sabon Zubi a Waƙoƙin ƙarni na 21 cu”, Kundin Digiri na Biyu, Jami’r Usumanu ɗanfodiyo,Sokoto

## 3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Manufofin waƙoƙin baka na zamani sun haxa da;
   a) Faxakarwa
   b) Yabo
2. Soyayya babbar jigo ce a waƙoƙin baka na zamani

# KASHI NA HUƊU ZUBINWAƘOƘIN HAUSA A ƘARNI NA 21

## Abubuwan da Suke Ciki

4.1 Gabatarwa
4.2 Manufar Darasi
4.3 ƙunshiyar Darasi
 4.3.1 Yanayin Kiɗan Waƙoƙin Zamani na Hausa
 4.3.2 Yanayin Jagoranci a Amshi
 4.3.3 Yanayin ‘Yan’amshin Waƙoƙi
4.4 Taƙaitawa
4.5 Jingar Aiki
4.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Nazari
4.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



## 4.1 Gabatarwa

A darasin da ya gabata, an yi sharar fage a kan waƙoƙinƘarni na ashirin da jigoginsu, wannan darasi ci gaba ne kan inda aka tsaya a can baya. Domin kuwa nazarin waƙar baka bai kammala sai yi bayyana yanayin zubi da waƙa a faifan nazari.



## 4.2 Manufa

Daga cikin manufofin gabatar da wannan darasi shi ne:

- Domin a gabatarwa daɗalibai ma’ana ta zubi da tsari a fannin nazarin waƙar baka
- Domin a fito da yanayin zubi da tsarin waƙoƙinƘarni na 21
- Domin ganin irin sabon ci gaban zamani da aka samu day a sauya alƙiblar zubi da tsarin waƙoƙinƘarni na 21 da na sauranƘarnukan

## 4.3 ƙunshiya

### 4.3.1 Zubi da Tsarin Waƙoƙin ƙarni na Ashirin da ɗaya (21)

Zubi da tsari yana nufin siffar abinda ake nazari. Idanɗalibai suna son su bayyana yanayin matanin da suke tsokaci to su shiga neman kalmomin da za su kwatanta abinda idonsu ke nazari. Yahya, (1997)[12] ya bayyana siga a matsayin siffa ko kamannun waƙa waɗanda ke bambanta tsakanin rubutacciyar waƙa, da ta baka. Wato akwai abubuwan da suka keɓanta ga waƙar baka kawai, da kuma abubuwan da suka keɓanta ga rubutacciyar waƙa.

#### 4.3.1.1 Zubin Baitoci

Tsarin waƙoƙinƘarni na 21 sun bambanta da waƙoƙin da suka gabace su ta fuskokin da suka haɗa da mabuɗi, da marufi, da layukan baiti, da yawan gaɓoɓinɗango, da yawan baitoci a waƙa, da ambaton suna, da kiɗa, da amshi, da rawa, da karɓeɓeniya, da aiwatar da waƙa aƘungiyance:

- Mabuɗi marar Basmala
  Gari ya waye dukan duhu na yayewa,
  Gari ya waye dukan duhu na yayewa,
  Gari ya waye dukan duhu na yayewa,
  Gari ya waye dukan duhu na yayewa. (MudassiruƘasim)

- Mabuɗi Mai Basmala,
  Rabbana tsare ni da sharrin mutum da aljanna,
  Ya zamo yabon Ala mai kwarmaton nan,
  MaiƘulabuci maiƘwaƙwa da kishin nan,
  Kar ka bani ikon kushe don dagga kai na,

#### 4.3.1.2 Zubin ɗiyan waƙa

A waƙa mai suna "Ankwa" ta Mahmud Nagudu ya tsara baitocin waƙar kamar haka:

Zuciyata na ba ki,
Burin ido kallonki,
Murmushi ko dariyarki
Ke sa wa rai na tsuma.
ƙaunar ma'aiki ita ce mafita

12.Yahya, A. (1997) *Salo Asirin Wa}a*, Fisbas Media Kaduna

Almuntaƙa baban Binta
Kyawun halinai mu kwatanta
Ya Rabbi salli ga mai tsabta
Mai kyan hali mai kyan fata
Son fiyayye mun huta
Rabbi ka sa da shi mui zama.
Ankwa sila ce mai sadar da so daƘauna
Sonka ya tsima ni burina ka zam mijina
GurinaƘauna ya sauka jikina ya sa tunani
Ankwa da so aminci daga wai ina ya zan saƙona
Ankwa yau na makance don hangenki na yi rauni
Ankwa rufe ni saya jazaba da ɗan bayani
Rai bai da buri sai in gan ki ga ki ga ni

Dole zan hawaye yaya zan sami kaina?

Waɗannan baitoci gaɓoɓin muryoyinɗangoginsu sun bambanta da juna dangane da tsawo. Baiti na uku ya fi na biyu tsawo, shi kuma na biyu ya fi na farko tsawo. Mahmud Nagudu ma haka ya tsara waƙarsa mai suna "Tallafa min" wasu baitocin sun fi wasu tsawo. Misali a wasu baitoci yana cewa:

So rai yaiƘudiri,
Zuciya na ta ɓari,
Tallafa min
Tallafa min
Agaza min
Ka ceto rayuwata
Ruwa na hawaye shaida lamarinƘauna
Kar kai wauta in babu kai ni a bayana
ƙuncin zuci raɗaɗi na damuna
Tausaya min tsarkake zuciyata.

A waƙar Yakubu Muhammad mai suna "Garin daɗi" ita ma wasu baitocin sunɗara wasu tsawo. Ga misali kamar haka:

Garin daɗi ba shi ne inda ka saba ba
ƙugiyar mutunci abin da ke nesa ta jawo kusa.
Mai gaskiya ba ya shayi
Jiki an ce magayi
So in har ka bi son rayi
Haƙiƙa za ka yi juyayi.

An fahimci akwai gazawa da rashin daidaituwarɗiyan waƙa a ma fi yawancin waƙoƙinƘarnina 21 domin ba su hawa dokokin da aka shata na nazarin Rubutatacciyar waƙa. Wannan rashin daidaiton shi ya sa

ake yi wa wasu rubutaccin waƙoƙi tahamisi ko tarbi'i, amma zai yi wuya waɗanna waƙoƙi su samu shiga wannan sahun na a yimusuƘari kasancewar yanayinsu ta fuskar yawan layukan baituka da tsarin muryoyin da ake amfani da su wajen shirya waƙoƙin.

**Auna Fahimta**

| | |
|---|---|
| 1. | Yaya daidaituwar xiyan waƙa yake a waƙoƙin ƙarni na 21? |

**Kammalawa**

A wannan kashin, an tattauna a kan siffofin waƙoƙinƘarni na Ashirin ta fuskar zubin baitinsu wato yawan layukan da ke cikin gundumar baiti. An ga yadda wasu waƙoƙin suke jinkirta mabuɗinsu na basmala sai a tsakiyar waƙa a maimakon a farkon waƙa da ya zama al'adar mawaƙa. WaƙoƙinƘarni na 21 ba su da tsawo idan za akwatanta ta su da waƙoƙinƘarni na 20 inda waƙoƙinsu Alhaji Aƙilu Aliyu "Hausa Mai Ban Haushi", da Alhaji Na'ibi Sulayman Wali "Waƙar Maraba da Yanci". Waɗannan waƙoƙin suna da baitoci masu tsawo kusan sama da hamsin (50) zuwa saba'in (70). Amma waƙoƙinƘarni na 21 baitocinsu ba su wuce biyar zuwa goma ba.

## 4.4 Taƙaitawa

- WaƙoƙinƘarni na 21 ba su hawa tsarin tarbi'i ko tahamisi saboda ba su da daidaito na yawan layukan baiti, wasu waƙoƙin ba su da yawan baitoci, duk tashen waƙa za a same ta da baitoci biyar kacal

## 4.5 Jingar Darasi

- Me aka nufi da baiti? Me ya bambanta baiti daɗango?
- Waɗanne siffofi ne suka bambanta waƙar baka da rubutacciya?
- Tattauna fitattun abubuwa uku da suka bambanta waɗoƙinƘarni na 20 da na 21,ta fuskar zubi da tsarinsu

## 4.6 Manazarta

Yahya, A. (1997) *Salo Asirin Waƙa*, Fisbas Media Kaduna

## 4.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Akwai gazawa da rashin daidaituwar ɗiyan waƙa a yawancin waƙoƙin ƙarni na ashirin da ɗaya.

# KASHI NA BIYAR ZUBIN WAƘOƘIN HAUSA A ƘARNI NA 21

## Abubuwan da Suke Ciki

5.1 Gabatarwa
5.2 Manufar Darasi
5.3 ƙunshiyar Darasi
5.3.1 Salon Waƙoƙin ƙarni na Ashirin da ɗaya
5.3.1.1Ma'anar Salo Bisa Hagen Malaman Hausa
5.3.2 Misalan Salailan Waƙoƙin ƙarni naAshirinda ɗaya (21)
5.3.2.1 Salon Kwatantawa
5.3.2.2 Salon Jinsarwa
5.3.2.3 Salon Jinsarwa Mutuntawa
5.3.2.4 Salon Jinsarwa Dabbantarwa
5.3.2.5 Salon Abantarwa
5.3.2.6Salon Kwaikwayo
5.3.2.7 Salon Alamtarwa
5.3.2.8 Salon Kambamawa
5.3.3 Salon Sarrafa Harshe
5.3.3.1Karin Magana
5.3.3.2 Kalmomin Aro
5.4 Kammalawa
5.5 Taƙaitawa
5.6 Jingar Aiki
5.7 Manazarta da Wasu Ayyukan Nazari



## 5.1 Gabatarwa

Wannan darasi, wanda shi neƘarshen darussan da aka gabatar a can baya, zai yi duba ne kan wani kandamin abu da aka sani da salo. Mun sani kalmar salo ba sabuwar kalma ba ce a cikin al'umma, kuma ana samunta a cikin ɓangarori da fannoni da yawa na rayuwa na ilimi da na zamantakewar rayuwa. Salon kowane mutum ya sha bamban da na wani, wannan ya sanya masana suke ganin baiwar da Allah ya yi wa kowane ɗan adam wajen tafiyar da rayuwarshi, ita ce salonsa. Wannan kalmar aka ara, ana yin nazarinta a cikin fannoni daban-daban na ilimi. A cikin fannin waƙa, salon a bambanta ta fuskoki mabambanta da mawaƙa suka bi wajen baje kolin hajar fasaharsu. A cikin wannan darasi za mu tattauna nau'o'in salailan da ake amfani da su wajen tsara waƙa, wanda ya bambantata da sauran ɓangarorin adabi daban-daban.

## 5.2 Manufa

Kowanne al’amari yana da manufar da aka fara ginawa kafin tunanin aiwatar da shi. Wannan darasi ma kamar sauran darussan da suka gabata ya yi duba ne zuwa ga abubuwa da sukaƘunshi:

- Sanin ma’anar salon waƙoƙinƘarni na 21
- Gabatar da salailan waƙoƙinƘarni na 21
- Nazarin salailan tare da misalai daga cikin mawaƙanƘarni na 21

## 5.3 Ƙunshiya

### 5.3.1 Salon Waƙoƙin ƙarni na Ashirin da ɗaya (21)

Salo dai shi ne hanyar da mawaƙi ko marubuci ya bi wajen isar da saƙonsa. Ana iya cewa babu wani aiki na adabi da ba ya da salo, sai dai ko a ce salon ba mai karsashi ba ne. Da wannan za a ce kenan salo yana da kashe-kashe wanda za a tattauna aƘarƙashin wannan kashi. Bayan misalai na salailai a cikin waƙoƙi za a kawo tambayoyin auna fahimtar abinda aka tattauna bayan jawabin taƙaitawa.

#### 5.3.1.1 Ma’anar Salo bisa Hangen Malaman Hausa

Masana kan fannin waƙa da dama sun bayar da gudummuwarsu wajen bayar da ma’anar salo kamar haka:

Gusau, (1993)[13] ya ce: “Salo wata hanya ce da ake bi a nuna gwaninta a cikin furuci ko rubutu, kuma yana nuna yadda mutum ya shirya wani abu ta bin yanayin harshensa da zaɓar abubuwan da suka dace game da shi abin da yake son bayyanawa”.
ɗangambo, (2007)[14] cewa ya yi: “Salo shi ne hanyoyi ko dabarun isar da saƙo”.

Shi kuwa Yahya, (2001)[15] ya bayyana ma'anar salo da cewa: “Salo yana nufin duk wata dabara ko hanya a cikin waƙa wadda aka bi domin

---

[13]. Gusau, S. M. 2003 *Jagoran Nazarin Wa}ar Baka.* Benchmark Publishers Limited, Kano, shafi na 18

[14].[angambo, A. 2007. *[aurayar Gadon Fe]e Wa}a*. Amana Publishers Limited, Zaria, shafi na 218

[15].Yahya, A. B. 2001. *Salo Asirin Wa}a*. Fisbas Media Ser~ices, Kaduna, shafi 85

isar da saƙo. Ita wannan dabara ko hanya tana yi wa waƙa kwalliya ta yadda saƙon waƙar zai isa ga mai saurare ko karatun waƙar”.

Ma’anar Salo a fahimtar malaman adabin Hausa ya sa aka nemiɗauko misalai daga cikin wasu waƙoƙi domin yadda abin ya bayyana

### 5.3.2 Nazarin Salailan Waƙoƙin ƙarni na Ashirin da ɗaya (21)

Kamar yadda aka yi bayani a wajen gabatar da wannan darasi, za a zurfafa wajen bayyana salailan waƙoƙinƘarni na 21 tare da gabatar misalai daga bakunan mawaƙan wannanƘarnin kamar haka:

#### 5.3.2.1 Salon Kwatantawa

Salon kwatantawa yaƘunshi salailai aƘarƙashinsa. Salailan nan sun haɗa da kamantawa da siffantawa da jinsarwa. A Kamance akwai na daidaito da kasawa da da na fifiko. A Salon jinsarwa akwai mutuntarwa da dabbantarwa da abantarwa.
A waƙar Aminu Ladan Abubakar mai suna “Angara” shi ma ya yi amfani da kamancen daidaito a inda yake cewa:

Raƙumi da akala ko gafiya za ta ja shi ba zai tsauri ba,
Na zamo *kamar* talalaɓo namijin da ba zaiƘarfi ba,
Jijiyar jikina har daƘashi jinin jiki ruwa banɗauke ba,
Sun zamo *kamar* na jikin tsoho saffa-saffa ba maiƘwari ba.

Kalmomin da ake amfani da su wajen bayyana kamanci sun bayyana a cikin wannan waƙen na Alhaji Aminu kamar yadda aka gani an jirga kalmoin ***kamar***. An siffanta halayyar Raƙumi da wanda ba shi daƘarfi na jiki idan wani abu na jan akalar da akeɗaura masa domin a ja shi. Hakanan an sake kamanta Raƙumi da mutum wanda ya tsufa idan yana tafiya a hankali saboda ba shi daƘwarin jiki. Wannan shi ake kira kamancen daidaito. Kamancen kasawa kuwa yana zuwa da nashi nau’in kalmomi masu nuna kasawa kamar bai kai ba. Misalinda ke biyeya bayyana wannan salo:

Mahmud Nagudu a waƙarsa mai suna “Uwa uwa ce’ da ya tashi kawo kamancen kasawa cewa ya yi:

Uwa uwa ce ba kowa ke amsa sunan ba,
Mijinta ce shi ya rako maza bai nuna nagarta ba.

Faram faran kan fuska ba shi ne mizani ba,
Shimfiɗa da ruwan sanyi ba za su zamo alƙibla ba,

Zuciya ita ce komai,ɗan Adam bai gyara ba,
Tafiya yau tai nisa amsa kira ba a dace ba.

Ruwa ruwa ne ba kowanne ke da tsabta ba,
Wani a sha kana a yo wanka, ba a yi ibada ba.

A baitin farko mawaƙin ya nuna cewa mijinta ce (mijin da bai da ta cewa sai abin da matarsa ta ce don tsoronta) ba shi da nagarta, kuma da faram-faran kan fuska, da wani nuna karamci duk ba su kai gyaran zuciya ba. Idan zuciya ta gyaru, shi ke nan ana sa ran duk ayyuka sun zama masu kyau. YaƘara da cewa ko da yake ana samun ruwa iri-iri, to za ka tarar cewa wani bai kai wani ba domin ba zai yi ayukkan da wani zai yi ba.

Kamancen fifiko salo ne da keɗaukar abubuwa guda biyu ya siffanta na farko, ya ce ya fi wancan na biyun. Kalmomin mizanin da ake amfani da su don gane fifiko su ne;ɗara, da wuce, da fi, da zarce, da dai sauransu. Fati Nijar ta yi amfani da wannan salo a waƙarta mai suna 'tutar so' inda take cewa:

Idan zakara yai cara ku zam sani wannan sa'a ce,
Hakan na gani ban mance yabonka ai ni na jajirce,
FNi ne jiya ni ne yau, Ali Nuhu wai ko kun mance?
Ku juya rawa nai zarce Mansura Isa ko kun mance?

Ana ta faɗa mini raga Zainab Umar sunan ne nawa,
Garanti sa'ar kowa ni Hafsat Shehu taken nawa,
Niɗan Ahmad sunana Musbahu mai waƙewa
Zainab Idris nai zarce fagen rawa ko an tarawa

A waɗannan baitoci mawaƙiyar ta nuna cewa ko da an tara mata masu yin fim, to ita ta zarce kowa, yayin da ita kuma Zainab Idris ke cewa idan an tara 'yan fim ta zarce kowa a fagen rawa. A nan an yi amfani da kalmar '***zarce***' don a nuna fifikon wani kan wani.

### 5.3.2.2 Salon Jinsarwa:

Jinsarwa shi neɗora wa wani jinsi halayya ko daraja ko aikin wani jinsi daban da ba shi ba. Jinsarwa ta rabu zuwa gida uku kamar haka:

- Mutuntarwa
- Dabbantarwa
- Abuntarwa

### 5.3.2.3 Jinsarwar Mutuntarwa:

Mutuntarwa ita ce nau'in jinsarwar da akeɗora wa abin da ba mutum ba wata halayya ko darajar mutum. Misali, a waƙar Sadi Sidi mai suna "Rana" ya yi amfani da wannan salo inda yake cewa:

Soyayya gamon jini
In har ta yi sansani
Ba mai ba ka magani
Sai ka hangi wanda ke sonka da gaskiya.

Mutuntarwa a nan ita ce kiran soyayya da sansani, domin kuwa mutane ne ke haɗuwa su samar da sansani (taron mutane).

Haka kuma a waƙar Fati Nijar mai suna "Duniya" an sami jinsarwar mutuntarwa a wani baiti inda ta ce:

ɗalibanki ne mu yauɗalibanki ne
Duniya mun shigo ajin jarabawarki na da sauƙi.

'Yan'uwa ku biyo ni a batun da zan ta zargawa
Ja mu je da sannu muna bin ki za mu kwancewa
Duniya budurwar wawa ake ta furtawa
Ba mu ja in ja kan maganarki babu mussawa
Yau muna ajin jarabawarki duniya ga mu
Da mun yi kuskure don Allah kar ki kora mu.

A waɗannan baitoci mawaƙiyar taɗauki halayyar malami (mutum) ta bai wa duniya da cewa tana karantar daɗalibai tana yi musu jarabawa kuma su ci ga wanda ya yi karatu. Wanda kuma bai ci jarabawar ba to tana iya korarsa a dalilin kasawar da ya yi. Haka kuma an siffanta duniya da cewa budurwa ce wacce ke cikinƘuruciya.

Shi ma Mahmud Nagudu ya yi amfani da irin wannan salo a waƙarsa mai suna "Ankwa" inda yake cewa:

Ankwa ta so taiɗauri,
Manufa a so cikar buri,
Zuciya ba ta inkari,
Soyayya ke sa tsima.

Wannan shi ma mutuntarwa ne, saboda an nuna cewa ankwar soyayya taɗaure masoyi kuma zuciya ma an nuna cewa ba ta yin inkari yayin da soyayya ta sa a yi tsuma.

### 5.3.2.4 Jinsarwar Dabbantarwa:

Dabbantarwa ita ceɗaukar hali ko yanayi ko daraja koɗabi'a ko abin da dabba ce aka sani da shi sai aɗora wannan abu a kan mutum. A waƙar Yakubu Muhammad mai suna "Lai lai laƙaninƘauna" ta fimɗin "Mujadala" ya yi amfani da jinsarwar dabbantarwa a wani baiti inda yake cewa:

'Yan mata zan yo muku caffa,
Ku zo daɗai-ɗai ku yi min rumfa,
Ku zo da hanzari ku yi sassarfa,
Ka ce na ce tsakaninku ku binne ku shafa.

Na yi mafarki na afka a gidan cinnaka,
Na rasa launi na gadara tamkar hankaka,

A waɗannan baituka, mawaƙin ya nuna cewa 'yan mata za su yi sassarfa. Sassarfa kuwaɗabi'a ce ta dabbobi a yayin da suke gudu, haka kuma a baiti na biyu mawaƙin ya nuna cewa saurayin ya rasa launi irin na hankaka, wato dai ya dabbantar da shi.

### 5.3.2.5 Jinsantarwar Abuntarwa:

Abuntarwa ita ce liƙa wa mutum hali koɗabi'a ko daraja ko kuma saka mutum cikin yanayi na wani abu wanda ba dabba ba (misali dutse ko ruwa ko mota). A waƙar Mahmud Nagudu mai suna "Kalabayye" ya yi amfani da salon jinsarwar abuntarwa inda yake cewa:

Hasken sonka ya doki zuciya,
Tunanina duka gunka ya tsaya,
Rashin hangenka na kasa kwanciya,
Kai ne fitila mai haskawa,
Madalla da zuwan farin wata jigon nutsuwa daɗimuwa.

A nan mawaƙin ya siffanta saurayin da ake waƙewa da fitila mai haske, hasken kuma irin na farin wata, sannan yaƘara da cewa jigo ne na nutsuwa. Shi kuwa jigo yana iyaɗaukar ma'anar wani ice da manoman rani ke amfani da shi wajen aikin lambu don bayar da ruwa ga shuka.
Abubakar Sani ma a waƙarsa mai suna "Zubar Gado" ya kawo jinsarwar abuntarwa a wani baiti kamar haka:

Mata adon gari,
Kun zama sinadari,
Nai muku tambari,
Na yiƘoƙari,
Naɗau alƙawari,

Kun ci sasari,
Ba za ni bar ku ko za a kar ni ,
Ba za na bar ku ba mata.

A nan shi ma Abubakar Sani ya kira mata da ado, wato suna yi wa gari kwalliya kuma su ne sinadari. Sinadari kuwa mahaɗi ne na haɗa abubuwa musamman magunguna ko wani nau'inƘira ta kimiyya da ake son samarwa.

### 5.3.2.6 Salon Kwaikwayo

Salon kwaikwayo salo ne da mawaƙa ke amfani da shi wajen isar da saƙo, da jan hankalin masu saurare ta hanyar kwaikwayon muryar waniɗan wasa (musamman ɗanmaraya Jos[16], da Ibro), ko kwaikwayon muryar Yarbanci, ko Gwari, ko Ibo. Sadi Sidi Sharifai yana daga cikin mawaƙan fim masu kwaikwayon muryar 'yan wasa wajen rera waƙa musamman ma kwaikwayon muryar Rabilu Musa (Ibro). Misali, a waƙar "Baba sai mana mai ros" Sadi ya kwaikwayi muryar Ibro inda yake cewa:

Wayyo! kai kai, na sami jarina da ku jimillar 'ya'yana
Baba sai mana mai ros a sa aɗakin aurena.

Na sami jarina da ku jimillar 'ya'yana
Baba sai mana mai ros a sa aɗakin aurena.

Ee zan batuna zan so ku dakata ku ji zancena,
Baba me za ka faɗa garemu don mu yi amfana,
Zan bayani kan samarinku kan a sa muku rana,
Ko sai mun yi biyayya kan a sanya mana rana?
A'a ba haka ba ni ku tatse su ne fatana.

A nan Sadi ya yi amfani da muryar Ibro ne ya tsara waƙa wadda taƘunshi bayani kan yadda Iyaye ke koya wa 'ya'yansu hanyoyi da hikimomin roƙo, da yaudarar samari don amsar abin hannunsu.

Haka kuma a waƙar Gobinda mai suna "Mai magani tuwo alabo" ya kwaikwayi muryar Yarbawa. Muryar Baban Cinedu aka yi amfani da ita wajen rera waƙar. Ga misali daga baitocin waƙar kamar haka:

Mai magani tuwo alabo Baban Shinedu me wasa,
Mai maganin tuwon alabo Baban Cinedu mai wasa.

Wata rana ina sone,
A Yinugu a dakina,
Ina ci tuwo tuwo alabo,

[16]. Wa}ar Karen Mota da Mata masu bin Bokaye domin neman biyan bu}atun rayuwa kamar na mallakar Miji

Se na ji sallaman bako,
Bako se ka shigo daki,
Bako ka ba mu letaka,
An gayyasheni gun taro,
In je Kano gurin wasa,
Wasa iri ne Ausawa.

Seboda na sani shewa,
Kano geri na Ausawa.

Na doki gariyo nawa,
Na boye shi shikin riga.

Na doki katako nawa,
Na boye shi shikin riga.

Na doki adda nawa,
Na boye shi shikin riga.

Na doki bindiga nawa,
Na boye shi shikin wondo.

Na she in dai na je wasa,
Ausawa in ye magana banza,
In buga shi ya lalashe,
Be sen alin Ausawa,
A she Ausawa bela'i ne,
A she Ausawa mosifa ne.

A waɗannan baitoci an kwaikwayi muryar Yarbawa da sunan cewa muryar Baban Cinedu ce aka kwaikwaya.

### 5.3.2.7 Alamtarwa

Alamtarwa na nufin amfani da inuwar wani suna a matsayin wani suna na wani abu daban. Wato kiran wani abu da wani suna wanda a cikin waƙa ko rubutu keɓantaccen suna ne da ke tsayawa a maƙwafin wancan abu, ko kuma a bayar da wani suna ga wani abu bayan ainihin sunan da mutane suka sani.

Gusau (2010:26) ya bayyana alamtarwa da wata hanya ce wadda ake bayyana wani abu ta ba shi wata alama da ta yi kama da shi ta fuskar siffa ko yanayi koɗabi'a ko hali ko asali ko jaruntaka koƘasaita.

Shi kuwa Auta, (2008:243) ya bayyana wannan dabara da bayyana wata manufa ko wani abu ta hanyar ba shi wata alama, wadda za ta tsaya a maimakonsa.

Mawaƙa da makaɗan baka na wannan zamani suna amfani da salon alamci a cikin waƙoƙinsu. Matsalar da wannan salo ke fuskanta shi ne, ko a can baya bai yawaita ba kamar yadda yanzuɗin ma sai an yi da gaske a cikin waƙoƙi sannan a samu cin karo da irinsa. Saboda haka, da rauninsa ya shigo zamani kuma a haka mawaƙan sukaƘauke shi. Misali
***Annoba*** ya kamata ka gyara halinka,
Bunsuru marar kunya ba ka da hangen baya.
(Mamuda Aƙilu: Waƙar Babbar ƙazanta Zina).

### 5.3.2.8 Kambamawa

Salon kambamawa dabara ce ta cicciɓa wani ko wani abu da kumbura shi ta yadda abinda aka faɗa a game da shi hankali ba zaiɗauka ba.
Ba wani sauyi da aka samu a salon kambamawa a waƙoƙin wannan zamani. Dalili kuwa shi ne, yadda ake yi da aiwatar da su a da yanzu ma haka ake yi.

**Misali**
Ga ki kyakkyawa ce surarki ga kowa ba ta misalta,
Karambani ne nayyi mutum ce ko aljan ‘yan mata,
Ki min uzuri na tare ki a hanya zan yaɗa manufata.
(Umar M. Shareef: Kalaman Baki)

A wani wuri kuwa mawaƙin cewa ya ke:

A kallo ke na ke wa kallo inƘara,
Kalami in kikai batu dole a saurara,
Wajen kwalliya ko dukka mata sun sara,
Muƙami babu wata sai ke....
(Umar M Sharif: Hisabi)

Annoba da aka kawo a nan ana nufin alama ce ta bala’in mazina ci. Kuma shi ne aka kira da annoba, amma ba a faɗi sunansa kai tsaye ba.

### 5.3.3 Sarrafa harshe:

Sarrafa harshe kamar yadda Sarɓi (2007:137) ya ce na nufin "hanya ce ta amfani da harshe a cikin waƙa. Wannan hanya taƘunshi irin yadda marubuci ke zaɓar kalmomi da jimloli da kuma irin yadda yake amfani da su wajen isar da saƙonsa ga jama'a. Abubuwan da mai nazari zai yi la'akari da su a wannan sashe sun haɗa da karin magana, karin harshe,

kalmomin aro,Ƙari ko ragi a cikin kalma,Ƙarangiya da kirari da kuma habaici da sauransu.

### 5.3.3.1 Karin Magana:

Karin magana, magana ce ta hikima a duƙule kuma a matsayin nuni ko ishara da ake iya yin bayani mai tsawo a kanta.

Karin magana fili ne da zamani ya baje kolinsa ya yi ciniki kuma har ya ci riba a cikin kasuwar salo. Tasirin da zamani ya kawo shi ne na yawaitar salon a cikin waƙoƙi sakamakon ilimin boko da mawaƙan ke da shi. Mawaƙa na amfani da salon ta harsuna daban-daban a cikin waƙoƙinsu domin nuna gwanancewa a harshensu. Misali
Ashe faɗa da muminai dai ba riba,
Zakaran Rabbi zai yi cara ba wai ba,
Duk mai son ya hana ya taho mu zuba,
ɗan giwa giwa ne haka ne Garba.
……
Ashe taskira asirin maiɗaki,
Kuma sannan uban dawa shi ne Zaki,
Shehu Maiki ne mai ban mamaki,
Ashe hassda ga Shehu ta zam taki.
(Tudun-Iya: Bawan Allah)

Nura M. Shareef a waƙarsa ta Hisabi ya kawo irin wannan salon a karin magana kamar haka:
Mai nema kar ya fidda ran za ya samu,
Kamar ni na sani akwai lokacinmu,
Idan rabbi yai nufinsa tilas a barmu,
Duk igiyar mahassada mu tsinke.....
(Umar M Sharif: Hisabi)

### 5.3.3.2 Kalmomin Aro

Kalmomin aro su ne kalmomin da marubucin waƙoƙin Hausa yaɗebo su daga cikin wani harshe ya yi amfani da su a cikin Hausa (Sarɓi 2007:148). Wani lokaci akan yi wa irin waɗannan kalmomi kwaskwarima domin su dace da wurin da aka yi amfani da su. Wani lokacin kuwa akan bar su ma yadda suke a harshe na asali.

Zamani riga in ji masu magana. Ko an rantse ba za a yi komo ba, yanzu ba wata waƙa da za aɗauka a rasa birbishi ko nason wani harshe cikinta. Musamman waƙoƙin soyayya da mawaƙa ke rubutawa domin isar da saƙon soyayya ga masoyansu, ko domin aiwatar da sana'ar fim don kuɗi. Waƙoƙin wannan zamani suna cike da salon aron kalmomin

Larabci da Turanci, wani lokaci ma da harshen Turancin ko Larabcin ake yin waƙoƙin. Misali

Falots suna kwamunikeshin wai altanetib a sauka cikin gulbi,
Aɗaura rigunan iska ana ta cillo mu kamar zabi,
A nan na nemi sikwiritis suna tururuwa ta neman hanyar bi,
A ka izoƘeyata kar sheda tsattsaya calak ba ta harbi.
(Aminu Ala: hangen Dala)

Fati Niger a waƙarta ta Duniya ta yi amfani da wannan salon kamar haka;

Kai nazari san da ka zo a ‘yamtinka,
Ran da za ka koma sai kai da aikinka.
(Fati Niger: Duniya)

Har wayau Billi’o shi ma ya kawo irin wannan aro a waƙarsa in da yake cewa:

Ina tunaninki kullum a hanya,
Kin zamo tsada ko in ce kanya,
Kin fi Kuin (ƙueen) kin fi ‘yar Indiya,
In da larabci ke ce jamila,
Inda turanci ke ce biyutiful
(Billi’o: Amina Yafe)

**Auna Fahimta**

1. Jero ire-iren salo guda uku da waƙoƙin ƙarni na ashirin da xaya suke da shi.
2. Mawaƙan ƙarni na ashirin da xaya na sarrafa harshe? Yaya abin yake?
3. Wane salo ne na mutuntarwa a waƙar baka ta Hausa?

**Kammalawa**

Wannan tattauna kan salailan da ake samu a waƙoƙin Hausa ne, amma ba su kaɗai ba ne, akwai wasu da dama da za a gani a cikin wasu ayyukan da ba a ambace su a wannan bagiren ba. Salon kwatantawa da sifanatawa da kambamawa a kawo misalansu a wannan kashi.

## 5.4 Taƙaitawa

- Salailai su ne gishirin kowace fasaha ta baka ko a rubuce. Hanyoyi ne da fasihai ke isar da saƙonsu.

- Salailai irinsu Kwatantawa da Sarrafa Harshe aka tattauna akansu

## 5.5 Jingar Darasi

- Bayyana Ma’anar Salo bisa ra’ayoyin Masana Hausa guda Uku
- Kawo Bayani tare da Misalai kan Salon Kwatantawa
- Kwaikwayo bazar Mawaƙa,tattauna wannan tunani ta la’akari da tattaunawar da aka yi aƘarƙashin wannan kasha

## 5.6 Manazarta

Gusau, S. M. 2003 *Jagoran Nazarin Waƙar Baka*. Benchmark Publishers Limited, Kano, shafi na 18

ɗangambo, A. 2007. *ɗaurayar Gadon Feɗe Waƙa*. Amana Publishers Limited, Zaria, shafi na 218

Yahya, A. B. 2001. *Salo Asirin Waƙa*. Fisbas Media Serɓices, Kaduna, shafi 85

Waƙar Karen Mota da ta Mata masu bin Bokaye domin neman biyan buƙatun rayuwa kamar na mallakar Miji waɗanda Marigayi ɗanmaraya Jos yay a rera.

## 5.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Daga ciin ir-iren salon waƙoƙin ƙarni na ashirin da xaya akwai:
   a) SalonKwatantawa
   b) Salon Jinsintarwa
   c) Salon Kwaikwayo
2. Ƙwarai mawaƙan baka na ƙarni na ashirin na sarrafa harshe a cikin waƙoƙinsu. Sukan sako karin magana ko habaici da sauransu a waƙoƙinsu. Karin Magana salon sarrafa harshe ne da ake kawo wata magana cikin hiima a dunƙule ta yadda a yawancin lokuta sai mutum ya yi tsai ko dogon tunani kafin ya fassara ta. Misali kamar yadda Tudun Iya ya kawo a waƙrsa mai suna *Bawan Allah.* Inda ya ce:

   Ashe faɗa da muminai dai ba riba,
   Zakaran Rabbi zai yi cara ba wai ba,

Duk mai son ya hana ya taho mu zuba,
ɗan giwa giwa ne haka ne Garba.
3.salon *Mutuntarwa* dabara ce da mawaƙan Hausa ke xaukar darajar mutum su ba wa wani abu da ba mutum ba.

# KASHI NA 6 FEƊE WAƘAR JARUMAR MATA TA MAKAƊI HAMISU YUSUF SA'ID (BREAKER) BISA GADON NAZARIN WAƘAR BAKA BAHAUSHIYA

## ABUBUWAN DA KE CIKI

6.1 Gabatarwa a kan Salsalar Waƙar
6.2 Tasirin waƙar ga al'ummar Hausawa
6.3 Saƙo ko Turken Waƙar
  6.3.1 Gundarin Turke
  6.3.2 Muhallan Turke na waƙar:
6.4 Taƙaita Turke Waƙar
6.4 Awon Baka na Wannan Waƙa
6.5 Manazarta
6.6 Manazarta Ta Haɗaka



## 6.1 Gabatarwa a kan Salsalar Waƙa

Wannan waƙa, makaɗi Hamisu Yusuf Sa'id[17] (Breaker) shi ne ya yi ta kuma ya yi wannan waƙa ne kamar yadda ya saba yin waƙoƙinsa na soyayya. Har wa yau kuma Hamisu Breaker makaɗi ne wanda yake amfani da Kiɗan Sitidiyo[18] kuma yakan yi waƙoƙi ne aƘungiya ko kuma a kaɗaita.

A nazarin nan kuma an sami wannan waƙa wadda aka turo mini ita cikin wayata daga mutane daban-daban waɗanda suka haɗa da Malam Kamilu ɗahiru Gwammaja da Kubra Muhammad Abba da Malam Ibrahim Ali KEZ, abokin Abdullahi Buba Gashuwa. Daga bisani ni kuma na saurari waƙar, sannan na juya ta a takarda[19].

[17] Hamisu Yusuf Sa'id wani matashi ne wanda Allah ya hore masa shirya waqar Hausa bisa lokacinsa da yake a cikinsa. Ana yi masa laqabi da Breaker domin ya iya taka rawa gwarwado da zamanin da yake a ciki ko don ya san dabaru daban-daban na shiryawa da aiwatar da waqoqinsa da kuma sadar da su ga jama'a. Bisa dukkan alamu Hamisu Breaker bai yi aure ba illa yana a ga~ar soyayya da mata, musamman matasa ko budurwoyi wato ko marasa aure. Domin haka, ba a bin mamaki ne ba idan ya tsara kuma ya rera wannan waqa ta Jarumar Mata.

[18] Kixan Sitidiyo, kixa ne wanda ake yi a wani xaki da ake kira Sitidiyo wanda aka zuba wa kayan kixa iri-iri kama daga fiyano da ganguna (irin na Turawa) da miksa da makirifon (Amsa-amo) da na'urar sauti (lasifika) da hedifon da maxaukan fiyano da sauransu. Shi wannan xaki na Sitidiyo yana da makaxa masu tafiyar da harkokin kixa a cikinsa kuma ana iya saka masa kowane irin nau'in sauti, tun ma ba na kixa ba (Gusau, 2016: 27-29). Da alama wannan ne ma ya sa aka buxe wannan waqa ta Jarumar Mata da wani amo na kixa mai karsashi da jan hankali.

[19] An kawo juyin matanin wannan waqa a ~angaren rataye na wannan takarda.

Makaɗi Hamisu Breaker ya yi wannan waƙa ta Jarumar Mata ba da jimawa ba aka yi sallaƘarama, Idil Fitri ta wannan shekara 2020 miladiyya (Lahadi 24/5/2020). Kuma ya yi waƙar ne a cikin ganiyar rani ko zafi daidai kuma da lokacin da ake hana mutane fita, ana kulle su a gidajensu saboda Corona ɓirus (Coɓid 19) duk da kuma ga watan Ramalan da azumin da ake yi a cikinsa. Har wa yau kuma waƙar Jarumar Mata tana da yawanɗiya aƙalla guda goma sha biyar (15)[20].

Kamar yadda aka bayyana a baya, sunan yanka na wannan makaɗi shi ne Muhammadu Hamisu, mahaifinsa kuma shi ne Sa'idu, sannan kakansa shi ne Yusufu. Unguwar Hamisu Breaker ita ceɗorayiƘarama a sashen Unguwar Bello. An haifi Hamisu a shekarar 1992. Ya yi makarantar Firamare ta Gwamnati aɗorayiƘarama, ya kuma yi makarantar sakandare ta Gwamnati, Ƙarama da Babba duka aɗorayi Babba a Jihar Kano. Haka kuma shi mutum ne mai riƙe abubuwa, mai kaifin hadda, mai mayar da maganganu kamar yadda ya ji su.

Hamisu Breaker ya fara waƙa ne a sa'ilin da yake a MakarantarƘaramar Sakandare ta Dorayi Babba, a Jihar Kano, kuma har yau yana a kai. Allah yaƘara masa basira daɗaukaka. Duk da yake Hamisu Breaker ya samo tashi da shirya waƙoƙi tun yana a makarantar allo, musamman waɗanda ya yi a tsakanin tsararrakinsa. Sannan bayan da ya zama mawaƙi ko makaɗi ya fara fitar da album nasa na farko a shekarar 2016. Lokacin nan ne ya fitar da album maiɗauke da waƙoƙi aƙalla guda shida, yawancinsu kuma na soyayya ne.



## 6.2 Tasirin Waƙar ga Al'ummar Hausawa

Waƙar jarumar Mata ta yi tashe sosai musamman ma a wajen matasa Hausawa, maza da mata, ma'aurata da marasa aure. Waƙar ta shiga zukatan matasa Hausawa ka'in-da-na'in, musamman a lokacin bikin SallaƘarama ta wannan shekara ta Lahadi 24/5/2020 Miladiyya. Waɗannan matasa sun haddace waƙar, sun kuma yi mamin nata dangane da soyayya daƘauna da son rai daban-daban da suke nunawa.

Ina iya tunawa a tarƙe ko a nazarin waƙar baka akwai abubuwa biyu da za a yi la'akari da su a kowace waƙa da za a yi nazari kuma aƘarfafa wa mutane su saurare ta. Akwai waƙar da za a yi wa nazari wadda ta dace

[20] Haqiqa, waqar Jarumar Mata ta zama ruwan dare game duniya a tsakanin mutane tun ma ba Hausawa ba. Hamisu Breaker ya yi wannan waqa ne da harshen Hausa bisa kari na Kananci. Domin haka,mutane tun ma ba matasa kawai ba sun yi hidimar haddace ta, tare da sassauya ta gwargwadon qauna da bukatar kowannensu. Wata matar aure ce da take nuna son mijinta, wani don son kuxi wani don qaunar dabbobi kamar akuya, wani don bukatar ya samu gida ko mota da sauransu. Ta haka suke maming waqar, suna juya ta, ta amfani da kalmominsu amma bisa amo da yanayin rerawarta da kuma raujinta ba.

da al’adu kyawawa na al’ummar Hausawa kuma ta bi sharuɗɗa da dokokin addinin Musulunci da Hausawa suka yi imani da shi kuma suke ɓiya. Sannan akwai waƙa Ballagazazziyar waƙa wato ita ce wadda ta saɓa wa al’adun al’ummar Hausawa da addininsu. Su kansu kuma zukatan[5] masu saurаron waƙoƙin baka kashi biyu ne. Akwai zukata masu kyau waɗanda suke bin kyawawan dokokin al’adu daƘa’idojin addinin al’ummarsu. Akwai kuma wasu zukatan waɗanda babu ruwansu da dacewar al’adu bisa godabu managarta ko kuma abubuwan da addininsu suka zo musu da su na shiriya.

Haka ne kamar yadda ya gabata, an sami matasa a wasu sassa naƘasar Hausa, maza da mata, waɗanda suka shisshirya ɓideo, suna mamin na wannan waƙa, wasu mata ne waɗanda suke caɓa rawa a gaban mazajensu[21], wasu sun sanya abubuwanƘaunarsu a gabansu .
A ma’ana ta lugga an bayyana Kalmar Zuciya da (i) ‘wata curarriyar tsoka da take cikinƘirjin mutuum ko dabba ko tsuntsu wadda ke aika jini zuwa sauran sassan jiki. (ii) Fusata ko saurin fushi. (iii) Sa zuciya, watau zaton aukuwar abin kirki. (iɓ)Ƙarfin Zuciya, watau jarunta. (ɓ) Zuciyar maraya, watau wata irin saƙa mai fari da baƙi. (ɓi) ya hau dokin zuciya, watau ya fusata. (ɓii) ajiyar zuciya, watau numfasawa. (ɓiii)Ƙawa-zuciya, watau tsananin son abu. (iɗ) wadatar zuci, watau dangana’ (CNHN,Ƙamusun Hausa na Jami’ar Bayero: sh 495). Dangane da ma’anar zuciya ta fannin ilimin addinin Musulunci kuwa ita ce yadda Annabin Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya ambata a cikin Hadisinsa na shida na littafin

Al-Arba’una al-Nawawiyya yana cewa: Tabbas akwai wata tsoka a jikinɗan’adam, idan ta gyaru dukkan jiki ya gyaru, idan kuma ta ɓaci dukkan jiki ya ɓaci. Lallai ita ce: Zuciya.
Buhari da Muslim suka ruwaito shi (ƙaura, Salihu Abubakar, 2017: 38-40).

Suna bin wannan waƙa, suna kuma sassaka nasuƘare-ƙare gare ta da sauran makamantan waɗannan abubuwa. Wannan wani nau’i ne na sheƙe aya, wataƙila ko ba komi sai don su kashe kwarkwatan zaman kulle na gida da aka saka su domin Corona ɓirus (Coɓid 19). Har wa yau kuma wannan ya zama wani nuni ne na abin da zukata suke so kuma ko suke sha’awa. Wannan abun da ya faru ya haddasa ka-ce-na-ce

[21] Bisa al’adu na Hausawa da na addinin Musulunci da suka samu daga bisani, Hausawa dukkansu, maza da mata, an san su da jin kunya da sirranta abubuwa, tun ma ba mata nasu ba. Namiji yake cewa mace yana son ta da aure amman ba ita macen ba. Zai yi wuce mace ta dubi idanun namiji, ta yi ido arba da shi,kuma ta gaya masa tana son sa ko tana qaunar sa ko tana begen sa. Amma a yau, an sami tasire-tasire na zamani da haxuwar Hausawa da wasu baqin al’adu na jinsunan mutane daban-daban tun ma ba Turawa ba, sai wasu Hausawan suka kwaikwayi wasu baqin al’adu har suka qanqame su, suka dinga aiki da su. Yau ga shi an cim ma wani lokaci matan aure na Hausawa wai su ne suke yi wa mazajensu waqa, suna nuna soyayyarsu gare su, ba su bari mazajen su gaya musu waxannan kalamai.

daƘalubale a tsakanin wasu Hausawa, musamman ma Malamai[22] waɗanda suke ganin wannan wata hanya ce ta cin zarafin addinin Musulunci da koin-kula da shi. Waɗannan Malamai suna ganin ba a nuna:

- Tsoron Allah ba, ko
- Kunya ko
- Kishin iyali
- Kuma baƘauna ce ba

Kuma ba mawadda ce ba domin ba a nuna sirri ba, kamar yadda al'adun Hausawa suka amince. Kuma addinin Musulunci ya yarda a dinga sirrintawa a kan aiwatar da abubuwa[23].

Amma idan aka dubi wannan waƙa ta Jarumar Mata[9] da nutsuwa, za a ga haƙiƙa ta dace da a yi nazarinta kuma a iya sauraronta, kuma mai nazari ya yi bugun gaba da ita. Waƙa ce wadda ba ta saɓaƘa'idojin fiɗar waƙa ba, kuma ba ta taɓa al'adun al'ummar Hausawa ko dokokin addininsu na Musulunci ba.

Wasu mutane ne sukaɗauke ta suka jujjuyata ta yadda zukatansu da sha'awace-sha'awacensu suke so. Hasali ma dai waƙar tanaƘarfafa soyayya da mawadda a tsakanin mutane. Ta haka ne Kamilu Dahiru Gwammaja yake tofa albarkacin bakinsa a kan waƙar yake faɗar, 'waƙa ce mai taɓa zuciya, mai sakaya zance kuma taƘunshi wasu maganganu na hikima, ga ta mai adonta harshe (Ganawa da Gwammaja, K.ɗ., ranar Talata 9/6/2020 daƘarfe 9:30 na dare). Domin haka, a fahimta ta, wannan waƙa ta Jarumar Mata ta cancanci nazari. Su kansu wasu Hausawa da sukaɗauki wannan waƙa ta Jarumar Mata, suka aiwatar da ita bisa waɗannan abubuwa kuma a zahiri, sun ari wani shiri ne na ɗEɗ wanda DSTɓ take gudanarwa wanda ake yin tsare-tsare iri-iri kamar tsari na Kardashians wanda ake nunawa, wato wanda ake haska shi a talabijin nasu.

---

[22] Daga cikin waxannan Malamai akwai Malam Mu'azzam Ibrahim na Sashen Musulunci a Jami'ar Bayero, Kano da Malam Dr. Abdullahi Usman Umar Gadon Qaya, Kano da Malam Muhammadu Rabi'u Rijiyar Lema, Kano da Dr. Sanusi Ramadhan da sauransu.

[23] Dubi misali a Alqur'ani, mai girma Suratu al-A'araf, aya ta 33. Sannan kuma akwai maganar Halifa Sayyadina Umar ibn Haxxa~i inda ya yi wa wani mutum wanda yake magana da matasa a qofar gidansa kandarko har ya zungure shi da sanda yana faxin: A fa qofar gida kake'. Shi ko mutumen ya gaya masa, ai yana bisa dokin qofar gidansa ne, kuma yana magana ne da matarsa. Sai Sayyadina Umar ya nuna masa, 'Ashe babu sirri a magana, kowa yana jin ka, yana kuma ganin ka, kuma Allah ya umurci a yi sirri a tsakanin iyali'. [9] Waqar Hamisu Breaker, Kano. Hamisu Breaker makaxi ne wanda Allah ya ba mutane da yawa. Mawaqi ne wanda ya yi shuhura a harkokin sadarwa na zamantakewar jama'a wato Social Media. A Youtube kaxai yana da mabiya fiye da dubu arba'in (40,000) ga kuma Facebook ga Instagram da makamantansu.

A wannan shiri na Kardashians mazauna gidan sukan bayyana sirri na gidan ne ta kowane gefe nasa ba tare da sayawa ba, kuma tufafin da matan gidan suke sanyawa na ainihin tsiraici ne na inna naha, ga yin kalamai sasakai babu wata kunya ko nutsuwa ko kishin kai. Haƙiƙa, waɗannan al'adu sun saɓa wa shiriya ta addinin Musulunci.

Matasa, maza da mata, masu son irin waɗannan al'adu waɗanda za a iya kira munana ne, sun yi gamon katar da wannan waƙa ta Jarumar Mata, makaɗin ya sake ta ko ya fitar da ita. Daga nan sukaɗauke ta suka dinga jujjuya ta, ta yadda suke buƙata, kowane rukuni bisa gwargwadon abin da zuciyarsa takeƘauna, kamar dai yadda aka bayyana a baya.

## 6.3 Saƙo ko Tarken Waƙar

### 6.3.1 Gundarin Turke

Babban saƙon da wannan waƙa takeƘunshe da shi, shi ne nuna tsantsar soyayya irin wadda take wanzuwa tsakanin masoyi da masoyiyarsa, wadda kuma bisa yawanci takan zama mutu ka raba ne. Soyayyar masoyi zuwa ga masoyiyarsa ya ratsa wannan waƙa tun dagaɗanta na farko har kuwa zuwaƘarewarta aɗa na 15. Wannan waƙa tanaɗauke da kalmomi masu fizgar zuciya, kuma masu sakaya zance bisa hikima da adonta masoyiya. Kuma waɗannan kalmomi da aka zaɓo masu bayyana soyayyar masoyi ga masoyiyarsa ne waɗanda suke tafiya tamkar sautin jirginƘasa a yayin da ya darkako hanya.

### 6.3.2 Muhallan Turke na waƙar:

Domin haka a wasu misalai na muhallan turke na waƙar su ne indaɗa na 4 daɗa na 5 suke faɗin:

Jagora: Tilas ganin mu tilas barinmu,
:Ƙaunarki tun da nai nisa,
: Sam ba batun na fasa ko za a ce mun in ba da rai fansa.

Jagora: Tsarin zubin ki daidai ne,
: Ya kama zuciyata ne,
: Ina ji kamar mafarki ne, : Ina son ki so mataki ne.
(Breaker, Waƙar Jarumar Mata,ɗa na 4-5)

Akwai kuma wani misali inda yake cewa aɗa na 6:

Jagora: Ni ban da damuwa in har zan buɗe ‘yan idanuna,
: In kalle ki ga ki dab da ni, : To me za ya damiƘalbina.
(Breaker, Waƙar Jarumar Mata,ɗa na 6)

## 6.4 Taƙaita Turke Waƙar

Saƙonnin da wannan waƙa taƘunsa a gunduwa-gunduwa ta ma’ana sun haɗa da:

ɗa na 1-2: Suna nunaƘarfin son masoyi ga masoyiyarsa domin ko ana ha maza ha mata sai ya sami masoyiyarsa kuma daga nan ba zai sake tanka wa kowa ba. Wato buri ya cika.

ɗa na 3: Masoyi ba zai kula kowa ba sai kawai masoyiyarsa

ɗa na 4-5: Waɗannanɗiya sun shafi muhallin tarke a inda masoyi ya yi ta kwatanta masoyiyarsa. A nan ne kuma masoyi ya nuna ba zai daina nuna soyayyarsa ga masoyiyarsa ba ko da ko zai mutu ne.

ɗa na 6: Shi ma wannanɗa wani muhallin turke ne a inda shi masoyi yake sauwara yana tare da masoyiyarsa. Domin haka babu wani abu da zai dami zuciyarsa ko yaɗauke masa hankali.

ɗa na 7-10: Suna nuna masoyi ya fahimci masoyiyarsa maiƘaunarsa ce, mai cika masa muradinsa, mai kuma ceto nasa bisa kowane hali na rayuwa.

ɗa na 11: Duk daƘarfin son da wannan masoyiya take nunawa, masoyin yana ganin a duniyar nan ba wanda zai iyaɗaukar tunaninsa sai kawai ita masoyiyarsa.

ɗa na 12: Masoyi yana ba da shawara a kan soyayya ga duk wanda ya sarƙu da ita sai ya yi hanƙuri, musamman dangane da sauye-sauyen halayenta.

ɗa na 14:ɗan waƙar yana gargaɗin samari da ‘yanmata a kan su dinga tafiya a sese a soyayya, kuma su yi hakuri da ita, sannan a daina gaugawa.

ɗa na 15: Wannanɗa na 15 shi ne wanda ya rufe wannan waƙar. Da ne da yake yin faɗakarwa a kan masoyi yana taka tasa sa’a, haka kuma shi ma yana da rana ta shanya garinsa.

## 6.5 Manazarta


CNHN, (2006) Ƙamusun Hausa na Jami'ar Bayero. Zaria: Ahmadu Bello Uniɓersity Press Limited.

Gusau, S. M. (2002) SarkinTaushi Salihu Jankiɗi. Kaduna: Baraka Press and Publishers Limited.

Gusau, S. M. (2003) Jagoran Nazarin Waƙar Baka. Kano: Benchmark Publishers Limited.

Gusau, S. M. (2008[a]) Dabarun Nazarin Adabin Hausa. Kano: Benchmark Publishers Limited.

Gusau, S. M. (2008[b]) Waƙoƙin Baka aƘasar Hausa: YanayeYanayensu da Sigoginsu. Kano: Benchmark Publishers Limited.

Gusau, S. M. (2016[a]) Makaɗa da Mawaƙan Hausa na Biyar. Kano: Century Research and Publishing Limited.

Gusau, S. M. (2016[b]) ƙamusun Kayan Kiɗan Hausa. Kano: Century Research and Publishing Limited.

ƙaura, S. A. (2017) Ma'anonin Hadisan Ma'aiki. Zaria: Ahlul-Lahi for Printing and Distribution.


**Rataye: Matanin Waƙar Jarumar Mata Ta Makaɗi Hamisu Breaker**

Makaɗi: Hamisu Yusuf Sa'id (Breaker)

Waƙar: Jarumar Mata

1. Jagora: Ashe da rai nake son ki jaruma ba da zuciyata ba,
- Komai ruwa da iska a kan ki ba za na daina kewa ba, : Idan na samu zarrar samun ki ba za na tanka kowa ba, : Ni ban ga mai harara ba, bare na waiwaya ba.

2. Jagora: In dai a kanki ne za na jure wahalar zuwa garin nisa,
- Da an taɓa ki a jira ni don ko tilas na zo naɗau fansa,
- Jimirin Jiranki nai don ki zo na kalle ki gimbiyar Hausa, : Sirri na rayuwata ke ce kawai da kin kira da na amsa.

3. Jagora: Zuma a baki dadî gare ta kin ba ni taki na lasa, : In dai a kanki ne na yi nisa, : Don ba kiran da zan amsa.

4. Jagora: Tilas ganin mu tilas barinmu,
- Ƙaunarki tun da nai nisa,
- :Sam ba batun na fasa ko za a ce mun in ba da rai fansa.

5. Jagora: Tsarin zubin ki daidai ne, : Ya kama zuciyata ne,
- Ina ji kamar mafarki ne, : Ina son ki so mataki ne.

6. Jagora: Ni ban da damuwa in har zan buɗe ‘yan idanuna,
- In kalle ki ga ki dab da ni, : To me za ya damiƘalbina.

7. Jagora: Yau za na yo amo,
- Tun da na gane kina da tausai na,
- Dan yanzu na zamo ya mafatauci mai biɗar gurin kwana.

8. Jagora: NaƘwallo shela dan sanar da iya maƙiya kalamaina, : Daga zuciya nake kwatanta ina zayyano jawabaina.
9. Jagora: Idan babu ke ina ne zan saka zuciya ta bar yawanƘuna, : Kowa da nasa amma ni ke ce cikar muradaina.

10. Jagora: Yau ga ni a ruwa kusa da kada,
- Zo ki ceciƘarkona,
- Komai da mafuta kar da ki saba da farta ban kwana.

11. Jagora: Ina ji ina gani yadda nake son ki ya fiƘarfina, : Na san a duniya da wanda yake janye duk tunanina.

12. Jagora: Soyayya rayuwa wani sa’in sai ta zama wutarƘuna, : Duk wanda ke cikinta shi ne jurau amma fa a gurina.

13. Jagora: So na faranta rai da ruhi ya sa ka zam kamar Sarki, : Kuma rayuwa da so misali ne yana kama a mafarki.

14. Jagora: Samari mu yi hakuri idan har mun sami so mu sa sauƙi, : ‘Yanmata mui hakuri idan har mun sami so mu sa sauƙi.

15. Jagora: Masoyi yana da rana ne,
- :Masoyi yana da rana ne, Jagora: Masoyi yana da rana ne.

Tamat

Wanda ya juya wannan waƙa:
Farfesa Sa’idu Muhammad Gusau
Laraba 10/6/2020 miladiyya

https://www.youtube.com/watch?v=PsRn4s1Ygj8&list=RDPsRn4s1Ygj8&index=1

## 6.6 Manazarta Ta Haɗaka


Abba, Muhammad. da Zulyadaini, Balarabe, Nazarin Waƙar Baka Ta Hausa**.** Gaskiya Corporation Limited, Zaria, 2000.

Abbas, Umma Ado. 2008. “Waƙoƙi A Fina-finan Hausa”. A Cikin *Algaita Journal of Humanities*. Bayero Uniɓersity, Kano. ɓol. 1 No 5.

Abbas, Umma Ado. “Sassarƙuwar Adabi Cikin Adabi: Nazarin Adon Harshe A Waƙoƙin Fina-finan Hausa”. Kundin Digiri Na Uku, Sashen Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero, Kano, 2008.

Abbas, Haruna. 2009. “Gudummuwar Hukumar Wallafa Littattafai Ta Nijeriya Ta Arewa Wajen Haɓaka Adabin Hausa Daga 1966 – 2006”. Kundin Digiri Na Biyu, Sashen Harsunan Nijeriya, Jami’ar Usmanu ɗanfodiyo, Sakkwato.

Abba Abba Tahir. “Loan Words As A Deɓice For Maintaining Rhyme: A Study of Hausa Modern Music”. A cikin *The FAIS Journal of Humanities*, Jami’ar Bayero,2011 Kano.

Abdulkadir, ɗangambo. Zaɓaɓɓun Waƙoƙin Da Da Na Yanzu**.** Thomas Nelson Nigeria Limited, Lagos, 1976

Adamu, Abdallah Uba. da Wasu. Hausa Home ɓideos: Technology, Economy and Society. Adamu Joji Publishers, Kano, 2004

Ainu, Hamza. “Rubutattun Waƙoƙin Addu’a Na Hausa: Nazarin Jigoginsu Da Salailansu”.Kundin Digiri Na Uku. Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami’ar Usmanu ɗanfodiyo, Sakkwato, 2004.

Alamuna, Nuhu. (2012) “Sauye-Sauye A Tsarin Waƙoƙin Zamani: Nazari A Kan Waƙoƙin Fina-Finan Hausa” Kundin Digiri na Biyu, Jami’ar Usumanu ɗanfodiyo, Sokoto

Ahmed, S. (2019) “Sabon Zubin Waƙoƙin Hausa a ƙarni na 20” Kundin Digiri na Biyu, Jami’ar Usumanu ɗanfodiyo, Sokoto

Bello, Sa'adiyya Omar. Malam Mu'zu Haɗeja Fasihin Mazan Jiya: Nazarin Rayuwarsa Da Waƙoƙinsa. Kundin Digiri Na Uku, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu ɗanfodiyo, Sakkwato, 2001.

Chamo, Ibrahim Yusuf. 2006. Saƙo a Fina-finan Hausa: Nazari kan Jigo da Rabe-Rabensa. Kundin Digiri Na Uku, Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

Chamo, Ibrahim Yusuf. "Sabon Zubi A Rubutattun Waƙoƙin Hausa NaƘarni Na 21". A Cikin *Harshe Journal of African Languages*, Department of African Languages,Ahmadu Bello Uniɓersity, Zaria, 2010.

ɗan'iya, Dahiru. Adon Harshe a CikinƘagaggun Labarai Na Hausa. Kundin Digiri Na Biyu, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, 1997.

ɗangambo, Abdulƙadir. Rabe-Raben Adabin Hausa Da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa. Triumph Publishers, Kano, 1984.

ɗangambo, Abdulƙadir. ɗaurayar Gadon Feɗe Waƙa. Amana Publishers Limited, Zaria, 2007.
ɗangambo, Abdulƙadir. Rabe-raben Adabin Hausa. (Sabon Tsari) Amana Publishers Limited, Zaria, 2007.

ɗangulbi, Adamu Rabi'u. "Siyasa a Nijeriya: Gudummuwar Marubuta Waƙoƙin Siyasa Na Hausa Ga Kafa Dimokuraɗiyya a Jamhuriya Ta Huɗu, Zango Na ɗaya". Kundin Digiri Na Biyu, Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu ɗanfodiyo, Sakkwato, 2003.

Dunfawa, Atiku Ahmad. Jigo a Cikin Fina-finai da Littattafan Zamani. Muƙalar da Aka Gabatar a TaronƘara wa Juna Sanin a Cibiyar Nazarin Hausa, Jami'ar Usmanu ɗanfodiyo, Sakkwato, 2002.

Dunfawa, Atiku Ahmad. Ma'aunin Waƙa**.** Garkuwa Media Serɓices, Sokoto, 2003.
Dunfawa, Atiku Ahmad. "Zambo da Habaici a Cikin Rubutattun Waƙoƙin Addini". A Cikin *ɗunɗaye Journal of Hausa Studies*. ɓol 1 No. 5, 2003.

Dunfawa, Atiku Ahmad. 2011. Dangantakar Waƙoƙin Hausa Da Samari: Rashin Sha'awa ko Rashin Fahimta. A Cikin Himma Journal of Contemporary Hausa Studies, Umaru Musa 'Yar'adua Uniɓersity, Katsina, 2011.

Fatuhu, Muhammad. "Batsa a Waƙoƙin Fina-finan Hausa: ƙalubale ga Masu Wa'azantarwa". Takardar da ta Fito a Cikin Mujallar *Fim.* Agusta, 2005.

Furniss, Graham.Poetry, Prose and Popular Culture in Hausa. Edinburgh, London,1996.

Gandu, Ibrahim Muhammad. Tasirin Fina-finan Indiya a kan Na Hausa. Kundin Digiri Na Biyu, Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu ɗanfodiyo, Sakkwato, 2006.

Gidan Dabino, Ado Ahmad. "Matsaloli da Nasarorin Masu Shirya Fina-finan Hausa Musamman na Kano". A Cikin Adamu, da wasu (Editoci), Gidan Dabino Publishers, Kano, 2004.

Gusau, Sai'du Muhammad. Dabarun Nazarin Adabin Hausa. Fisbas Media Serɓices, Kaduna, 1995.

Gusau, Sa'idu Muhammad. Jagoran Nazarin Waƙar Baka. Benchmark Publishers Limited, Kano, 2003.

Gusau, Sa'idu Muhammad. "Waƙar Baka aƘasar Hausa:Yanaye-yanayenta Da Sigogint"a. Longman Publishers Limited, Ibadan, 2009.

Gusau, Sa'idu Muhammad. Diwanin Waƙoƙin: Zaɓaɓɓun Matanonin Waƙoƙin Baka Na Hausa. Century Research and Publishing Company Limited, Kano, 2009.

Gusau, Sa'idu Muhammad. 2011. Tarihi Da Hanyar Nazarin Waƙar Baka Bahausiya. A Cikin *Waƙoƙin Baka Na Hausa*. Century Research And Publishing Limited, Kano, 2011.

Habibu, Lawal. 2001. Bunƙasar Rubutattun Waƙoƙin Hausa a ƙarni na Ashirin. Kundin Digiri Na ɗaya, Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu ɗanfodiyo, Sakkwato.

Ibrahim, Aminu. 2004. "Salon Jawo Hankali Cikin Rubutattun Waƙoƙin Soyayya na Dr. Abdullahi Bayero Yahya". Kundin Digiri Na ɗaya, Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Danfodiyo, Sakkwato.

Iyantama, Hamisu. "Matsayin Fina-finan Hausa a Musulunci". A Cikin Adamu da wasu (Editoci). Adamu Joji Publishers, Kano, 2004.

Kafin Hausa, Abdullahi Umar . Jiya Da Yau. Uniɓersity Press Limited, Ibadan, 1984.

Koko, B. A. S. 2002. "Tasirin Waƙoƙin Fina-finan Hausa na Zamani a kan Waƙoƙin Addini".

Kundin Digiri Na ɗaya, Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu ɗanfodiyo, Sakkwato.
Koko, Hadiza. Salihu. "Saƙo a Cikin Waƙa". A Cikin *Makarantar* Hausa. Mujalla ga Mai Neman Ilmin Hausa, Fitowa ta 2, 2007.

Magaji, Ahmad. 1982. "Tasirin Adabin Baka a Kan RubutattunƘagaggun Labarai". Kundin Digiri Na Biyu, Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero , Kano.

Mohammad, Nata'Ala. 2002. Mata a Cikin Fina-finan Hausa. Kundin Digiri na Biyu, Jami'ar Bayero, Kano.

Mack, Berbly. Muslim Women Sing: Hausa Popular Song. Indiana Uniɓersity Press, Bloomington, 2004.
Mohammed, Wada Hamza. Tauna Ka Busa. Abokin Hira na 4. Logman, Nigeria, 1983.

Mandawari, Ibrahim."Tarihi da Tasirin Waƙoƙin Fina-finan Hausa". A Cikin *Hausa Home ɓideo: Technology, Economy & Society*. Gidan Dabino Publishers, Kano, 2004.

Mohammed, Lawal. Mutanen Boye: Nazari da Sharhin Mawaƙan Fina-finan Hausa. Kundin Digiri Na ɗaya, Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu ɗanfodiyo, Sakkwato, 2009.

Mu'azu, Adamu. 2005. Tasirin Baƙin Al'adu aƘagaggun Labaran Soyayya Na Hausa. Kundin Digiri Na Uku, Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu ɗanfodiyo, Sakkwato, 2005.

Mungadi, Awwal Muhammad. da Wani 2000. Tarsashin Tatsuniyoyin Hausa a Cikin Wasannin Kwaikwayon Hausa na Bidiyo. Kundin Digiri Na ɗaya, Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu ɗanfodiyo, Sakkwato.

Northern Nigerian Publishing Company. 1970. Waƙoƙin Mu'azu Haɗeja. Zaria, 1970.
Nuhu, Alamuna. 2007. "Jigogin Gargaɗi da Faɗakarwa a Wasu Waƙoƙin Alhaji Aƙilu Aliyu". Kundin Digiri na ɗaya, Sashen Harsunan Nijeriya, Jam'ar Usmanu ɗanfodiyo, Sakkwato.

Omar, Sa'adiyya. Style and Theme in the Poem of Mu'azu Haɗeja. M. A. Dissertation, School of Oriental and African Studies, London,1983.

Sarɓi, Abubakar. *Nazarin* Waƙen Hausa. Samarib Publishers, 2009, Kano.

Sabe, Bihishir Abu. 2011. "Adabin Kasuwar Kano: Nazari Game daƘagaggun Labaran Hausa (1084-2008)". Kundin Digiri na Biyu, Jami'ar Usmanu ɗanfodiyo, Sakkwato, 2011.

Talata Mafara, Muhammad Isah. 2002. "Yawaitar Wasannin kaset-kaset na Hausa da Littattafan

Zamani (1980-2002) ƙalubale ga Al'ummar Musulmi". Muƙallar da Aka Gabatar a TaronƘara wa

Juna Sani na Cibiyar Nazarin Harshen Hausa, Jami'ar Usmanu ɗanfodiyo, Sakkwato, 2002.

Usman, Bello Bala. 2002. Zubin Amsa Amon Waƙoƙin Hausa. *Majolls Maiduguri Joural of Linguistics and Literary Studies*, Uniɓersity of Maiduguri, Maiduguri, 2002.

Yahya, Abdullahi Bayero."Gudummuwar Mawaƙa a Fagen Wayar da kan Jama'a". Muƙalar da Aka Gabatar a Taron ƙungiyar Marubuta da Manazarta Waƙoƙin Hausa naƘasa, Argungu, 1987.

Yahya, A. B. 1997. *Jigon Nazarin Waƙa*. Fisbas Media Serɓices, Kaduna.

Yahya, Abdullahi Bayero. Salo Asirin Waƙa. Fisbas Media Serɓices, Kaduna, 2001.

Yahya, Abdullahi, Bayero."Waƙa: Ma'ana da ɗabi'a da Ginshiƙanta". Muƙalar da Aka Gabatar a Taron ƙara wa Juna Sani, Cibiyar Nazarin Hausa, Jami'ar Usmanu ɗanfodiyo, Sakkwato, 2010.

Yakasai, Salisu Ahmad. 2002. Waƙoƙin Cikin Wasannin Kaset-kaset na Hausa da Littattafan Zamani: Gyara ko ɓarna? Muƙalar da Aka Gabatar a TaronƘara wa Juna Sanin a Cibiyar Nazarin Hausa, Jami'ar Usmanu ɗanfodiyo, Sakkwato daga 8-9 ga watan Yuli, 2002.

'Yankara, Musa. (2017) "Wane Irin Sauyi ko Tasiri Zamani ya Kawo a cikin Salon Waƙoƙin Hausa na Baka da Rubutttu? Aikin Jinga a Matakin Digiri na Biyu, Sashen koyar da Haursunan Nijeriya, Jami'ar Usumanu ɗanfodiyo, Sokoto